# TAUHIDI

WALLAFAR SHEIKH:
DR. SALEH BN FAUZAN AL-FAUZAN
a cikin Harshen Hausa



FASSARA: SURAJ BALA UMAR | BITA: ISMA' IL GARBA ALI

# كــتاب

# الـــتوحـــيد

تأليف: فضيلة الشيح

الدكتور/ صالح بن فوزان الفوزان

ترجمة: سراج بلا عمر

مراجعة: إسماعيل غرب علي

# TAUHIDI

**WALLAFAR SHEIKH**

**DR. SALEH BN FAUZAN AL-FAUZAN**

**Cikin Harshen Hausa**

**FASSARA: SURAJ BALA UMAR**

**BITA: ISMA'IL GARBA ALI**

بسم الله الرحمن الرحيم

**DA SUNAN ALLAH MAI RAHAMA MAI JINƙAI**

**GABATARWA**

Godiya ta tabbata ga Allah ubangijin talikai, tsira da aminci su tabbata ga annabinSa mai gaskiya mai amana annabimmu Muhammad da alayensa da sahabbansa baki daya. bayan haka:

Wannan littafi ne na ilimin Tauhidi, na kula da takaitawa a cikinsa tare da saukin bayani, na tsakuro shi daga manazarta mai tarin yawa daga cikin litattafan jagororimmu fitattu- musamman ma Sheikul Islam ibn Taimiyah, da litattafan bijimin malami Ibnul Kayyim, da litattafan Sheikhul Islam Muhammad bn Abdulwahhab da almajiransa cikin jagororin wannan da'awa mai albarka. Yana daga cikin abin da babu kokwanto a kansa cewa ilimin akida ta Musulunci shi ne ilimi na tushe wanda ya cancanta a kula da shi wajen koyo da koyarwa da aiki da abin da ya kunsa, domin ayyuka su kasance karbabbu a wajen Allah, masu amfani ga masu aiki, musamman muna cikin wani zamani da kiraye-kiraye na bata suka yi yawa; kiraye-kirayen musanta samuwar Allah, kiraye-kirayen sufanci da rahbana, kiraye-kirayen 'yan bautar kabari da gumaka, kiraye-kirayen bidi'o'I da suka sabawa tsarin annabi, dukkansu kiraye-kiraye ne masu hadari matukar musulmi bai yi wukar gindi da Akida ingantacciya ba wadda ta ginu a kan Alkur'ani da Sunna da abin da magabatan al'umma na kwarai suke a kai, to, lallai yana dab da fuzguwa zuwa wadannan kiraye-kirayen na bata, wannan yana daga cikin abin da ya ke bukatar kulawa cikakkiya wajen koyar da Akida ingantacciya ga 'ya'yan musulmai daga manazartarsu ta asali.

Tsaira da amincin Allah su kara tabbata ga Annabimmu Muhammad da alayensa da sahabbansa.

[Mawallafin]

# BABI NA FARKO

## KARKACEWA (BATA) A RAYUWAR MUTANE DA DAN TARIHI GAME DA KAFURCI DA MUSUNT SAMUWAR ALLAH DA SHIRKA DA KUMA MUNAFUNCI

*Ya kunshi fasalai masu zuwa:*

**Fasali na farko:** Karkacewa (Bata) a rayuwar mutane.

**Fasali na biyu:** Shirka – ma'anarta da nau'o'inta.

**Fasali na uku:** Kafurci – ma'anarsa da nau'o'insa.

**Fasali na hudu:** Munafunci - ma'anarsa da nau'o'insa.

**Fasali na biyar:** Bayanin hakikanin wadannan abubuwan:

Jahiliyya – Fasikanci – Bata – Ridda – rabe-rabensu da hukunce-hukuncensu.

## FASALI NA FARKO: KARKACEWA (ƁATA) A RAYUWAR MUTANE

Allah Ya halicci halitta domin bauta maSa, kuma Ya tsara su bisa tsarin da zai taimaka musu a kan haka ta bangaren arziki; Allah SWT Yana cewa: ***(Ban halicci aljani da mtane ba sai don su bauta min. ba na menan wani arzuki daga wajensu, kuma ba na neman su ciyar da ni. Lallai Allah Shi ne mai yawan azirtawa Ma'abocin karfi mai kwari)*** **[al-Zariyat 56 – 58].**

Zuciya ita da kanta idan aka barta bisa tsarin halittarta za ta tabbatar cewa Allah Shi ne abin bauta, da kauna a gareshi ba tare da hada shi da wani abu ba, sai dai abin da ya ke bata ta kuma ya ke karkatar da ita daga yin haka shi ne abin da shaidanun mutane da aljanu su ke kawata mata, sashinsu yana yi wa sashi wahayin zakin baki cikin yaudara. Tauhidi dai an dasa shi a cikin halitta, shirka kuwa fadowa ta ke, kutse take a kan ainihin tsarin halitta; Allah SWT Yana cewa: ***[Ka tsayar da fuskarka a kan addini mikakke, [hakan] tsarin halittar Allah ne da Ya halicci mutane a kai, babu sauyi a halittar Allah )*** **[Al-Rum: 30].**

Manzon - Allah tsira da amincin Allah su tabbata a gareshi - ya ce: ***"Kowane abin haihuwa ana haifarsa a tsarin halitta [na imani da Allah], iyayensa su ne su ke yahudantar da shi, ko su nasarantar da shi, ko su maguzantar da shi"***[1], asalin al'amari a cikin 'Yan-Adam shi ne Tauhidi.

Addin shi ne: Musulunci tun daga zamanin Annabi Adam - amincin Allah a gareshi - da wadanda suka biyo bayansa cikin zuriyarsa cikin lokatai masu tsawo – Allah SWT ya ce: ***[ Mutane sun kasance al'umma guda daya, sai Allah Ya aiko Annabawa suna masu albishir da gargadi)*** **[al-Bakara: 213].**

Farkon shirka da ta faru da karkacewa a akida ta faru ne a mutanen Annabi Nuhu.

1 - Ya zo a Sahihaini daga hadisin Abu Huraira.

[Annabi Nuhu] amincin Allah ya tabbata a gareshi ya kasance farkon manzo ***(Hakika mun yi wahayi zuwa gareka da zuwa Nuhu da annabawa bayansa)*** **[Al-nisa: 163].**

Ibn Abbas ya ce: tsakanin [annabi] Adam da [annabi] Nuhu akwai karni goma dukkanninsu a kan Musulunci su ke –Ibnul Kayyim ya ce[1]- wannan maganar tabbas ita ce daidai, domin kira'ar Ubayyu bn Ka'ab yana nufin a ayar [Surar] Bakara; ***"sai suka saba, sai allah Ya aiko musu da annabawa".***

Akwai abin da yake kara tabbatar da wannan Kira'ar shi ne fadinSa SWT: ***(Mutane ba su kasance ba face al'umma guda daya sai suka saba)*** **[Yunus: 19].**

[Ibnul Kayyim] Allah Ya yi masa rahama yana nufin aiko da Annabawa sababinsa shi ne sabawa abin da aka kasance a kansa na addini ingantacce – kamar yadda larabawa sun kasance bayan haka a kan addinin [Annabi] Ibrahim - amincin Allah a gareshi -, har sai da Amru dan Luhay Alkhuza'iy ya zo sai ya sauya addinin [Annabi] Ibrahim, ya kawo gumaka zuwa kasar Larabawa da kasar Hijaz gaba daya, sai aka rika bauta musu ba Allah ba, shirka ta yadu a wadannan garuruwa masu tsarki da makotansu- har dai zuwa lokacin da Allah Ya aiko AnnabinSa Muhammad cikamakin Annabawa SAW, sai ya kira mutane zuwa Tauhidi da bin addinin [Annabi] Ibrahim, ya yi gwagwarmaya iya gwagwarmaya a kan [ci gaban] Addinin Allah, har sai da Akida ta Tauhidi da Addinin [annabi] Ibrahim suka dawo, aka karya gumakan, Allah Ya cika addini da shi, ya cika ni'ima a kan talikai. A bisa tsarinsa ne karni-karni na farko wannan al'umma suka rayu.

1 -Igathatul Lahfan (2/102).

Har izuwa lokacin da jahilci ya yadu a karni-karni na baya, aka samu kutsen wasu abubuwa daga wasu addinai da ban, sai shirka ta dawo cikin [mutane] da yawa daga cikin wannan al'umma a dalilin masu kira zuwa bata, a dalilin ***(yin gine-gine a kan Kkaburbura, suna masu nuna girmama waliyyai da salihai, da da'awar kaunarsu, har ta kai suna gina dakuna a kan kabarin, sai aka mayar da su gumaka ana bauta musu ba Allah ba da nau'ikan abubuwan neman kusanci kamar addu'a da neman agaji da yin yanka da bakance a wurarensu. Sai suke kiran shirka da tawassali da salihai, da kuma bayyana soyayyarsu, ba bauta ba ce a yadda su ke rayawa. Sun manta cewa wannan ce maganar mushirikan farko inda su ke cewa: ﴾Ba don komai muke bauta musu ba sai don su kusatamu zuwa ga Allah﴿*** **[Al-Zumar: 3].**

Duk da wannan shirka da ta faru a cikin mutane a da da yanzu da yawansu sun yi imani da Tauhidin Rububiyya, kawai dai suna yin shirka ne a ibada, kamar yadda [Allah] S.W.T Ya ce***: (Da yawansu ba sa imani da Allah face suna yin shirka﴿*** **[ Yusuf:106 ].**

Babu wadanda suka yi musun samuwar Ubangiji sai 'yan tsiraru kadan daga cikin mutane: Kamar Fir'auna, da masu kore Allah 'Yan komai zamani ne, da 'Yan gurguzu a wannan zamanin- kuma musantawar ta su kawai ta girman kai ce, in ba haka ba ai suna da tsananin bukatar tabbatar da samuwarSa a zukatansu da can cikin ransu- kamar yadda Allah SWT Ya ce: ***(Sun musanta don zalunci da girman kai amma zukatansu sun tabbatar﴿*** **[Al-naml:14].**

Hankulansu sun tabbatar musu da cewa duk wani abin halitta dole yana da mahalicci, duk wani samamme dole yana da wanda ya samar da shi, kuma tsarin wannan duniyar mai saiti da tsari dole akwai Mai tsarawa Gwani Mai lissafawa Masani, wanda duk ya musanta, to, ko dai ba shi da hankali, ko mai girman kai da ya yi watsi da hankalinsa, ya wawantar da kansa, irin wannan kam ba a izina da shi.

## FASALI NA BIYU: SHIRKA: MA'ANARTA DA NAU'O'INTA

### A. MA'ANARTA:

Shirka ita ce sanya abokin tarayya ga Allah SWT a RububiyyarSa ko IlahiyyarSa. Yawanci yin shirka a Uluhiyya ake samu ta hanyar [mutum] ya roki Allah tare da waninSa, ko ya sarrafa masa wani abu na nau'o'in ibada: kamar yanka da bakance da tsoro da fata da soyayya. Shirka ita ce mafi girman zunubi, saboda wasu al'amura, kamar haka:

1- Saboda kwatanta Mahalicci da abin halitta ne a kebance-kebance Ilahiyya- duk wanda ya hada wani tare da Allah, to, ya kwatantaShi da shi, wannan shi ne mafi girman zalunci, Allha SWT Ya ce: ***(Lallai shirka zalunci ne babba)*** **[Lukman: 13].** Zalunci shi ne ajiye abu ba a wajensa ba, duk wanda ya bautawa wani ba Allah ba, to, ya ajiye ibada ba a wajenta ba, ya sarrafata ba ga wanda ya cancanceta ba, wannan shi ne mafi girman zalunci.

2- Lallai Allah Ya ba da labari cewa ba zai gafartawa wanda bai tuba daga yinta ba – Allah SWT Ya ce: ***(Hakika Allah ba Ya gafartawa a yi shirka da shi, Yana gafarta abin bai kai ta ba ga wanda Ya so)*** **[al-Nisa': 48].**

3- Allah Ya ba da labari cewa Ya haramta aljanna ga mai yin shirka, kuma zai dauwama, shi dawwamamme ne a cikin wutar Jahannama – Allah SWT Ya ce: ***(Lallai yadda lamarin da sha'anin ya ke duk wanda ya yi shirka da Allah; to, hakika Allah Ya haramta masa aljanna, kuma makomarsa wuta, azzalumai ba su da wani mai taimaka musu)*** **[Al-ma'idah': 72].**

4- Lallai shirka tana rushe dukkan ayyuka- Allah SWT ya ce: ***(Da sun yi shirka da abin da suke aikatawa ya rushe)*** **[al-An'am: 88].** Allah SWT Ya ce:

***(Hakika an yi maka wahayi, da wadanda aka yi kafinka cewa lallai idan ka yi shirka ayyukanka za su rushe, kuma lallai za ka kasance cikin asararru)*** **[al-Zumar: 65].**

5- Lallai mushriki jininsa da dukiyarsa halal ce – Allah SWT Ya ce: ***(Ku kashe mushirikai a duk inda ku ka samesu, ku kamasu, ku tsaresu, ku yi zaune a duk madakatarsu)*** **[al-Tauba: 5].** Annabi SAW ya ce: ***"An umarceni in yaki mutane har sai sun ce: Babu abin bautawa da gaskiya sai Allah, idan suka fada, to, sun tsare jinanansu daga gareni da dukiyarsu sai in da hakki"***[1].

6- Lallai shirka ita ce mafi girman laifuka – Manzon Allah SAW ya ce: ***"Shin ba na gaya muku mafi girman manyan laifuka ba? Sai muka ce: eh ya ma'aikin Allah, sai ya ce: Yin shirka da Allah, da sabawa iyaye"*** hadith[2] - Babban malami Ibnul Kayyim ya ce[3]: Allah S.W.T Ya ba da labari cewa manufar halitta da al'amari shi ne a sanShi da sunayenSa da siffofinSa, a bauta maSa kada a yi shirka da Shi, mutane su tsaya su yi adalci, adalci wanda da shi ne sammai da kasa suka tsaya, kamar yadda Allah S.W.T ya ce: ***(Hakika mun aiko da manzannimmu da bayyanannun [hujjoji], mun saukar da littafi tare da su da ma'auni domin mutane su yi adalci)*** **[Al-hadid: 25].**

Allah S.W.T Ya ba da labari cewa Ya aiko da manzanninSa, Ya saukar da litattafanSa, domin mutane su yi KISDU wanda shi ne adalci, daga cikin mafi girman adalci akwai Tauhidi, shi ne ma jagoran adalci, kuma kashin bayansa, kuma shirka zalunci ce, kamar yadda Allah SWT Ya ce: ***(Lallai shirka zalunci ce babba)*** **[Lukman: 13].**

Shirka ita ce mafi girman zalunci, Tauhidi shi ne mafi adalcin adalci, duk abin da ya zama mafi kore wannan manufar, to, shi ne mafi girman manyan laifuka – har dai ya ce: Yayin da shirka ta kasance kai-tsaye tana karo da wannan manufar shi ya sa ta zamo mafi girman manyan laifuka gaba daya, Allah Ya haramta aljanna a kan dukkan mushiriki, kuma Ya halatta jininsa da dukiyarsa da iyalansa ga

---

1 - Bukhari da Muslim ne suka ruwaito shi.
2 - Bukhari da Muslim ne suka ruwaito shi.
3 - Al-Jawabul kafi shafi na 109.

ma’abota Tauhidi, su mai da su bayinsu yayinda suka ki yin ibadarSa, kuma Allah S.W.T Ya ki karbar wani aiki daga mushiriki, ko ya ba shi damar ceto, ko Ya amsa masa roko a lahira, ko Ya amsa masa wani fata, domin mushiriki ya fi dukkan jahilai jahiltar Allah, ta yadda ya sanya masa abokin tarayya daga cikin ababan halittarSa, wannan shi ne karshen jahilci (wauta) –kamar yadda kuma ya ke shi ne mafi karshen zalunci- duk da cewa fa a aikace mushiriki bai zalunci Ubangijinsa ba, sai dai kansa ya zalunta- [zancen] ya tuke.

7- Shirka tawaya ce aibu ce Ubangiji S.W.T Ya tsarkake kanSa daga ita, wanda ya yi shirka da Allah, to, ya tabbatar wa Allah abin da Ya tsarkake kanSa daga shi, wannan shi ne karshen fito-na-fito da Allah S.W.T, kuma shi ne makurar taurin kai da ja-in-ja da Allah.

**B. NAU’O’IN SHIRKA: SHIRKA NAU’I BIYU CE:**

**<u>NAU’I NA FARKO:</u>** Shirka mafi girma wadda ta ke fitarwa daga addini, mai yinta ya ke dauwama a wuta idan ya mutu bai tuba ba, Ita ce sarrafa wani abu na nau’o’in ibada ga wanin Allah- kamar Addu’ar wanin Allah, da neman kusanci da yanka da bakance ga wanin Allah kamar

Kaburbura da aljanu da shaidanu. Da tsoron matattu ko aljanu ko shaidanu cewa za su cutar da shi ko za su sanya masa rashin lafiya- da kuma fatan samu daga wajen wanin Allah cikin abin da babu mai yin sai Allah kamar biyan bukatu, yaye damuwoyi irin abubuwan da ake yi yanzu a gindin gine-ginen da aka yi a kan kaburburan waliyyai da salihai, Allha SWT Ya ce: ***(Suna bautawa abin da ba zai amfanesu ba , kuma ba zai cutar da su ba koma bayan Allah, suna cewa wadannan ne masu cetommu a wajen Allah)*** **[Yunus: 18].**

**<u>NAU’I NA BIYU:</u>** Shirka karama wadda ba ta fitarwa daga Addini, sai dai tana tauye Tauhidi kuma hanya ce ta fadawa shirka babba- ita kuma kashi biyu ce:

**KASHI NA FARKO:** Shirka ta zahiri: ita ce lafazai ayyuka, Lafazan kamar rantsuwa da wanin Allah- Manzon Allah S.A.W Ya ce: ***“Wanda ya rantse da wanin Allah ya kafurta kuma ya yi shirka”[1]- da fadinSa: “Abin da***

1 - Tirmiziy ne ya ruwaito shi ya hassana shi, Alhakim ya ingantashi.

***Allah Ya so ka so" Manzon Allah SAW ya ce: Yayin da wani mutum ya ce: Abin da Allah Ya so ka so, sai ya ce: " Shin ka mai da ni kishiyar Allah? Ka ce: Abin da Allah Ya so shi kadai"***[1]. Da fadar cewa: Ba don Allah da wane ba- daidai shi ne a ce: Abin da Allah Ya so sannan wane, Ba don Allah sannan wane ba- saboda ita "sannan" tana nuna jerantawa ne tare da jinkiri- tana sanya ganin damar bawa tana biye da ganin damar Allah- kamar yadda Allah S.W.T Ya ce: ***(Babu abin da za ku so [da zai faru ko nya ki faruwa] sai in Allah Ya so ubangijin talikai )*** **[Al-takwir: 29].**

Amma shi "da" yana nuna hadawa ne kawai da kuma tarayya, baya nuna jerantawa ko Ko biyo baya, irinsa ne fadin: Ba ni da kowa sai Allah da kai, Wannan daga albarkar Allah ne da albarkarka.

Amma ayyuka: Kamar rataya zobe da guru domin maganin bala'i ko kawar da shi, kamar dai rataya layoyi domin tsoron kambun baka da sauransu, idan ya kudirce cewa wadannan dalilai ne na daukewar bala'i ko kawar da shi, to, wannan shirka ce karama, saboda Allah bai sanya wadannan su zama dalilai ba. Amma idan ya kudirce cewa suna kawarwa ko dauke bala'i su da kansu, to, wannan shirka ce babba, domin ya ratayu ga wanin Allah.

**KASHI NA BIYU:** Yana daga cikin shirka karama: Shirka boyayya, ita ce shirka a manufofi da niyyoyi – kamar riya da jiyarwa- kamar ya yi wani aiki daga wanda ake neman kusancin Allah da shi, shi kuma ya rika neman yabon mutane- kamar ya kyautata sallarsa, ko ya yi sadaka domin a yabeshi a zugashi, ko ya rika furta zikiri yana kyautata muryarsa da tilawa don ya jiyar da mutane, sai su zugashi su yabe shi. Ita kuma riya idan ta cakuda da aiki bata shi take yi, Allah SWT Ya ce: ***(Wanda yake fatan haduwa da ubangijinsa [lami-lafiya] sai ya yi aiki nagari kuma kada ya hada kowa a bautar ubangijinsa)*** **[al-Kahf: 110].**

Annabi S.A.W ya ce***: "Mafi tsoron abin da na ke jiye muku tsoro shi ne karamar shirka, sai suka ce: ya ma'aikin Allah! Mecece shirka karama? sai ya ce: Riya***[2]***. Yana daga ciki yin aiki don kwadayin abin duniya- kamar wanda zai yi hajji ko ya yi kiran sallah ko ya yi wa mutane***

---

1 - Al-Nasa'i ne ya ruwaito shi.

2 - Ahmad ne ya ruwaito shi da Dabarani da Bagawy a Sharhus sunnah.

***limanci sabo da kudi – ko ya koyi ilimin shari'a {addini], ko ya yi jihadi sabo da kudi. Annabi SAW ya ce: "Bawan dinare ya yi asara, bawan dirhami ya yi asara, bawan riga ya yi asara, bawan shimfida ya yi asara, in an ba shi, ya yarda in ba a ba shi ba ya yi fushi"***[1]. Babban Malami Ibnul Kayyim – Allah Ya yi masa rahama- ya ce: "Amma shirka a cikin manufofi da niyyoyi, wannan kogi ne da ba shi da gaba, kadan ne mutanen da za su kubuta daga shi, wanda ya nufi wanin Allah da aikinsa, ya yi niyyar wani abu ba neman kusancinSa ba, ba neman sakamako daga wajenSa ba, to, ya yi shirka a niyyarsa da manufarsa – Ikhlasi shi ne [mutum] ya tsarkake zuciya ya yi don Allah a ayyukansa da maganganunsa da manufarsa da niyyarsa, wannan ita ce hanifiyya [mikakken addini] na [Annabi] Ibrahim wadda Allah Ya umarci bayinSa gaba daya da ita, kuma ba zai karbi wani abin ba ita ba daga kowaye, ita ce hakikanin Musulunci, kamar yadda Allah SWT Ya ce: ***(Wanda ya ke neman wani addini ba Musulunci ba, to, Allah ba zai karba daga gareshi ba, kuma a ranar lahira yana cikin asararru)*** **[al-Imran: 85].** Ita ce addinin [Annabi] Ibrahim - amincin Allah ya tabbata a gareshi wadda duk wanda ya kyamaceta , to, yana cikin wawaye[2].

**Daga abin da ya gabata za mu ga cewa akwai banbance-banbance tsakanin shirka babba da shirka karama, su ne:**

1- Shirka babba tana fitarwa daga addini, shirka karama bata fitarwa daga addini.
2- Shirka babba tana dawwamar da mai yinta a wuta, shirka karama ba ta dawwamar da mai yinta a cikinta ko da ya shigeta.
3- Shirka babba tana bata dukkan ayyuka- shirka karama ba ta bata dukkan ayyuka, sai dai ita riya da yin aiki don duniya suna bata aikin da suka cakuda da shi ne.
4- Shirka babba tana halatta jini da dukiya – shirka karama ba ta halattasu.

***

1 - Bukhari ne ya ruwaito shi.
2 - Al-Jawabul kafi shafi na 115.

**FASALI NA UKU: KAFURCI: MA'ANARSA DA NAU'O'INSA**

**A. MA'ANARSA:**

Kafurci a harshen larabci shi ne rufewa da lullubewa. Kafurci a shari'ance: Kishiyar Imani ne, hakika kafurci shi ne rashin imani da Allah da manzanninSa- duk daya ne an karyata ko ba a karyata ba, kokonto kawai ko tantama ko bijirewa ko hassada ko girman kai ko bin wani bangare na son rai da ya hana bin manzancin, duk da cewa mai karyatawa kafircinsa ya fi girma, haka nan mai musantawa da karyatawa don hassada tare samun tabbacin gaskiyar manzannin[1].

**B. NAU'O'INSA: Kafurci yana da nau'i biyu:**

***Nau'i na farko:*** Kafurci babba yana fitarwa daga addini, shi kuma kashi biyar ne:

***Kashi na farko:*** Kafurcin karyatawa – dalili fadarSa S.W.T: ***(Wa ya kaishi zalunci; wanda ya kirkiri karya ya danganata ga Allah, ko kuma ya karyata gaskiya yayin da tazo masa, shin a Jahannama babu makomar kafirai)*** **[Al-ankabut: 68].**

***Kashi na biyu:*** Kafurcin kin [amsar gaskiya] da girman kai tare da gasgatawa; dalili fadarSa SWT: ***(Ambaci lokacin da muka ce da mala'iku ku yi sujjada ga [Annabi] Adam sai su ka yi sujjada ban da Iblis, ya ki , ya yi girman kai, ya kasance daga cikin kafirai)*** **[Al-Bakara: 34].**

***Kashi na uku:*** Kafurcin kokonto –shi ne kafurcin zato- dalilin fadarSa S.W.T: ***(Sai ya shiga gonarsa alhalin yana mai zaluntar kansa, sai ya ce: Ban taba zaton wannan [gonar] za ta lalace ba har abada, kuma ba na zaton alkiyama za ta tsaya, kuma in koma wajen Ubangijina ma zan samu makomar da ta fi ta. Sai dan uwansa ya ce da shi yana mai tattatunawa da shi yanzu kenan ka kafircewa wanda Ya halicceka daga turbaya sannan daga maniyyi, sannan ya daidaitaka mutum [cikakke]. Sai dai ni ubangijina shi ne Allah, kuma ba zan hada Ubangijina da kowa ba )*** **[Al-kahf: 35 - 38].**

---

1 - Majmu'u fatawa na Sheikul Islam Ibn Taimiya (12/335).

**Kashi na hudu:** Kafurcin bijirewa – dalilin fadarSa SWT: ***(Kafirai masu bijirewa ne ga abin da aka yi musu wa'azi a kansa)*** **[Al-ahkaf: 3].**

***Kashi na biyar:*** Kafurcin Munafunci - dalilin fadarSa S.W.T: ***(Hakan ne saboda sun yi imani sannan suka kafurce, sai aka yunke zukatansu, ba za su fahimta ba )*** **[Al-Munafikun: 3].**

**NAU'I NA BIYU: KAFURCI KARAMI:** kafurci ne karami ba ya fitarwa daga Addini, shi ne kafuci a aiki, shi ne zunubai wadanda ambatonsu da kafurci ya zo a Alkur'ani da saunnah, ba sa kai wa matakin kafurci babba – kamar kafurcewa ni'imar da aka ambata a fadinSa S.W.T: ***(Allah Ya buga misalin wata alkarya da ta kasance cikin aminci da kwanciyar hankali arzikinta yana zuwar mata cikin yalwa ta ko'ina sai ta kafircewa ni'imomin Allah)*** **[Al-Nahl: 112].**

Haka nan misalin kashe mumini da aka ambata cikin fadin manzon Allah S.A.W: ***"Zagin musulmi fasikanci ne, yakarsa kuma kafirci ne"[1]. Da kuma cikin fadinsa SAW: "Kar ku zama kafirai bayana, sashinku yana dukan wuyan sashi"***[2].

Da misalin rantsuwa da wanin Allah [Manzon Allah] S.A.W ya ce: ***"Wanda ya rantse da wanin Allah, to, ya kafurta, ko ya yi shirka"[3]. Allah Ya sanya mai aikata babban laifi a matsayin mumini,*** *Allah S.W.T Ya ce:* ***(Yã kũ waɗanda suka yi ĩmãni! An wajabta, a kanku, yin ƙisãsi a cikin kasassu)*** **[Al-Bakara: 178].** Bai fitar da wanda ya yi kisan daga cikin muminai ba, Ya sanya shi a matsayin Dan uwa ga majibincin ƙisãsi, sai ya ce: ***(to, wanda aka yi rangwamen wani abu gare shi daga ɗan'uwansa to a bi da alhẽri da biya zuwa gare, shi da kyautatãwa)*** **[Al-Baqara: 178].** Abin nufi ba tare da kokonto ba shi ne 'yan uwantaka ta addini. Allah S.W.T Ya ce: ***(Kuma idan jama'a biyu ta mũminai suka yi yãki, to, kuyi sulhu, a tsakãninsu)*** **[Al-Hujurat: 9]** har izuwa fadinSa S.W.T: ***(Mũminai 'yan'uwan jũna kawai ne, sabõda haka ku yi sulhu a tsakãnin***

1 -Bukhari da Muslim ne suka ruwaito shi.
2 - Bukhari da Muslim ne suka ruwaito shi.
3 - Tirmiziy ne ya ruwaitoshi Hakim ya inganta shi.

***'yan'uwanku biyu)*** **[Al-Hujurat: 10]** Anan ya tike daga sharhin [Littafin] Dahawiyya[1] a takaice.

**A dunkule banbance-banbance tsakanin kafurci babba da kafurci karami:**

1- Lallai kafurci babba yana fitarwa daga addini, kuma yana rusa ayyuka, Kafurci karami baya fitarwa daga Addini, kuma ba ya rusa ayyuka, sai dai yana tauyesu gwargwado, yana jefa mai yinsa cikin narko.
2- Lallai kafurci babba yana dawwamar da mai yinsa a wuta, kafurci karami kuwa idan mai yinsa ya shiga wuta ba zai dawwama ba a cikinta, kuma Allah Ya kan yafewa mai shi ba ma zai shigar da shi wutar ba.
3- Lallai kafurci babba yana halatta jini da dukiya, kafurci karami ba ya halatta jini da dukiya.
4- Lallai kafurci babba yana wajabta kiyayya tsakanin mai shi da muminai, ba ya halatta ga muminani su so shi, su kaunaceshi ko da shi mafi kusancin makusanta ne. Amma kafurci karami ba ya hana kauna kwata-kwata, sai dai mai shi za a so shi, za a kaunace shi gwargwadon abin da ya ke da shi na imani, za a ki shi a yi gaba da shi gwargwadon abin da ya ke da shi na sabo.

***

1 - Shafin na ( 361) bugun Almaktab al-Islamiy.

## FASALI NA HUDU: MUNAFUNCI: MA’ANARSA – NAU’O’INSA

### (A) MA’ANARSA

Munafunci a harshen Larabci – masdari ne na: Ya yi munafunci, ana cewa Ya yi munafunci munafunci da munafunci, an samo shi daga rami: daya daga cikin mafitar kurege daga raminsa, idan aka tarfa shi ta daya sai ya gudu zuwa dayar ya fice ta ita, an ce kuma [an samo kalmar ne] daga gidan kasa, shi ne ramin da ake buya a cikinsa[1].

Amma munafunci a shari’a ma’anarsa ita ce: Bayyana Musulunci da boye kafurci da sharri, an kirashi da haka ne saboda ya shiga shari’a ta wata kofa kuma ya fita ta wata, a bisa wannan ne Allah SWT Ya fadakar da fadinSa: ***(Lallai munafukai su ne fasikai)*** **[Al-Taubah: 67].** Ai wadanda suka fice daga shari’a. Allah Ya sanya munafikai cewa sun fi kafirai sharri, sai Ya ce: ***(Lallai munafukai suna mataki na can kasa a wuta)*** **[al-Nisa’i: 145].** Allah S.W.T Ya ce: ***(Lallai munafukai suna yaudarar Allah alhali Shi kuwa mai mayar musu da sakamakon yaudarar ne)*** **[Al-Nisa’i: 142].** [ Suna yaudarar Allah da wadanda suka yi imani, ba kowa suke yaudara ba sai kansu, amma ba su sani ba, a zukatansu akwai ciwo sai Allah Ya kara musu ciwo, suna da azaba mai radadi sakamakon abinda suke karyatawa ) [al-Bakara: 9 -10].

### (B) NAU’O’IN MUNAFUNCI:

**Munafunci nau’i biyu ne: Nau’i na farko: Munafunci a akida, Shi ne munafunc** Babba wanda mai yinsa ya ke bayyana musulunci ya boye kafurci- wannan nau’in kafurci yana fitarwa daga Addini gaba daya, mai yinsa yana matakin kasa a wuta- Allah Ya siffanta masu yinsa da siffofin sharri gaba daya: Na kafurci da rashin imani, da yin izgilanci da Addini da masu shi, da yi musu wulakanci, da karkata gaba da zuwa makiya Addini domin tarayyarsu wajen gaba da Musulunci- Wadannan akwaisu a kowane zamani, musamman idan karfin Musulunci ya bayyana, suka kasa fito-na-fito da shi a fili, domin za su bayyana shiga cikinsa sabo da yi masa makirci da ma’abotansa a boye, saboda su rayu tare da musulmai, su kuma amintar

---

1 - Al-Nihaya ta ibnul Asir (5/98) a ma’ana.

da jininsu da dukiyarsu, sai munafiki ya bayyana imaninsa da Allah da mala'ikunSa da litattafanSa da manzanninSa da ranar lahira, amma a boye kuma ya fice daga cikinsa gaba daya kuma ya karyata shi, bai yi imani da Allah ba, [bai yi imani] da cewa Allah Ya yi magana da zancen da Ya saukar wa mutum ba, [bai yi imani] cewa ya sanyashi manzo ga mutane ba, yana shiryar da su da izininSa,yana gargadinsu fushinSa, yana tsoratar da su ukubarSa, Allah ya tona asirin wadannan munafukai, Ya tona asirinsu a cikin Alkur'ani mai girma, Ya bankadewa bayinSa al'amuransu don su yi hankali da su da ma'abotansu, Ya ambaci kungiyoyin mutanen duniya guda uku a farkon suratul Bakara; muminai da kafirai da munafukai. Ya ambaci ayoyi hudu game da muminai, ayoyi biyu game da kafirai, ayoyi goma sha uku game da munafukai, saboda yawansu, da gamewar bala'insu, da tsananin fitinarsu a kan Musulunci da ma'abotansa. Domin bala'in da musulunci ya shiga a sanadinsu yana da tsanani sosai saboda sun dangantu da shi, da taimaka masa, da kaunarsa, alhali kuwa su makiyansa ne a hakika, suna fito da gaba da shi ta kowane salo, mara sani zai zaci ilimi ne, kuma gyara nema alhali kuwa karshen jahilci ne da barna[1].

1 - Daga wata Risala ta Ibnul Kayyim wajen bayanin siffofin munafukai.

**Munafuncin nan nau'i shida (6) ne:**

1- Karyata manzo S.A.W.
2- Karyata wani bangare na abinda manzo SAW ya zo da shi.
3- Kiyayyar Manzo SAW.
4- Kiyayyar wani bangare na abin da manzo SAW ya zo da shi.
5- Yin murna da koma bayan addinin manzo SAW.
6- Kyamar taimakawa addinin manzo SAW.

**NAU'I NA BIYU: MUNAFUNCI A AIKI:** shi ne aikata wani abu daga ayyukan munafukai tare da wanzuwar imani a zuciya, wannan ba ya fitarwa daga Addini- sai dai hanya ne zuwa hakan. Mai yinsa zai zamo akwai imani da munafunci a tare da shi, idan kuma ya yi yawa zai zama munafuki tsantsa. Dalili a kansa fadin [annabi] SAW: ***"Abubuwa guda hudu wanda ya ke da su ya zama munafiki tsantsa, wanda ya ke da wata dabi'a daga ciki, to, ya zama yana da dabi'ar munafunci har sai ya daina, idan aka amince masa sai ya yi ha'inci, idan ya yi zance sai ya yi karya, Idan aka kulla alkawari da shi sai ya yi yaudara, Idan aka yi husuma da shi sai ya yi fajirci"***[1].

Wanda wadannan dabi'u hudun suka hadu a kansa , to, ya tattaro wa kansa dukkan sharri, siffofin muanfunci sun cika a tare da shi, wanda kuma yake da da dabi'a daya daga cikinsu, to, ya zama yana da dabi'ar munafunci – za a iya samun mutum yana da dabi'u na alheri da dabi'u na sharri, da dabi'u na imani, da dabi'u na kafurci da munafunci. Kuma ya cancanci lada da ukuba gwargwadon abin da ya ke da shi na kowanne. Daga ciki akwai kasala game da yin sallah cikin jam'i a masallaci, hakan yana daga cikin siffar munafukai, Munafunci sharri ne kuma hadari ne sosai, sahabbai sun kasance suna kaffa-kaffa game da fadawa cikinsa. Ibn Abu Mulaika ya ce: Na riski mutum talatin daga cikin sahabban manzon Allah SAW kowannesu yana jiyewa kansa tsoron munafunci.

---

1 -Bukhari da Muslim ne suka ruwaito shi.

**BANBANCI TSAKANIN MUNAFUNCI BABBA DA MUNAFUNCI KARAMI:**

1- Lallai munafunci babba yana fitarwa daga Addini, munafunci karami ba ya fitarwa daga addini.
2- Lallai munafunci babba shi ne abin da yake zuciya ya saba wa abin da ya ke fili a akida.
3- Lallai munafunci babba ba ya faruwa daga mumini, amma munafunci karami ya kan faru daga mumini.
4- Munafunci babba a galibi mai yinsa ba ya tuba, ko da ya tuba an yi sabani game da karbar tubansa a wajen shugaba (alkali), sabanin munafunci karami, lallai mai yin sa ya kan tuba zuwa ga Allah kuma ya karbi tubansa. **Sheikhul Islam Ibn Taimiya** ya ce[1]: "Sau da yawa mumini ya kan fada wani bangare daga bangarorin munafunci sai Allah S.W.T Ya karbi tubansa. Kuma wani abu ya kan gangaro zuwa zuciyarsa cikin abubuwan da suke tabbatar da munafunci, sai Allah Ya yi masa maganinsa. Mumini ana jarrabarsa da wasiwasin Shaidan Da kuma wasiwasin kafurci wadanda za su makure kirjinsa. Kamar yadda Sahabbai suka ce: Ya manzon Allah hakika dayanmu ya kan ji a ransa irn abin ya fi mai sauki ya rikito daga sama a kan ya furta shi, sai ya ce: ***"Wannan ai shi ne gangariyar imani"***[2] A wata riwayar "Abin ya yi nauyi ace an furta shi" sai ya ce: ***"Godiya ta tabbata ga Allah da Ya mayar da kaidinsa ya zama wasiwasi"*** – ai samuwar wannan wasiwasi tare da jin wannan kyamar babba, da kawar dashi daga zuciya, shi ne gangariyar imani- maganar ta kare.

Amma masu munafunci babba, Allah Ya fada game da su cewa: (Su kurame ne, bebaye ne, makafi ne, don haka ba za su taba dawowa ***(kan gaskiyaba)*** **[Al-Bakara: 18].** Ai zuwa Musulunci a badini. Allah SWT ya ce: ***(Shin yanzu ba sa ganin cewa ana jarrabarsu sau daya ko sau biyu, sannan ba sa tuba, sannan ba sa wa'azantuwa)*** **[Al-tauba: 126].**

---

1 - Duba Kitabul Iman shafi 238.
2 -Ahmad da Muslim ne suka ruwaito shi.

Sheikhul Islam Ibn Taimiya ya ce: Malamai sun yi sabani game da karbar tubansu a zahiri, saboda ba za a iya gane hakan ba, domin su a koda yaushe suna bayyana Musulunci"[1].

***

1 - Duba Majmu'ul fatawa (28/434 -435)

## FASALI NA BIYAR: BAYANIN HAKIKAR KOWANNE CIKIN:

## JAHILIYYA – FASIƘANCI – ƁATA – RIDDA

## RABE-RABENSU – HUKUNCE-HUKUNCENSU

### 1. JAHILIYYA:

Ita ce halin da larabawa su ke ciki kafin Musulunci game da rashin sanin Allah da manzanninsa da dokokin Addini, da tutiya da nasaba, da girman kai, da nuna isa, da sauransu[1]. An danganta ne zuwa jahilci wanda kishiyar ilimi ne, ko rashin bin ilimi. Sheikhul Islam Ibnu Taimiya ya ce: "Idan [mutum] bai san gaskiya ba, to, ya zama jahili matakin farko, idan kuma ya san abin ba a yadda ya ke ba, to, ya zama jahili jahilci mai ninkuwa, idan an fahimci wannan, to, mutane kafin aiko manzon Allah SAW sun kasance ababan dangantawa zuwa jahilci, domin abin da suke kansa na maganganu da ayyuka jahilci ne ya haifar musu da shi, abin da suke yi jahilci ne, haka nan duk abin da ya saba abin da manzanni suka zo da shi Yahudanci ne ko Nasaranci, to, shi ma Jahiliyya ne, Wannan ita ce jahiliyya gamammiya- Amma bayan aiko manzo S.A.W tana kasancewa a wasu garin ban da wani, kamar yadda take a garin kafirai. Kuma ta kan kasance a wani mutumin ban da wani, kamar mutum kafin ya musulunta, to, ai yana cikin Jahiliyya, ko da yana rayuwa a garin Musulunci, amma a zamani kawai, to, babu Jahiliyya bayan aiko [Annabi] Muhammad S.A.W. Domin har yau wata tawaga daga cikin al'umarsa ba su gushe ba suna taimakawa gaskiya har izuwa tashin Alkiyama Jahiliyya kayyadaddiya tana iya kasancewa a gidajen wasu musulmai tare da wasu da yawa daga cikin musulmai, kamar yadda Manzon Allah SAW ya ce: ***"Wasu abubuwa guda hudu a cikin al'ummta suna daga cikin al'amarin jahiliyya"***[2], Ya ce da Abu Zarr: ***"Lallai kai mutum ne wanda akwai jahiliyya a tare da kai"***[3]. Da abin da ya yi kama da haka. Maganar ta kare[4].

1 -Al-Nihaya ta ibnul Asir (1/323).
2 - Muslim ne ya ruwaito shi.
3 -Ya zo a cikin Sahihaini.
4 - Iqtida'us Siratil Mustaqim (1L/ 225 -227), Tahkik: Nasir Al-akl.

**Bayanin hakan a dunkule: Lallai Jahiliyya dangantawa ne zuwa jahilci, wanda shi ne rashin ilimi, kuma ta rabu gida biyu:**

1- ***Jahiliyya gamammiya:*** ita ce wadda ta kasance kafin aiko Manzon Allah SAW kuma ta kare da aiko shi.
2- ***Jahiliyya kebatacciya da wasu kasashe,*** da wasu garuruwa da wasu mutane, irin wannan ba ta gushe ba akwaita. Da wannan ne kuskuren masu yin kudin goro a batun Jahiliyya ya ke bayyana, sai ka ji suna cewa: Jahliyya wannan karnin da abin da ya yi kama da haka, abin da ya ke daidai shi ne a ce; Jahiliyyar wasu 'yan wannan karnin, amma yin kudin goro ba ya inganta, kuma ba ya halatta, Sabo da aiko Annabi Muhammad SAW ya kore Jahiliyya gamammiya.

## 2. FASIƘANCI:

***Fasikanci a harshen larabci shi ne:*** fita, abin nufi da shi a shari'ance shi ne: fita daga da'ar Allah Ya kunshi fita ta gaba daya, sai a ce da kafiri: Fasiki, da kuma ta wani bangare; sai a ce da mumini mai aikata babban laifi daga cikin manyan laifuka; fasiki.

***Fasikanci kala biyu ne:*** Fasikanci mai fitarwa daga Addini shi ne kafurci, sai a ambaci kafiri da [suna] fasiki, Allah Ya ambaci Iblis sai Ya ce: ***(Sai ya yi fasikanci (ya fita) daga umarnin Ubangijinsa)*** **[al-Kahf:50].** Wannan fasikancin nasa kafurci ne. Allah S.W.T Ya ce: ***(Amma wadanda suka yi fasikanci (fita daga da'ar Allah), to, makomarsu wuta ce)*** **[al-Sajdah: 20],** Yana nufin kafirai, akwai fadinSa da ya yi nuni a kan haka: ***(Duk lokacin da suka so fitowa daga ciknta sai a mayar da su cikinta, sai a ce da su kudandani azabar wutar da ku ka kasance kuna karyatawa)*** **[Al-Sajdah: 40],** ana kiran mai sabo daga cikin musulmai fasiki, fasikancinsa bai fitar da shi daga Musulunci ba, Allah S.W.T Ya ce: ***(Kuma waɗanda ke jĩfar mãtã masu kãmun kai, sa'an nan kuma ba su jẽ da shaidu huɗu ba to, ku yi musu bũlãla, bũlãla tamãnin, kuma kada ku karɓi wata shaida tãsu, har abada. Waɗancan su ne fãsiƙai)*** **[Al-Nur:4].** [Allah] SWT Ya ce: ***(To, wanda ya yi niyyar hajji a cikinsu to bãbu jimã'i kuma bãbu***

***fãsiƙanci, kuma bãbu jãyayya a cikin hajji)*** **[Al-Baqarah:197].** Wajen tafsirin fasikanci a nan malamai suka ce shi ne ayyukan sabo.[1]

### 3. ƁATA:

Bata shi ne: Kaucewa hanya mikakkiya, kishiyar shiriya, Allah SWT Ya ce: ***(Wanda ya nẽmi shiryuwa, to, ya nẽmi shiryuwa ne dõminkansa kawai kuma wanda ya ɓace, to, ya ɓace ne a kansa kawai)*** **[Al-Isra'i:15].**

**ƁATA ANA FADARSA A MA'ANONI MASU YAWA**:

1. Wani lokaci ana faɗarsa ana nufin kafurci, Allah SWT Ya ce: ***(To, wanda ya kãfirta da Allah da malã'ikunSa, da LittattafanSa, da ManzanninSa, da Rãnar Lãhira, to, lalle ne yã ɓace, ɓata mai nĩsa)*** **[Al-Nisa'i:136].**
2. Wani lokaci ana faɗarsa ana nufin shirka, Allah SWT Ya ce: **(Kuma wanda ya yi shirki da Allah, to, lalle ne ya ɓace ɓata mai nĩsa) [Al-Nisa'i:116].**
3. A wani lokacin ana faɗarsa ana nufin saɓawa wadda ba ta kai kafurci ba – kamar yadda ake cewa ƙungiyoyi ɓatattu da wadanda suka saɓa.
4. A wani lokacin ana faɗarsa ana nufin kuskure, a irin wannan ne maganar [Annabi] Musa - amincin Allah gareshi - ta ke: Ya ce: ***(Na aikata shi a lõkacin inã daga mãsu jãhilcin fushi)*** **[Al-Shu'ara:20].**
5. A wani lokacin ana faɗarsa ana nufin mantuwa yana daga cikin hakan fadinSa SWT: ***(Idan dayarsu ta manta sai dayar ta tuna mata)*** **[Al-Bakarah: 282].**
6. Ana faɗar ɓata ana nufin ɓacewa ko rasawa, daga nan ne ma ake cewa: Bataccen ra rakumi.

### 4. RIDDA DA RABE-RABENTA DA HUKUNCE-HUKUNCENTA:

**Ridda a harshen Larabci ita ce:** Komawa, Allah S.W.T Ya ce: ***(Kada ku koma kan duga-duganku)*** **[Al-Ma'idah:21]** ai kar ku koma – Ridda a wajen malaman Fiqhu: Ita ce Kafurci bayan Musulunci – Allah SWT ya ce: ***(Wanda ya yi ridda a cikinku, sai ya mutu yana kafiri,***

1 - Kitabul Iman na Sheikhul Islam Ibn Taimiyah (278).

***wadannan ayyukansu sun rushe a duniya da lahira, wadannan su ne 'yan wuta, su masu dawwama ne a cikinta)*** **[Al-Bakarah:217].**

**RABE-RABENTA:** Ridda tana faruwa ne ta hanyar wani abu mai warware Musulunci, abubuwan da suke warware Musulunci suna da yawa , an raba su gida hudu su ne:

1- ***Ridda ta hanyar magana:*** kamar zagin Allah S.W.T ko ManzonSa SAW ko mala'ikunSa ko wani cikin manzanninSa, ko da'awar ilimin gaibi, ko da'awar annabta, ko gasgata wanda ya ke da'awarta, ko rokon wanin Allah, ko neman taimakonSa cikin abin da ba mai ikonsa sai Allah, ko neman tsarinSa wajen haka.
2- ***Ridda ta hanyar aiki:*** Kamar sujjada ga gunki da bishiya da dutse da kaburbura da yanka dominsu, da yin wurgi da Al-Kur'ani cikin wuraren kazanta, da yin tsafi da koyonsa da koyar da shi da yin hukunci da wanin abin da Allah Ya saukar tare da kudirce halaccinsa.
3- ***Ridda ta hanyar Akida:*** Kamar kudirce abokin tarayya ga Allah, ko cewa zina da shan giya da riba halal ne, ko cewa gurasa haram ce, ko cewa sallah ba wajibi ba ce, da makamantan haka daga cikin abin da aka yi Ijima'i a kan halaccinsa ko wajibcinsa bisa Ijma'i yankakke, kuma irin wannan ba'ajahiltarsa.
4- ***Ridda ta hanyar kokonto cikin wani abu da ya gabata:*** Kamar wanda ya yi kokonto wajen haramcin shirka ko haramcin zina da giya – ko wajen halaccin gurasa, ko kokonto cikin manzancin Annabi S.A.W ko manzancin waninsa daga cikin Annabawa ko game da gaskiyarsa ko cikin Addinin Musulunci, ko ingantuwarsa ga wannan zamani.

**HUKUNCE-HUKUNCEN DA SUKE BIYO BAYANTA BAYAN TA TABBATA:**

1- Neman tuban wanda ya yi ridda – idan ya tuba ya dawo zuwa Musulunci cikin kwana uku sai a karba kuma a kyaleshi.
2- Idan ya ki tuba, to, ya wajaba a kasheshi saboda fadin Annabi SAW: ***"Wanda ya sauya addinisa ku kashe shi".***[1]
3- Za a hanashi sarrafa dukiyarsa tsawon lokacin neman tubansa, in ya dawo musulunci sai a mayar masa, idan ba haka ba, to, ya zama fai'i zuwa baitul-mal daga lokacin da aka kasheshi, ko ya mutu a kan riddar. An ce ai tun daga lokacin riddar ta sa za a sanya dukiyarsa cikin abinda zai amfani musulmai.
4- Cin gado ya yanke tsakaninsa da 'yan uwansa , ba zai gajesu ba, ba za su gajeshi ba.
5- Idan ya mutu ko aka kasheshi a kan riddarsa, to, ba za a yi masa wanka ba, ba za ayi masa sallah ba, ba za'a binneshi a makabartar musulmai ba, sai dai za a binne shi a makabartar kafirai, ko a binne a wani wajen da ba makabartar musulmai ba.

***

1 - Bukhari da Abu Dawud ne su ka ruwaito shi.

# BABI NA BIYU

## MAGANGANU DA AYYUKAN DA SUKE WARWARE TAUHIDI KO SU TAUYESHI

**A CIKINSA AKWAI FASALAI MASU ZUWA:**

**FASALI NA FARKO:** DA’AWAR SANIN GAIBI WAJEN KARANTA TAFI KO FINJANI DA DUBA (ILIMIN TAURARI) .. DA SAURANSU.

**FASALI NA BIYU:** SIHIRI BOKANCI DA BUGUN KASA.

**FASALI NA UKU:** GABATAR ABUBUWAN YANKA DA BAKANCE DA YIN KYAUTUTTUKA GA WAJEN ZIYARCE-ZIYARCE DA KABURBURA DA KUMA GIRMAMASU.

**FASALI NA HUDU:** GIRMAMA MUTUM-MUTUMI DA GIRKAKKUN ABUBUWAN TARIHI.

**FASALI NA BIYAR:** IZGILANCI GA ADDINI DA WULAKANTA ALFARMARSA.

**FASALI NA SHIDA:** HUKUNCI DA WANIN ABIN DA ALLAH YA SAUKAR.

**FASALI NA BAKWAI:** DA’AWAR HAKKIN YIN DOKA DA HALATTAWA DA HARAMTAWA.

**FASALI NA TAKWAS:** DANGANTUWA ZUWA MAZHABOBIN KARYATA SAMUWAR ALLAH DA KUNGIYOYI NA JAHILIYYA.

**FASALI NA TARA:** KALLON RAYUWA A MATSAYIN ABIN DUNIYA KAWAI.

**FASALI NA GOMA:** LAYU DA TAWAIDA.

**FASALI NA GOMA SHA DAYA:** RANTSUWA DA WANIN ALLAH, DA TAWASSALI, DA NEMAN TAIMAKO DA ABIN HALITTA DA ALLAH.

## FASALI NA FARKO: DA’AWAR SANIN GAIBI WAJEN KARANTA TAFI KO FINJANI DA DUBA (ILIMIN TAURARI) .. DA SAURANSU

## ABIN NUFI DA GAIBI:

Abin da ya buya daga mutane na al’umuran da za su faru nan gaba da wadanda su ka wuce da kuma abin da ba sa gani, Allah ne Ya kebanta da saninsa, Allah SWT Ya ce: ***(Ka ce: Duk wadanda su ke sama da wadanda su ke kasa babu wanda ya san gaibi sai Allah)*** **[ al-Naml:65].** Babu wanda ya san gaibi sai Allah S.W.T Shi kadai, Ya kan nuna wa ManzanninSa abinda Ya so na gaibinSa domin wata hikima da maslaha, Allah S.W.T Ya ce: ***(Masanin gaibi ba Ya nuna wa kowa gaibinSa. Sai dai wanda Ya so daga cikin manzanninSa)*** **[Al-Jinn:26 - 27].** Ai ba wanda ya ke nuna wa wani abu na gaibi sai wanda Ya zaba da manzancinSa, Sai Ya nuna masa abin da Ya so na gaibi wanda Allah zai tsinkayar da shi saboda manzancinsa, sai ya nuna masa abin da ya so na gaibin, saboda yana kafa dalili a kan annabtarsa da mu’ujizozi wanda daga ciki akwai bayar da labarin gaibi wanda Allah Ya ke tsinkayar da shi, wannan ya kunshi manzo daga mala’iku da kuma daga mutane, waninsu ba Ya tsinkayar da waninsu kenan saboda dalilin iyakancewa (hasr), duk wanda ya yi da’awar gaibi ta kowace hanya daga hanyoyi in banda wadanda Allah Ya togace daga ManzanninSa, to, makaryaci ne kafiri – duk daya ne shin ya yi da’awar hakan ne ta hanyar tafin [hannu], ko finjani ko bokanci ko tsafi ko duban taurari ko sauransu – wannan ne ya ke faruwa daga wasu ‘yan bori da kuma dajjalai wajen ba da labarai na wajen abubuwan da aka rasa, da abubuwan da ba sa nan, da dalilan wasu cututtukan, sai su ce wane ne ya yi maka kaza-da-kaza sai ka kamu rashin lafiya a dalilinsa, kuma ta hanyar amfani da aljanu da shaidanu ne, amma sai su bayyanawa mutane cewa wannan abu yana faruwa ne ta hanyar aikata wadannan abubuwan duk hanyar yaudara ce da rufa ido. Sheikhul Islam Ibnu Taimiyah ya ce[1]: “Bokaye sun kasance dayansu zai zama yana da karini (wani aljani da yake manne da shi) daga cikin shaidanu zai rika ba shi labarin abubuwa da yawa na gaibi ta hanyar sato magana da yake yi, kuma sun kasance suna cakuda gaskiya da karya, har dai inda ya ce: A cikin wadannan akwai wadanda shaidanu suke zuwar musu da abinci:

1 -Duba: Majmu’atu al-tauhid (797 - 801)

Kayan marmari, alawa, da sauransu irin abin da babu a nan wurin, acikinsu akwai wanda aljanin yake tashi da shi zuwa Makka ko Baitul Mukaddas ko wani wurin – [magnar] ta kare.

Kuma ba su labarin zai iya kasancewa ta hanyar ililmin taurari – shi ne kafa dalili da yanayin falaki a kan abubuwan da suke faruwa a doron duniya: kamar lokutan kadawar iska, da zuwan ruwan sama, da sauyawar farashi da sauransu cikin al’amuran da suke raya cewa sun samo saninsu ne ta hanyar tafiyar taurari a matafiyarsu da kuma haduwarsu da rabuwarsu. Suna cewa: Wanda ya yi aure a tauraro kaza-da- kaza, to, kaza-da- kaza zai faru da shi. Wanda ya yi balaguro a tauraro kaza, to, kaza zai faru da shi, wanda aka haifeshi a tauraro kaza-da-kaza, to, kaza-da-kaza zai faru da shi na arziki (Sa’id) ko na tsiya (Nahis) . kamar yadda wasu mujallu na banza suke sanarwa game da shirme (khuza’abalat), game da burujai da abin da ya ke gudana a cikinsu na rabo.

Lallai Wasu jahilan da masu raunin imani su kan je wajen wadannan masu ilimin taurarin, sai su tambayesu game da rayuwarsu ta gaba, da abinda ya ke faruwa a tare da shi, da kuma aurensa da sauransu, wanda duk ya yi da’awar sanin gaibi, ko gaskiyar wanda ya ke da’awar, to, ya zama mushiriki Kafiri; sabo da yana dea’awar tarayya da Allah cikin abin da Ya kebanta da shi, taurari an fuwacesu ababan halitta ne, ba su da komai , kuma ba ya nuni a kan tsiya (Nuhus) ko Sa’ud babu mutuwa babu tashi [bayan mutuwa], babu wata rayuwa, kadai dai wannan ya kasance daga ayyukan shaidanun da suke sato magana.

***

## FASALI NA BIYU: TSAFI (SIHIRI) BOKANCI DA DUBA

Dukkan wadannan al'amura suna daga cikin ayyukan Shaidan haramtattu, suna cin karo da Akida ko ma su warwareta, saboda ba ayinsu sai da al'amura na shirka:

1- **SHI TSAFI (SIHIRI)** – bayani ne game da abin da ya buya kuma dalilin faruwarsa kadan ne:
An ambace shi Sihiri ; saboda yana faruwa ta hanyar wasu al'amura boyayyu, da ba a ganinsu da idanu – sune layu da tawaida da wani irin zance da ake yinsa, da wasu magunguna da hayaki, kuma gaske ne, daga cikinsa akwai irin wanda ya ke tasiri a zukata da jiki, sai ya jawo rashin lafiya, kuma yana kisa, yana rabawa tsakanin mutum da matarsa, amma tasirinsa yana kasancewa ne da izinin Allah na halitta da kaddara – shi din aiki ne na shaidanci- da yawansa ba a kai wa ga gaci sai an yi shirka, da neman kusanci da mugayen rauhanai da irin abin da suke so, kuma kai wa izuwa amfani da su (sa su aiki) yana faruwa ne ta hanyar yin shirka da su- shi ya sa Mai shari'a (Allah) Ya hadasu da shirka, inda Annabi S.A.W ya ke cewa: ***"Ku nisanci abubuwa bakwai masu hallakarwa, sai suka ce: Menene su? Sai ya ce: "Hada Allah da wani, da Tsafi***"[1].. Hadith. Ya shiga shirka ta nahiya biyu:

**NAHIYA TA FARKO:** Abin da ya ke ciki na amfani da shaidanu da ratayuwa da su, da neman kusanci zuwa garesu da abin da suke so don su yi wa matsafin aiki, tsafi dai yana daga cikin koyarwar shaidanu, Allah SWT Ya ce: [Sai dai shaidanu sun kafurta) [ al-Bakarah: 103].

**NAHIYA TA BIYU:** Abin da ya ke cikinsa na da'awar gaibi da da'awar tarayya da Allah cikin hakan, wannan kafurci ne, kuma bata ne, Allah SWT Ya ce: (Lallai sun sani cewa Wanda duk ya sayeshi [tsafin] a lahira ba shi da rabo ) [ al-Bakarah: 102] ai kaso, idan kuwa haka ne, to, babu shakka cewa kafurci ne, shirka ne yana cin karo da Akida, kuma ya wajaba a kashe mai yinsa, kamar yadda sahabbai da yawa -Allah Ya yarda da su- sun kashe, mutane sun yi

1 - Bukhari da Muslim ne suka ruwaito.

sakaci game da lamarin matsafi da tsafi, har wasu suna ganinsa a matsayin wani fanni daga cikin fannoni wanda suke alfahari da shi, har ma suke bai wa masu yi kyauta da kwarin gwuiwa, suke shirya dandali da tarurruka da gasar matsafa, dubunnan masu kallo da masu goyon baya suke zuwa shakatawa. Wannan rashin sanin Addini ne da kuma sakaci game da lamarin Akida da kuma bayar da dama ga masu wasa da ita.

**2- BOKANCI DA DUBA:**

Su din da'awar ilimin gaibi ne da sanin al'amuran da suke a boye: Kamar bayar da labarin abin da zai faru a duniya da abin da zai biyo baya, da bayanin wajen da abin da ya bata ya ke, duk wannan duk ta hanyar amfani da shaidanu wadanda suke sato magana daga sama, Allah SWT Ya ce: ***(Shin ba na ba ku labarin wadanda shaidanu suke sauka a wajensu ba. To, suna sauka ne a wajen duk mai kagar karya mai saɓo. Suna jefawa {bokaye] abin da suka sato jinsa, yawancinsu kuwa makaryata ne)*** **[Al-Shu'ara: 221 - 223].** Hakan yana faruwa ne saboda shaidanin yana sato kalma daga zancen mala'iku, sai ya jefata a kunnen bokan, sai bokan ya shirya karya dari ta hanyar amfani da wannan kalamar, sai mutane su gasgata shi saboda waccan kalmar da aka jiyo daga sama, Allah Shi kadai ne Ya kebanta da sanin gaibi, duk wanda ya yi da'awar tarayya da shi a wani abu cikin wani abu ta hanyar bokanci ko wani abu, ko ya gasgata wanda ya ke da'awar hakan, to, ya sanyawa Allah abokin tarayya cikin abin da ya kebance Shi. Bokanci ba ya rabuwa da shirka; saboda neman kusancin shaidanu ne cikin abin da su ke so. Don haka shirka ce a *Rububiyya* ta fuskar da'awar tarayya da Allah a cikin iliminSa, Kuma shirka ce a *Uluhiyya* ta fuskar neman kusanci zuwa wanin Allah da wani abu na ibada, daga Abu Hurairah –Allah Ya yarda da shi- daga Annabi SAW ya ce: ***"Wanda ya je wajen boka sai ya gasgata shi cikin abin da ya fada , to, ya kafircewa abin da aka saukarwa [Annabi] Muhammad SAW"***.[1]

[1] -Abu Dawud ne ya ruwaito shi.

***Yana daga cikin abin da yake wajaba ayi fadakarwa a kansa:*** a ja hankali saboda shi: Cewar matsafa da bokaye da ‘Yan duba suna wasa da Akidun mutane, suna bayyana a siffar masu magani, sai su umarci marasa lafiya da yin yanka ga wanin Allah – cewa su yanka rago mai siffa kaza-da-kaza ko [a yanka] kaza, ko su rubuta musu saƙandamai na shirka da ta’awizai na shaidanu da sunan tsari (hirzi) suka rika ratayawa a wuyansu, ko su sanya a akwatunansu ko gidajensu. Wasu kuma sai ya bayyana a siffar mai ba da labarin gaibi, da wuraren [da za a sami] abubuwan da suka bata, ta yadda jahilai za su rika zuwa wajensa suna tambayarsa game da abubuwan da suka bata sai ya ba su labarinsu, ko ma ya kawo musu su ta hanyar shaidanu masu tayashi aiki, wani kuma sai ya bayyana da siffar waliyyi wanda yake da abubuwan da suka sabawa al’ada da karamomi, kamar shiga wuta ba tare da ta kona shi ba, da dokawa kansa makami, ko ajiye kansa karkashin tayar mota, ba tare da sun yi masa tasiri ba, ko kuma dai wani abin na rufa-ido wanda a hakikarsa tsafi ne yana daga cikin aikin Shaidan wanda ya ke gudana a hannun wadannan saboda fitina, ko kuma wasu abubuwa ne da suke cikin tunani kawai wadanda ba su da tabbas, kawai dai dabaru ne boyayyu kawai da suke yinsu a gaban idon mutane kamar aikin bokayen Fir’auna da suka yi da igiyoyi da sanduna- Sheikhul Islam Ibn Taimiya ya fada a tattaunawarsa da matsafan *Bata’ihiyyar Ahmadiyya* (Rufa’iyya), ya ce: (yana nufin Shehin *Bata’ihiyya*) ya daga muryarsa: Mu muna da wasu halaye da kaza-da-kaza. Ya yi da’awar halaye masu sabawa al’ada kamar wuta da waninta da kebantarsu da ita. Kuma cewa su sun cancanci sallama mata sabo da ita- Sheikhul Islam ya ce: :Sai na fada kuma na daga muryata na yi fushi: Ni ina magana da duk dan Ahmadiyya tun daga gabashin duniya har yammacinta, duk abin da za ku yi a wuta ni ma zan yi irin abin da ku ka yi, duk wanda ya kone an cinye shi. Mai yiwuwa ma na ce: Allah ma Ya tsine masa- amma sai bayan an wanke jikimmu da *Khal* da ruwa mai zafi- sai sarakuna da sauran mutane suka tambayeni game da hakan, sai na ce: Saboda suna da wasu dabaru da suke game da wuta na [hade-haden] mai da kwaɗi da ɓawon lemo mai ɗaci *(citrus aurantium ),* da dutsen tok (Talc stone), sai mutane suka yi ihu da jin haka- sai ya rika nuna damar yin hakan , sannan ya ce: Ni da kai a nademu a cikin [tabarmar] kaba, bayan mun shafe jikimmu da farar wuta. Sai na ce: To, tashi, na rika maimaita masa maganar a tashi ayi, sai ya mika hannunsa yana yin kamar zai cire riga, sai na ce: A’a,

sai bayan ka yi wanka da ruwan zafi da *khal*, sai ya rika nuna cewa bai gane ba kamar yadda yake a al'adarsu, sai ya ce: Wanda duk ya ke kaunar sarki ya je ya kawo katako. Ko kuma cewa ko ya je ya kawo damen itace, sai na ce: Ai duk wannan bata lokaci ne, kuma neman watsa mutane ne, kuma ba da shi za a yi abin da ake nufi ba. Kawai a samo fitila da za a kunna in shigar da yatsana da yatsanka a ciki bayan wankewa, duk wanda na sa ya kone Allah Ya tsine masa, ko kuma cewa na yi an cinyeshi, da na fadi haka sai ya sauya kuma ya kaskanta- [maganar] ta kare.[1] Abin nufi a wannan shi ne bayanin cewa wadannan makaryata suna yi wa mutane karya ne da irin wadannan dabarun boyayyu.

[1] - Majmu'ul Fatawa: 11/ 446 – 465.

## FASALI NA UKU: GABATAR DA ABUBUWAN YANKA DA BAKANCE DA KYAUTUTTUKA GA MAZIYARTA (WAJEN ZIYARA) DA KABURBURA DA GIRMAMASU

Hakika Manzon Allah S.A.W ya toshe duk wata hanya da za ta kai zuwa shirka, ya tsawatar game da ita iya tsawatarwa, yana daga cikin hakan mas'alar kaburbura, hakika ya sanya ƙa'idoji da za su tsare daga bautarsu, da zaƙewa a kan ma'abotan [kaburburan], yana daga cikin hakan:

1- Lallai [Annabi] S.A.W ya tsawatar game da Waliyai da Salihai, saboda hakan yana kai wa zuwa bauta musu, sai ya ce: ***"Ina yi muku kashedi a kan zaƙewa, lallai abin da ya halakar da wadanda aka yi kafinku shi ne zaƙewa"[1]. Kuma ya ce :"Kada ku zaƙe wajen yabona kamar yadda Nasara suka zaƙe a kan [Annabi Isa] Dan Maryam, ni dai bawan Allah ne, ku ce: Bawan Allah da ManzonSa".***[2]

2- [Annabi] S.A.W ya tsawatar a kan yin gini a kan kaburbura – kamar yadda Abul Hayyaj al-Asadiy ya ruwaito ya ce: Aliyyu dan Abu Dalib –- Allah Ya yarda da shi - ya ce: ***"Shin ba na aikeka a kan abin da Annabi SAW ya aike a kansa ba, kar ka bar wani mtum-mutumi sai ka shafeshi, ko wani kabari da aka daga shi face ka daidaita shi [da ƙasa].***[3] Ya hana a sumunceshi da yin gini a kai, daga Jabir -Allah Ya yarda da shi – ya ce: ***"Manzon Allah SAW ya hana sumunce kabari, da zama a kai, da yin gini a kai"***[4]

3- [Annabi] S.A.W ya tsawatar a kan yin sallah a wajen kabari, daga nana A'isha – Allah Ya yarda da ita- ta ce: Yayin da aka saukarwa Manzon Allah SAW [ajali], sai ya riƙa ture mayafin da ya ke fuskarsa, idan numfashin ya toshe sai ya yayeshi, sai ya fada alhali yana wannan yanayi: La'anar Allah ta tabbata a kan Yahudu da Nasara sun riƙi kaburburan annabawansu masallatai, [ya fada] yana gargadi game da abin da suka aikata, ba don haka ba da an fito da kabarinsa, sai dai ya jiye tsoron kar a riƙeshi masallaci"[5]. Manzon Allah SAW ya ce:

---

[1] - Imam Ahmad da Tirmiziy da Ibn Majah ne suka ruwaito shi.
[2] - Bukhari ne ya ruwaito shi
[3] - Muslim ne ya ruwaito shi.
[4] -Muslim ne ya ruwaito shi.
[5] - Bukhari da Muslim ne suka ruwaito shi.

***“Ku saurara hakika wadanda aka yi kafinku sun kasance suna rikar kaburburan annabawansu masallatai, ku saurara kada ku riki kaburbura a matsayin masallatai, lallai ina hanaku yin haka”***[1]. Rikarsu a matsayin masallatai yana nufin yin sallah a wajensu, ko da ba agina masallacin a kai ba, duk wajen da ake yin sallah a cikinsa ya zama masallaci. Kamar yadda [Annabi] S.A.W ya ce: ***“An sanya min kasa ta zama masallaci kuma abin yi tsarki”***[2]. Idan kuma aka gina masallacin a kai , to, lamarin ya fi muni.

Da yawan mutane sun sabawa wadannan hane-hanen , sun aikata abin da Annabi SAW ya tsawatar a kai, a dalilin haka sun fada a cikin babbar shirka: irin su yin yanka dominsu, da rokon ma’abotansu, da neman agaji da su, da sarrafa bakance zuwa garesu, da sauransu, Babban malami Ibnul Kayyim -Allah Ya yi masa rahama- ya ce: Wanda ya tattara tsakanin sunnar Manzon Allah SAW game da kaburbura da abin da ya yi umarni da shi da wanda ya hana da abin da sahabbansa suke kai, da kuma tsakanin abin da yawancin mutane a yau[3] suke zai ga daya yana kishiyantar dayan, yana warwareshi ta yadda ba za su hadu ba har abada.

Manzon Allah S.A.W ya hana yin sallah zuwa kaburbura, wadannan su kuma suna yin sallah ne a wajensu [kaburburan], kuma ya hana a rikesu masallatai, wadannan su kuma gina masallatan su ke yi a kai, suna kiransu da *Mashahida*, suna masu kwaikwayon dakin Allah, ya hana kunna musu fitilu, wadannan kuwa har wakafi suke sanyawa a kan kunna musu [kaburbura] fitilu, kuma ya hana a rikesu a matsayin idi, wadannan kuwa suna rikarsu a matsayin idi da wuraren bauta. Suna taruwa a wajen kamar taruwar idi ko ma sama da haka, ya yi umarni a bajesu – kamar yadda Muslim ya ruwaito a Sahihinsa daga Abul-Hayyaj al-Asadiy ya ce: Aliyu dan Abu Dalib –Allah Ya yarda da shi- ya ce da ni: ***“Shin ba na aike ba a kan irin abin da Manzon Allah SAW ya aike ni a kai ba? Kar ka bar wani hoto sai ka shafeshi, ko wani kabari da aka daga shi sai ka bajeshi”, A cikin***

---

[1] - Muslim ne ya ruwaito shi a Shihinsa.

[2] - Bukhari ne ya ruwaito shi.

[3] -Yana nufin a lokacinsa –Allah Ya yi masa rahama- lamarin ya ma wuce yadda aka ambata.

***Sahihinsa kuma daga Sumamah dan Shufiy ya ce: Mun kasance tare da Fadala dan Ubaid a kasar Rum [yankin] Rudis sai wani abokimmu ya rasu, sai fadala ya ba da umarni a daidaita kabarinsa, sannan ya ce: Na ji Manzon Allah S.A.W yana ba da umarnin a daidaitasu"***[1]. [ka ga] Wadannan suna zakewa da yawa wajen sabawa wadannan hadisai guda biyu, Suna ɗaga su [su yi tudu] kamar ɗaki. Suna ɗora musu ƙubba- har dai ya ce: Kalli wannan tazara mai girma tsakanin abin da Annabi S.A.W ya shara'anta kuma ya nufa game da hanin da ya yi a kan abin da ambatonsa ya gabata a kan kaburbura, da kuma abin da su wadannan suka shara'anta kuma suka nufa, babu kokoknto cewa wajen yin haka akwai barnar da mutum ba zai iya lissafeta ba- sannan ya fara ambaton barnar, har ya ce: Daga ciki [akwai] cewa abin da Annabi S.A.W ya shara'anta wajen ziyarar kabubura shi ne tunowa da lahira da kyautatawa wanda aka yi wa ziyarar ta hanyar yi masa addu'a, da nema masa rahama da gafara, da roƙa masa lafiya, sai ya zama shi mai ziyara ya kyautatawa kansa [kuma ya kyautata wa] mamacin, sai su wadannan masu shirka suka juyar da lamarin, suka jirkita Addini, suka mayar da manufar ziyara ita ce yin shirka da mamacin, da roƙonsa, da yin kamun ƙafa da shi, da roƙon buƙatunsu, da neman saukar albarka daga shi [mamacin], da taimaka musu a kan maƙiya da makamancin haka, sai suka zamo suna munanawa kansu da shi mamacin, ko ba komai sun haramta masa albarkar abin da Allah Ya shara'anta na addu'a da nema masa rahama da nema masa gafara.. maganar ta ƙare.[2]

Da wannan ne zai bayyana cewa gabatar da bakance da abubuwan yanka ga wuraren ziyarar [ibada] shirka ce babba, dalilinsa shi ne saɓa wa tsarin manzon Allah S.A.W a yanayin da ya wajaba kabubura su kasance, na rashin yin gini a kansu, da yin masallatai a kansu- saboda yayin da aka gina ƙubba a kansu, aka yi masallatai da wuraren ziyara sai jahilai suka zaci cewa na binne a wurin suna anfanarwa ko cutarwa, kuma suna agazawa wanda ya nemi agajinsu, suna biyan buƙatar wanda ya fake da su, shi ya sa suke gabatar musu da

[1] -Ai kada a daga su.
[2] - Igathatul-lahfaan, (1/214 -215-217)

bakance da abubuwan yanka. Har aka wayi gari sun zama wasu gumaka da ake bautawa ba Allah ba- lallai Annabi SAW ya ce: ***"Ya Allah ka da ka sanya kabarina ya zama wani gunki da za a bautawa"***[1]. Bai yi wannan addu'a ba sai don wani abu irin wannan zai faru a wanin kabarinsa S.A.W, kuma hakika ya faru a garurun musulmai da yawa, amma kabarinsa dai Allah Ya kare shi albarkacin addu'arsa S.A.W. Ko da ya ke wasu abubuwa na saɓawa su kan faru a masallacinsa daga wasu jahilai ko 'yan damfara, saidai ba za su iya kai wa ga kabarinsa ba S.A.W, saboda kabarinsa yana cikin gidansa, ba a cikin masallaci ba, kuma an kewayeshi da katangu-kamar yadda babban malami Ibnul-Kayyim ya fada a *Nuniyyarsa:*

*Sai ubangijin talikai ya amsa addu'arsa* ** *Ya kewayeshi da katangu uku*

***

[1] - Malik ne ya ruwaito shi da Ahmad.

## FASALI NA HUDU: BAYANIN HUKUNCIN GIRMAMA GUMAKA DA MUTUM-MTUMIN TUNAWA DA WANI

**GUMAKA:** jam'in Gunki – shi ne hoto mai jiki (inuwa) bisa yanayin mutum ko dabba ko waninsu cikin abubuwa masu rai, Mutum-mutumi a asali: Fitaccen abu ko dutsen da mushirikai sun kasance suna yin yanka domin zagayowar tunawa da wani jagora ko wani babba ana yin hotonsu.

Annabi SAW ya tsawatar a kan yin hoton abubuwa masu rai, musamman ma yin hoton manya daga cikin mutane: kamar malamai da sarakuna da masu ibada da jagorori da shugabanni, ko dai hoton ya zama ta hanyar zanen hoto a kan wani allo ko takarda ko bango ko tufafi, ko kuma ta hanyar dauka da na'ura mai haske sananniya a wannan zamani. Ko ta hanyar kartawa da gina hoton bisa yanayin mutum-mutumi. [Annabi] S.A.W ya hana rataya hotuna a bango da makamantansu, da kuma girke mutum-mutumi, yana daga cikin yin hakan a kafa mutum-mutumi na tarihi, domin hakan hanya ce zuwa shirka. Hakika shirka ta farko da ta faru a duniya ta kasance ne a dalilin yin hoto da kafe hotuna. Hakan ya faru ne a cikin mutanen [Annabi] Nuhu an yi wasu salihai, yayin da suka mutu sai mutanensu suka yi bakin ciki sosai, sai Shaidan ya yi musu wahayin cewa ku kafa mutum-mutumi a majalisansu da suke zama, sai ku sanya musu sunayensu, sai suka yi hakan ba tare da sun bauta musu ba, har sai bayan wadannan sun halaka, an manta da karatu sai aka bauta musu[1]. Yayin da Allah Ya aiko AnnabinSa Nuhu – amincin Allah ya tabbata a gareshi - ya yi hani game da shirka da ta faru a dalilin wadannan hotuna da a ka kafa sai mutanensa suka ki karbar da'awarsa, suka kafe a kan bautar wadannan hotunan da aka kafa, wadanda daga baya suka koma gumaka: ***(Suka ce kada ku bar ababen bautarku, kada ku bar Waddu da Suwa'a, ko Yagusa da Ya'uƙa da Nasra)*** **[Nuhu: 23].** Wadannan sunayen wasu mazaje ne wadanda aka suranta hotunansu a bisa kamanninsu, domin tunawa da su da girmamasu.

Kalli yadda lamari ya koma a dalilin wadannan mutum-mutumi na tarihi wajen yin shirka da Allah da yin taurin kai ga manzanninSa. Abinda ya jawo halakar da su da Ɗufana da ƙinsu da Allah Ya yi da halittunSa, wannan abu ne wanda ya ke nuna hadarin hoto da girke mutum-mutumi. Saboda haka Annabi S.A.W ya la'anci masu yin hoto, ya bayar da labari cewa su ne mafi tsananin mutane shan azaba ranar alkiyma, ya yi umarni a shafe hotuna, ya bayar da labari cewa mala'iku ba sa shiga gidan ya ke da hoto a cikinsa, duka wannan saboda illolinsa da girman hadarinsa a al'umma da akidarta. Hakika farkon shirkar da ta faru a ban kasa ta kasance a dalilin kafe hotuna, kuma duk daya da kafe hotuna a majalisai da kafesu a filaye ko lambuna,

[1] -Bukhari ne ya ruwaito shi.

duk haramun ne a shari’ance saboda hanya ce zuwa shirka da lalacewar akida. Idan kafirai a yau sun kasance suna aikata wannan aiki saboda ba su da akida da suke kula da ita, to, bai halatta ga musulmai ba su kwaikwayesu, su yi tarayya da su a wannan aikin; saboda kulawa da akidarsu wadda ita ce tushen karfinsu da kwanciyar hankalinsu.

***

## FASALI NA BIYAR: BAYANIN HUKUNCIN IZGILI GA ADDINI DA WULAKANTA ALFARMARSA

Izgilanci ga Addini ridda ne daga Musulunci, kuma fita ne daga Addini gaba daya, Allah SWT Ya ce: ***(Ka ce: Yanzu da Allah ne da ayoyinSa da manzonSa ku ke izgilanci, kada ku ba da uzuri, kun riga kun kafirta bayan imaninku)*** **[ Al-Tauba: 65 – 66].**

Wannan aya tana nuni bisa cewa izgilanci da ayoyin Allah kafirci ne, kuma izgilanci da manzon [Allha] kafirci ne, kuma izgilanci da ayoyin Allah kafirci ne, duk wanda ya yi izgilanci da daya daga cikin wadannan al'amura, to, ya yi da dukkansu, abin da ya faru da wadannan munafikai shi ne cewa sun yi izgilanci ne ga Manzo da sahabbansa sai ayar ta sauka. Don haka izgilanci da wadannan abubuwa yana hade da juna, duk wadanda suke raina tauhidin Allah S.W.T suke girmama rokon waninSa cikin matattu, idan kuma aka umarcesu da Tauhidi aka hanasu shirka sai su raina hakan, kamar yadda Allah SWT Ya ce***: (Idan suka ganka ba sa daukarka face abin izgilanci, [sai su rika cewa): yanzu wannan ne Allah Ya aiko a matsayin manzo. Har ya kusa batar da mu daga abubuwan bautarmu ba don mun dage a kansu ba)*** **[Al-Furkan: 41 – 42].** Sai suka yi izgilanci ga Manzo S.A.W yayin da ya hanasu shirka. Mushirikai ba su gushe ba suna aibata Annabawa suna siffanta su da wauta da bata da hauka idan suka kirasu zuwa tauhidi saboda abin da ya ke cikin zuciyarsu na girmama shirka. Haka za mu ga duk wanda yake da kama da su idan ya ga wanda ya ke kira zuwa tauhidi sai ya yi masa izgilanci saboda shirkar da ya ke da ita, Allah SWT Ya ce: ***(Daga cikin mutane akwai wanda ya ke rikar wasu kishiyoyi koma bayan Allah, yana sonsu kamar son Allah)*** **[ Al-Bakarah: 165].**

Duk wanda ya so wani abin halitta kamar yadda ake son Allah, to, ya zama mushiriki, wajibi ne a banbance tsakanin soyayya saboda Allah da soyayya tare da Allah, wadannan da suka riki kaburbura gumaka za ka samu suna izgili da abin da ya ke Tauhidin Allah ne a ibadarSa, suna girmama abin da suka rikesu ba Allah ba a matsayin masu ceto, Dayansu zai rantse rantsuwa mai dulmiyarwa alhalin karya ya ke, amma ba zai iya karfin zuciyar rantsuwa da shehinsa ba a halin karya ba. Da yawa daga cikin kungiyoyi masu yawa za ka ga dayansu yana ganin neman agajin shehinsa ko dai a wajen kabarinsa ko wanin kabarin ta fi masa amfani a kan ya roki Allah a masallaci a lokacin karshen dare. Yana yin izgili ga wanda ya kaucewa darikarsa zuwa tauhidi, da yawansa suna rusa masallatai [ta hanyar wofintarwa] suna raya wuraren ziyara, wannan menene idan ba rainawarsu

ga Allah da ayoyinSa da manzonSa ba da kuma girmama shirka[1] . faruwar wannan yana da yawa a wajen masu bautar kabari a yau, Izgilanci nau'i biyu ne:

**NA FAKONSU:** Izgilanci ƙarara kamar wanda ayar ta sauka a kansa, shi ne fadinsu: Ba mu taba ganin irin wadannan makarantan namu ba, sarakan ciki, mafiya ƙarya a magana, ragwaye yayin haɗuwa da magauta. Ko dai maganganun masu izgili masu kama da wannan, kamar cewar waninsu: Wannan Addinin naku addini ne na biyar [bambarakwai], wani kuma ya ce: Addininku mara kan gado ne, wani kuma idan ya ga masu umarni da kyakkyawa da hani da mummuna sai ya ce: Ga 'yan Addini nan sun zo muku, [yana fadar wannan] a matsayin izgili garesu, da sauran irin wadannan abubuwan da ba za su lissafu ba sai an sha wahala sama da abin wadanda ayar ta sauka a kansu suka fada.

**NAU'I NA BIYU:** Wanda ba ƙarara ba, wannan kam kogi ne da ba shi da gaɓa – kamar yin alama da ido, da fito da harshe da taɓe baki. Da zunguri da hannu lokacin karatun littafin Allah ko sunnar Manzon Allah SAW, da lokacin umarni da kyakkyawan aiki, da hani daga mummuna[2]- duk a cikin irin wannan ne abin da wasunsu suke fada cewa: Lallai Musulunci bai dace da ƙarni na ashirin ba- kawai ya dace da ƙarnuka na na tsakiya [can baya], kuma [shi Musulunci ci baya ne, da koma baya, kuma akwai kaushi a cikinsa da dabbanci a uƙubobin haddi da ta'azir. Kuma ya tauyewa mace hakkokinta wajen halatta saki da ƙarin aure, da inda suke cewa: Yin hukunci da dokokin da aka ƙirƙira ya fi dacewa da mutane a kan hukunci da Musulunci. Kuma suna cewa game da wanda ya ke kira zuwa tauhidi ya ke inkarin bautar makabarta da kaburbura: Wannan dan zafin [Addini ne], ko [su ce] yana so ya kawo rarrabuwar kan musulmai, ko [su ce] Bawahabiye ne, ko [su ce] dan Mazhaba ta biyar ne, da abin da ya yi kama da wadannan maganganun wanda duk zagin Addini ne da masu shi, kuma izgili ne ga Akida ingantacciyya *wa la haula wa la ƙuwwta illa bil laah.* Yana daga cikin izgilinsu ga wanda ya yi riko da wata sunna daga cikin sunnonun Manzon Allah SAW, sai su ce: Addini ba a gashi ba ne, [suna fadar wannan ne] don izgili ga wanda ya cika gemu- da abin da ya yi kama da wadannan lafazai na rashin mutunci.

***

[1] - Majmu'ul Fatawa (15/48 – 49)

[2] - Majmu'atul tauhid al--najadiyya shafi na 409.

## FASALI NA SHIDA: YIN HUKUNCI DA WANIN ABIN DA ALLAH YA SAUKAR

Yana daga abin da imani da Allah S.W.T da bautarSa su ke hukuntarwa ƙanƙan da kai ga hukuncinSa, da yarda da shari'arSa, da komowa zuwa littafinSa da sunnar ManzonSa a lokacin saɓani a maganganu da asalai da husumomi da [lokacin saɓani] a kan jinane da dukiyoyi da sauran haƙƙoƙi. Haƙiƙa Allah Shi ne Gwanin hukunci, zuwa gareShi hukunci ya ke , ya zama wajibi a kan mahukuntasu yi hukunci da abin da Allah Ya saukar. Yana wajaba a kan talakawa [wadanda ake shugabanta] su riƙa kai ƙara zuwa abin da Allah Ya saukar a littafinSa da sunnar ManzonSa, Allah S.W.T Ya fada game haƙƙin shugabanni***: (Haƙiƙa Allah Yana umartarku ku isar da amanoni zuwa ma'abotansu, idan za ku yi hukunci tsakanin mutane, to, ku yi shi da adalci)*** **[Al-Nisa'i: 58].** Ya fada game da haƙƙin talakawa: ***(Ya wadanda suka yi imani ku yi biyayya ga Allah ku yi biyayya ga Manzo da majibinta lamari daga cikinku, idan kun yi ja-in-ja a wani abu, to, ku mayar da shi zuwa ga Allah da Manzo in dai kun kasanace kuna yin imani da Allah da ranar lahira, wannan shi ne mafi alheri, mafi kyawun fassara)*** **[Al-Nisa'i: 59].** Sanna ya yi bayanin cewa imani da kuma kai ƙara zuwa wanin Allah ba sa haduwa, sai Allah S.W.T Ya ce: ***(Ba ni labarin wadanda su ke riya cewa sun yi imani da abin da aka saukar maka, da abin da aka saukar kafinka, suna son kai ƙara zuwa Ɗagutu, alhalin an umarcesu da su kafirce masa, Shaidan yana so ya batar da su bata mai nisa)*** **[al-Nisa'i: 60]** har zuwa fadinSa S.W.T: ***(Na rantse da Ubangijinka ba za su yi imani ba [imaninsu ba zai cika ba], har sai sun riƙa kawo ƙara wajenka game da sabanin da ya faru a tsakaninsu, sannan kada su samu wani ƙunci cikin abin da ka yi hukunci, su sallama [maka] iya sallamawa)*** **[Al-Nisa'i: 65].**

Sai Allah S.W.T Ya kore imani – korewa mai karfi da rantsuwa- daga wadanda ba sa kai kararsu wajen Manzon Allah S.A.W ba sa yarda ba sa sallama masa – kamar yadda ya yi hukuncin kafircewar jagororin da ba sa hukunci da abin da Allah Ya saukar [ya yi hukunci] da zaluncinsu da fasiƙancinsu, Allah S.W.T Ya ce: ***(Wadanda ba su yi hukunci da abin da Allah Ya saukar ba, wadannan su ne kafirai)*** **[Al-Ma'idah: 44].**

***(Wadanda ba su yi hukunci da abin da Allah Ya saukar ba, wadannan su ne kafirai azzalumai)*** **[Al-Ma'idah: 45].** ***( Wadanda ba su yi hukunci da abin da Allah Ya saukar ba, wadannan su ne fasiƙai)*** **[al-Ma'idah: 47].**

Babu makawa wajen aiki da abin da Allah Ya saukar da yin hukunci zuwa gareshi cikin dukkan abubuwan ja-in-ja na maganganun *Ijtihadi* tsakanin Malamai, [ya zama] ba za a karba ba sai abin da Alkur'ani da sunna suka yi nuni a kai, ba tare da ƙabilancin Mazhaba ba, ko tarewa wajen wani jagoran [Mazhaba] ba. [hakan ya kasance] Wajen ɗaukaka ƙara, da rigingimu a kan sauran haƙƙoƙi ba *Ahwalus Shakhsiyya* ba kawai (zamantakewar aure da rabon gado). Kamar yadda hakan ya ke faruwa a wasu kasashe da suke dangantuwa zuwa Musulunci – hakika musulunci duka ne ba gutsire, Allah SWT Ya ce: ***(Ya wadanda su ka yi imani ku shiga musulunci duka)*** **[Al-Baqarah: 208].** Allah S.W.T Ya ce: ***(Shin za ku yi imani da wani bangare na littafin, ku kafircewa wani?)*** **[Al-Baqarah: 85].**

Haka nan yana wajaba a kan mabiya Mazhabobi su rika mayar da maganganun jagororinsu zuwa littafin Allah da sunna, abin da ya dace su sai suyi riƙo da shi , abin da ya saɓa musu sai su mayar da shi ba tare da ƙabilancin Mazhaba ba ko bangarenci ba, musamman dai a batutuwan Akida, hakika jagoroin - Allah Ya yi musu rahama- sun yi wasiyya a kan haka – wannan ce Mazhabarsu baki daya- wanda duk ya saɓawa haka, to, ba su ya ke bi ba, ko da ya dangantu zuwa garesu, yana cikin wadanda Allah Ya ce game da su: ***(Sun riki malamansu da masu ibadarsu abubuwan bauta ba Allah ba da Masihu dan Maryam)*** **[Al-Taubah: 31].** Ayar ba ta kebanta da Nasara ba ne kawai, sai dai ta shafi duk wanda ya yi irin aikinsu (Duk wanda ya saɓawa abin da Allah da manzonSa S.A.W suka yi umarni ya yi hukunci tsakanin mutane ba da abin da Allah Ya saukar ba, ko ya nemi haka don bin abin ransa ya ke so ya ga dama, to, ya cire rigar Musulunci da imani daga wuyansa, ko da yana riya cewa shi mumini ne, Hakika Allah Ya yi inkari ga wanda ya yi nufin hakan ya karyatasu cikin abin da suke riyawarsu imani. Saboda abin da fadinsa (suna riyawa) ya kunsana kore imanin nasu, hakika (suna riyawa) kadai ana fadarta ne a mafi yawanci ga wanda ya yi da'awar abin da karya ya ke a cikinsa domin ya saɓawa abin da zai tabbatar

[da maganarsa], kuma ya aikata abin da zai warwareta, abin da ya ke tabbatar da wannan shi ne fadin Allah S.W.T: ***(Alhalin an umarcesu su kafirce masa)*** **[Al-Nisa'i: 60].** Saboda kafircewa Dagutu rukuni ne a tauhidi, kamar yadda ya zo a cikin ayar Bakarah[1], idan wannan rukunin bai samu ba, to, bai zama mai tauhidi ba, Tauhidi shi ne tushen imanin da dukkan ayyuka suke gyaruwa da shi, kuma suke lalacewa da rashinsa, kamar yadda hakan ya ke a bayyane a cikin fadinSa SWT: ***(Wanda ya kafircewa Dagutu ya yi imani da Allah, to, hakika ya yi riko da igiya mai kwari)*** **[al-Baqarah: 256].** Hakan ya kasance ne saboda kai kara [da neman hukunci] wajen Dagutu imani da shi ne).[2]

Kore imani daga wanda bai yi hukunci da abin da Allah Ya saukar ba, yana nunu a kan cewa yin hukunci da shari'ar Allah imani ne, Akida ne kuma bauta ne ga Allah, da ya wajaba musulmi ya yi Addini da shi, ba wai a na yin aiki da dokar Allah ba ne domin kawai ita ce ta fi maslaha ba, domin wasu mutane suna mai da hanakali a wannan bangaren kawai, suna mantawa da bangare na farko – Allah SWT Ya aibatawa wanda yake aiki da hukuncin Allah saboda maslahar kansa ba tare da yin bauta ga Allah SWT ba, Allah SWT Ya ce: [ Idan aka kirasu zuwa Allah da ManzonSa don ya yi hukunci a tsakaninsu, sai ka ga wasu daga cikinsu suna juya baya. Idan kuwa suna da gaskiya sai su zo suna kaskantar da kai ) [al-Nur: 48 - 49]. Su ba sa damuwa sai da abin da ya zama son ransu, abin da ya sabawa son ransu kuwa sai su bijire masa, saboda ba sa yin bautar Allah ta hanyar mikawa ManzonSa SAW hukunci.

## HUKUNCIN WANDA YA YI HUKUNCI DA WANIN ABIN DA ALLAH YA SAUKAR:

Allah S.W.T Ya ce: ***(Wanda bai yi hukunci da abin da Allah Ya saukar ba, wadannan su ne kafirai)*** **[Al-Ma'idah: 44].** A cikin wannan aya mai girma akwai [bayanin] cewa hukunci da wanin abin da Allah ya saukar kafirci ne, wannan kafircin wani lokacin yana zama kafirci mafi girma da zai dauke [mutum] daga Musulumci, wani lokacin kuma yana zama kafirci mafi

---

[1] - Yana nufin fadin Allah S.W.T: ***(wanda ya kafircewa Dagutu ya yi imani da Allah, to, hakika ya yi riko da igiya mai kwari)***

[2] - Fathul majid, shafi na 467 – 468.

kankanta ba ya fitarwa daga musulunci, wannan yana kasancewa ne gwargwadon yanayin shi mai yin hukuncin, idan ya kudurce cewa yin hukunci da abin da Allah Ya saukar ba wajibi ba ne, kuma yana da zabi a ciki, ko kuma ya raina hukuncin Allah, ya kudirce cewa waninsa cikin dokokin da tsare-tsaren da aka kirkira sun fi shi kyau, kuma bai dace da wannan zamanin ba, ko kuma ya yi nufin neman yardar kafirai da munafikai ta hanyar yin hukunci da wanin abinda Allah Ya saukar, to, wannan kafirci ne mafi girma, idan kuma ya kudirce wajabcin yin hukunci da abinda Allah Ya saukar, kuma ya sanshi a wannan abin da ya farun , amma ya kauce masa tare da ganin girmansa, to, wannan mai saɓo ne, kuma ana kiransa kafiri kafirci mafi kankanta. Idan kuma ya jahilci hukuncin Allah a cikinsa tare da yin iya kokarinsa da duk damar da ya ke da ita wajen sanin hukuncin sai kuma ya yi, to, wannan mai kuskure ne yana da lada bisa *ijtihadinsa* kuskure kuskurensa kuma an yafe masa[1]. Wannan game da batu kebantacce kenan. Amma hukunci a batutuwa gamammu wannan yana da bambanci. *Sheikhul Islam Ibnu Taimiyah ya ce:* Mai hukunci [alkali] idan ya kasance mai Addini sai dai ya yi hukunci ba da ilimi ba, to, ya zama ɗan wuta, idan kuma yana da ilimi amma sai ya yi hukunci saɓanin gaskiyar da ya sani, to, ya zama ɗan wuta, idan kuwa ya yi hukunci babu adalci babu ilimi, shi ya fi dacewa ma ya zama ɗan wuta, duka wannan idan ya kasance a batun wani mutum guda daya ne, amma idan ya yi hukunci hukunci gamamme cikin Addinin musulmai, ya mayar da gaskiya ta koma karya, karya ta koma gaskiya, sunna ta koma bidi'a, bidi'a ta koma sunna, mummunan aiki ya koma kyakkyawa, kyakkyawa ya koma mummuna, ya hana abin da Allah da ManzonSa suka yi umarni, ya yi umarni da abin da abin da Allah da ManzonSa suka hana, to, wannan wani kalar ne na da ban wanda Ubangijin talikai, abin bautar manzanni, mamallakin ranar sakamako, wanda yabo na sa ne a farko da karshe zai yi hukunci a kansa: ***(Mulki na sa ne, zuwa gareShi ne za ku koma)*** **[Al-Qasas: 88].** ***(Shi ne Ya aiko ManzonSa da shiriya da Addinin gaskiya, don ya yi rinjaye a kan addinai duka, Allah Ya isa zama shaida)*** **[al-Fathi: 28].**

[1] - Sharhul dahawiyyah, shafi na ( 363 – 364).

Kuma ya ce: Babu kokonto cewa duk wanda bai kudirce wajabcin hukunci da abin da Allah Ya saukar ga ManzonSa ba, shi kafiri ne, Duk wanda ya ke ganin halaccin a yi hukunci tsakanin mutane da abin da ya ke ganin adalci ne ba tare da an bi abin da Allah Ya saukar ba, to, shi kafiri ne, domin babu wata al'umma face tana umarni da yin hukunci da adalci, kuma adalcin zai iya zama abin da manyansu suke gani, kai da yawa daga cikin masu dangantuwa zuwa Musulunci suna hukunci ne da al'adunsu wadanda Allah bai saukar ba kamar gargajiyar kauye (ai al'adun wadanda suka gabacesu), sun kasance sarakuna ne da ake yi wa biyayya, suna wannan [abu] shi ne wanda ya dace a yi hukunci da shi ba Al-kur'ani da Sunna ba, wannan kuwa shi ne kafirci. Hakika da yawan mutane sun musulunta sai dai ba sa hukunci sai da al'adun da suke gudana wadanda ake yi wa wasu biyayya a kai. Irin wadannan idan sun san ba ya halatta su yi hukunci sai da abin da Allah Ya saukar, amma ba su rike hakan ba, kawai sunna ganin halaccin yin hukunci da wanin abin da Allah Ya saukar, to, sun zama kafirai[1]. [maganar] ta ƙare. Sheikh Muhammad bn Ibrahim ya ce: Amma wanda aka ce kafirci ne: to, kafirci ne [karami] wanda bai kai kafirci [babba] ba idan ya nemi hukuncin wanin Allah tare da kudirce cewa shi mai saɓo ne, kuma hukuncin Allah shi ne gaskiya, irin wannan shi ne wanda zai faru da shi sau daya ko makamancinsa, amma sanya wasu dokoki a jere da rankwafa musu wannan kafirci ne, ko da sun ce mun yi kuskure hukuncin Allah shi ne mafi adalci, wannan kafirci ne mai cirewa daga musulunci.[2] [Malamin] -Allah Ya gafarta masa- sai ya bambanta tsakanin hukunci na wani yanki wanda ba ya maimaituwa, da wanda ya ke gamamme wanda ya ke zama makoma [manazarta] a dukkan hukunce-hukunce ko yawancinsu, kuma ya tabbatar da cewa wannan kafirci ne mai cirewa daga Musulunci sake-ba-kaidi, [ya fadi] haka ne saboda wanda ya ture shari'ar musulunci gefe, ya sanya dokoki kirkirarru musanyarsu wannan dalili ne cewa yana ganin dokokin sun fi kyau sun fi shari'ar dacewa, wannan kuwa babu shakka kafirci ne mafi girma yana fitarwa daga Musulunci, kuma yana warware Tauhidi.

---

[1] - Minhajus Sunnah

[2] - Fatawa Sheikh Muhammad bn Ibrahim Al-Sheikh (12/280)

## FASALI NA BAKWAI: DA'AWAR HAƘƘIN YIN DOKOKI DA HALATTAWA DA HARAMTAWA

Yin dokar hukunce-hukuncen da bayi za su tafi a kai a ibadunsu da mu'amalolinsu da sauran sha'anoninsu, wadanda suke rabe jayayya tsakaninsu, su ke kawo karshen rigingimu hakkin Allah ne, Ubangijin mutane, Mahaliccin halitta: ***(Ku saurara! Halittta da al'amari na sa ne, albarkatun Allah sun yawaita, Ubangijin talikai)*** **[al-A'araaf: 54]**, shi ne ya san abin da zai gyara bayinSa, sai Ya shar'anta musu shi. A hukuncin RububiyyarSa ne garesu ya ke shari'anta musu [dokoki], a hukuncin bautarsu gareshi ne su ke karbar hukunce-hukuncenSa- a cikin yin hakan kuma maslahar kansu take komawa, Allah S.W.T Ya ce: ***(Idan kun yi sabani a wani abu, sai ku mayar da shi zuwa ga Allah da Manzo in dai kun kasance kun yi imani da Allah da ranar lahira, hakan shi ya fi alheri, kuma shi ne mafi kyawun fassara)*** **[Al-Nisa'i: 59].** Allah S.W.T Ya ce: ***(Duk abin da ku ka samu wani sabani a cikinsa, to, hukuncinsa yana ga Allah, Wannan dai shi ne Allah Ubangijina)*** **[al-Shura: 10].** Allah S.W.T Ya yi inkarin bayi su rika daukar wani mai yin doka ba Shi ba, sai Ya ce: ***(Ko suna da wasu abokan tarayya da suka shar'anta musu wani abu a Addini irin abin da allah bai yi izini a kansa ba)*** **[Al-Shura: 21].**

Duk wanda ya karbi wata doka ba dokar Allah ba, to, ya yi wa Allah S.W.T shirka- duk abin da Allah da ManzonSa ba su shara'antashi ba na ibadu, to, ya zama bidi'a, dukkan bidi'a bata ce- [Manzon Allah] S.A.W ya ce: ***"Wanda ya farar da wani abu acikin addini wanda ba ya cikinsa, to, [wannan abin] abin mayarwa ne"***|[1]. A wata riwayar: ***"Wanda ya aikata wani aiki wanda babu umarnimmu a ciki, to, abin mayarwa ne"***[2], duk abin da Allah da ManzonSa bai shar'anta shi ba A siyasa da hukunci tsakanin mutane, to, hukuncin dagutu ne, kuma hukuncin Jahiliyya ne: ***(Shin hukuncin Jahiliyya su ke nema! Wa ya fi Allah kyawun hukunci ga mutane masu yakini)*** **[Al-Ma'idah: 50]** haka nan halattawa da haramtawa hakkin Allah ne S.W.T, ba ya halatta ga wani ya yi tarayyya da Shi a cikinsa. Allah SWT Ya ce: ***(Kada ku ci daga abin da ba a ambaci sunan***

---

[1] - Hadisin Bukhari da Muslim ne suka rawaito shi.
[2] - Muslim ne ya rawaito shi.

***Allah a kai ba, hakika shi din fasikanci ne, hakika shaidanu suna yi wa masoyansu wahayi; domin su rika jayayya da ku, idan ku ka yi musu da'a, to, lallai ku [kun zama] mushirikai)*** **[al-An'am: 121].**

Sai Allah S.W.T Ya sanya da'ar shaidanu da masoyansu wajen halatta abin da Allah Ya haramta shirka ne da Shi SWT, haka nan wanda ya yi da'a ga malamai da sarakuna wajen haramta abin da Allah Ya halatta, ko halatta abinda Allah Ya haramta, to, ya rikesu ababen bauta ba Allah ba, saboda fadin Allah S.W.T: ***(Sun riƙi malamansu da masu ibadarsu da Masihu dan Maryam a matsayin ababen bauta ba Allah ba, ba a umarcesu ba sai don su bautawa abin bauta guda daya, babu abin bautawa da gaskiya sai Shi, tsarki ya tabbata a gareShi game da abin da suke yin shirka da Shi )*** **[al-Tauba: 31].** [ya zo] a wajen Tirmiziy da wanisa cewa Annabi S.A.W ya karanta wannan aya ga Adiyy dan Hatim - Allah Ya yarda da shi- sai ya ce: ***"Ya Manzon Allah ba ma bauta musu, sai ya ce: Shin ba sa halatta muku abin da Allah Ya haramta, sai ku dauka halal ne, [shin ba sa] haramta muku abin da Allah Ya halatta sai ku dauka haram ne? Sai ya ce: Eh, sai Annabi S.A.W ya ce: "Wannan ce bautarsu"***[1]. Sai yi musu da'a wajen halattawa da haramtawa da ba Allah ne Ya yi ba bauta ce a garesu kuma shirka ce sannan kuma shirka ce mafi girma da take cin karo da Tauhidin da shi ne abin da shida wa babu abin bautawa da gaskiya sai Allah[2] ta ke nunawa, Hakika yana daga cikin abin da ta ke nunawa cewar halattawa da haramtawa hakkin Allah ne S.W.T- idan ya kasance wanda ya yi da'a ga malamai da masu ibada wajen halattawa da haramtawar da saɓawa shari'ar Allah tare da cewa su ne mafiya kusanci da zuwa ilimi da Addini, kuma zai iya yiwuwa kuskuren nasu a *ijtihadi* ne wanda ba su da ce da gaskiya ba ne a cikinsa kuma za a ba su lada a kansa, to, yaya kuma wanda ya ke biyayya ga dokoki kirkirarrau wadanda kafirai ne da masu musun samuwar Allah sauka yi su- da aka kawosu zuwa garuruwan musulmai ake hukunci da su a tsakaininsu – *fa lahaula wa la kuwwata illa bil laah.*

---

[1] -Timiziy ne ya rawaito shi da Ibn Jarir da waninsu.

[2] -fathul majid shafi na 107.

Hakika wannan ya riki kafirai a matsayin ababen bauta ba Allah ba, suna yi masa dokokin da ya ke hukunci da su, suna halatta masa haram , suna yin hukunci tsakanin mutane.

***

## FASALI NA TAKWAS: HUKUNCIN DANGANTUWA ZUWA ƘUNGIYOYI NA MASU MUSUN SAMUWAR ALLAH DA ƘUNGIYOYIN JAHILIYYA

1- Dangantuwa Zuwa Ƙungiyoyi Na Masu Musun Samuwar Allah: kamar Gurguzu da Almaniyanci [Boko A ƙida] da Jari-hujja da sauran ƙungiyoyin kafirci fita ne daga Musulunci, idan wanda ya ke dangantuwa izuwa wadannan kungiyoyi ya yi da'awar Musulunci, to, munafunci ne babba, Hakika munafikai suna dangantuwa izuwa musulunci a zahiri, amma suna tare da munafikai a boye- kamar yadda Allah SWT Ya fada game da su: ***(Idan suka hadu da wadanda suka yi imani sai su ce mun yi imani, idan kuma suka kebe da shaidanunsu sai su ce muna tare da ku, kawai izgili mu ke [musu])*** **[Albaqara: 14].** Allah S.W.T Ya ce: ***(Wadanda suke jiran wani abu ya sameku, idan kun samu wani budi daga Allah, sai su ce ba muna tare da ku ba, idan kuma kafirai ne suka samu wani rabo sai su ce: Ba mun tsareku ba, kuma mun ba ku kariya daga muminai)*** **[al-Nisa'i: 141].**

Wadannan munafukan mayaudara; kowannensu yana da ***fuska biyu:*** Fuskar da ya ke haduwa da mummunai da ita, da fuskar da ya ke komawa cikin 'yan uwansa *Mulhidai* [masu musun samuwar Allah], kuma yana da ***harshe biyu:*** Da zahirinsa ne musulmai suke karbarsa, dayan kuma yana fassara sirrinsa da ya ke boye ***(Idan suka hadu da wadanda suka yi imani sai su ce mun yi imani, idan kuma suka kebe da shaidanunsu sai su ce muna tare da ku, kawai izgili mu ke [musu])*** **[al-Baqara: 14]**. Hakika sun bijirewa Al-kur'ani da sunnah saboda izgili ga masu [riko] da su da raini garesu, sun ki yin biyayya ga hukuncin wahayi biyu [Al-kur'ani da sunnah], suna masu fariya da abin da suke da shi na ililmin da tara shi ba zai amfanar da wani abu ba sai sharri da girman kai, ***sai ka gansu a koda yaushe suna ta izgili ga masu riko da zahirin wahayi: (Allah Yana mayar musu da sakamakon izgilinsu, kuma yana barinsu a cikin dagawarsu suna fagauniya)*** **[al-Baqara:15]** hakika Allah Ya yi umarnin dangantuwa zuwa muminai: ***(Ya ku wadanda suka yi imani ku kiyayi Allah , kuma ku kasance tare da masu gaskiya)*** **[Al-Tauba: 119].**

Wadannan kungiyoyina *Ilhadi* [musanta samuwar Allah] fada su ke yi da junansu, saboda an kafasu ne a kan barna, Gurguzu suna musun samuwar Mahalicci [Allah] SWT, suna yaki da Addinai da aka saukar daga sama, wanda ya yarda a hankalinsa ya rayu ba tare da wata Akida ba, yana inkarin abubuwa na zahiri masu tabbas, to, ya zama tamkar ya yi watsi da hankalinsa ne, *Almaniyanci* [Akidar boko da cewar babu ruwan Addini da harkokin rayuwa] suna inkarin addinai , suna dogara a kan abubuwanda da ido zai iya gani hannu ya taba, irin abubuwan da ba su da mai saitasu, ba su da wata manufa a wannan rayuwar, sai tamkar rayuwar dabbobi? Shi kuma tsarin Jari Hujja damuwarsu kawai ita ce a tara kudi ta kowace hanya, babu wani kaidi na halal ko haram, babu jin kai, babu tausayi ga talakawa da miskinai, kuma kashin bayan tattalin arzikinta [an dora shi], kan riba wadda ita kuma faɗa ce da Allah da ManzonSa, wanda hakan rushewar kasashe ne da daidaikun mutane- Da shan jinin al'uma da talakawa. Wane mai hankain ne – ballantana wanda ya ke da kwayar imani a zuciyarsa- da zai yarda ya rayu a wadannan kungiyoyi babu hankali, babu Addini, babu wata manufa ingantacciya a rayuwarsa da ya ke tunkara, ya ke gwagwarmaya saboda ita, kadai wadannan kungiyoyi sun yaki garuruwan Musulmai ne a lokacin da yawancinsu suka bar [koyarwar] Addini ingantacce, suka taso a kan tozarci, suka zama bi ta zai zai.

**1-** Dangantuwa zuwa kungiyoyi na Jahiliyya da 'Yan kasancin kabilanci shi ma din kafurci ne, kuma fita ne daga Musulunci, saboda musulunci ba ya goyon bayan kabilanci da gadara ta *Jahiliyya*, Allah SWT Yana cewa: ***(Ya ku mutane hakika mun halicceku daga namiji da mace, mun sanya ku al'umatai da kabilu don ku san juna, lallai mafi daraja a cikinku shi ne mafi taqawarku)*** **[Al-Hujurat: 13].** Annabi S.A.W yana cewa: ***"Ba ya cikimmu; wanda ya ke kira zuwa kabilanci, baya cikimmu wanda ya yi yaki saboda kabilanci, ba ya cikimmu wanda ya ke fushi saboda kabilanci"***[1]. ***[Annabi] S.A.W ya ce: Hakika Allah Ya tafiyar muku da gadara ta Jahiliyya, da fariyarta da iyaye, kawai [mutum] mumini ne mai taqawa, ko fajiri***

1 - Muslim ne ya rawaito shi.

***shaqiyyi, mutane 'Yan Adam ne, [Annabi] Adam [an halicce shi] daga kasa, babu fifikon balarabe a kan bobayi sai da taqawa"***[1].

Wadannan kungiyoyi suna raba kan musulmai, Allah kuma Ya yi umarnin hadin kai, da taimakon juna bisa nagarta da taqawa, Ya hana rarrabuwada sabani- Allah S.W.T Ya ce: ***(Ku yi riko da igiyar Allah gaba daya, kada ku rarrabu, ku tuna ni'imar Allah a gareku lokacin da ku ka kasance makiya juna, sai Ya hada tsakanin zukatanku, sai ku ka wayi gari a matsayin 'yan uwa)*** **[Al-Imran: 103].** Hakika Allah S.W.T Yana son mu kasance kungiya daya, wadanda su ne kungiyar Allah masu rabauta (sai dai duniyar Musulunci bayan Turawa sun yakesu a siyasance da wayewa sun wayi gari suna rankwafawa [ya ba da kai bori ya hau ga] irin wadannan kabilanci na zubar da jini, da wariyar jinsi da 'yan kasanci, kuma ya yarda da ita a matsayi wani batu da ilimi na hakika da aka tabbatar, kuma abu ne mai faruwa wanda babu makawa game da shi, Kuma an wayi gari al'umarsa suna tururuwa ta ban-mamaki wajen raya wadannan abubuwa na kabilancin da Musulunci ya riga ya matar da su [ya kawo karshensu], da yin yekuwa a kansu da raya alamominsu, da alfahari da lokacinsu da ya gabaci na Musulunci, wanda shi ne Musulunci ya dage wajen ambatonsa da Jahiliyya. Hakika Allah Ya yi wa Musulmai baiwar fita daga su [watsi da su], kuma ya kwadaitar da su a kan godewa wannan ni'imar.

A al'adance a wajen mummuni ba zai rika tuno wata Jahiliyya da lokacinta ya riga ya zama na da can, ko ya kusa zama sai da ta hanyar ƙi da ƙyama da yamutse fuska da tashin tsigar jiki. Shin dan kurkuku da aka saki zai tuna wani abu na kamashi da aka yi, da azabtar da shi, da wulakantashi in ban da ƙangin [wahalar] da tashin tsigar jiki. Shin wanda ya warke daga jinya mai tsananin da ya kusa mutuwa a kanta zai tuna da kwanakin jinyar tasa ba tare da ransa ya shiga damuwa ba, launinsa [kamanninsa] sun sauya ba.[2] Abin da ya wajaba shi ne a sani cewa wadannan kungiyoyi azaba ne Allah Ya aiko da su a kan wanda ya bijirewa shari'arSa, ya ke inkari ga

---

1 - Tirmiziy da waninsa ne suka rawaito shi.

2 - Daga Risala: (Riddar da Abu bakr ba shi da hannu a kanta) ta Abul Hasan al-Nadawiy.

AddininSa, kamar yadda Allah SWT ya ce: ***(Ka ce Shi ne mai ikon Ya aiko muku da azaba daga samanku, ko ta kasan kafafunku, ko ya mayar da ku kungiyoyi, sashinku ya dandanawa sashi azaba)*** **[Al-An'am: 65].** [Annabi] S.A.W ya ce: ***"Matukar jagororinsu ba su yi hukunci da littafin Allah ba, to, sai Allah Ya sanya fushinsu a tsakaninsu"***[1]. Hakika kabilanci a kan kungiyoyi yana jawo kin gaskiyar da ta ke tare da wasu, kamar yanayin Yahudawan da Allah Ya fada game da su cewa***: (Idan aka ce da su ku yi imani da abin da Allah Ya saukar sai su ce mun yi imani da abun da aka saukar mana, suna kafircewa abin da ba shi ba, alhali shi din gaskiya ne, mai gasgata abin da ya ke tare da su)*** **[ al-Baqarah: 91],** kamar yanayin 'yan Jahiliyya wadanda suka ki gaskiyar da Manzo ya zo musu da ita don kabilancin riko da abin da iyayensu suke a kai: ***(Idan aka ce da su ku bi abin da Allah Ya saukar, sai su ce, a'a, za mu bi abin da muka samu iyayemmu a kai)*** **[Al-baqarah: 170].** Ma'abota wadannan kungiyoyi suna so su sanyasu su zama musanyar Musuluncin da Allah Ya yi wa mutane baiwa da shi.

***

1 - Daga wani Hadisi da Ibn Majah ya ruwaito.

## FASALI NA TARA: YI WA RAYUWA KALLON DUNIYANCI DA ƁARNAR DAKE CIKIN IRIN WANNAN KALLON

Akwai kallo kala biyu da ake yi wa rayuwa, kallon duniyanci ga rayuwa, da kuma kallo ingantacce, kowane kallo yana da na sa tasirin:

**A. Kallon duniyanci ga rayuwa – (ma'anarsa):**

Shi ne ya zama tunanin mutum ya takaitu ga samun abubuwan jin dadinsa na nan magaggauciya [duniya], ya zama duk aikinsa ya takaitu a wannan fagen, tunaninsa ba ya shallake abin da zai je ya zo bayan nan, ba ya aiki domin haka, bai damu da wannan sha'anin ba, bai san cewa Allah Ya sanya wannan duniya don ta zama gona ta gidan lahira ba, don haka ya sanya duniya ta zama gidan aiki, Ya sanya lahira ta zama gidan sakamako, wanda duk ya shagaltar da duniyarsa da aiki nagari, to, zai ci ribar gidajen biyu, wanda kuma ya wulakantar da duniyarsa, to, lahirarsa ma ta wulakanta: ***(Ya yi asarar duniya da lahira, wannan ita ce asara bayyananniya)*** **[al-Hajj: 11].** Allah bai halicci wannan duniya don wasa ba, a'a Ya halicceta ne saboda wata hikima mai girma, Allah S.W.T Ya ce: ***(Hakika mun sanya abin da ya ke bayan kasa don ya zama ado a gareta, domin mu gwadaku wane ne zai fi kyawun aiki)*** **[al-Kahfi: 7],** Allah S.W.T Ya samar a wannan rayuwar abubuwa na jin dadin magaggauciya [duniya], da ado na zahiri, ta bangaren dukiyoyi da 'ya'ya da matsayi da sarauta da sauran abubuwan more rayuwa irin abin da ba wanda ya san iyakarsu sai Allah.

Daga cikin mutane –wannan shi ya fi yawa- akwai wanda ya takaita tunaninsa a kan zahirinta da kuma abubuwan jan hankali [a cikinta], ya ji dadinsa da abin, [amma] bai yi la'akari da sirrinta ba, kawai sai ya mayar da hankali game da nemanta da Tarawa Da morewa da ita ya manata da yin aiki domin abin da zai biyo bayanta. Bari [wannan zance] har ma ya yi inkarin wata rayuwa ba wannan ba, kamar yadda Allah S.W.T Ya ce: ***(Saka ce ba komai bane face rayuwarmu ta duniya, kuma mu ba za a tashemu ba)*** **[al-An'am: 29].** Hakika Allah S.W.T Ya yi narko game da yi wa rayuwa irin wannan kallon, Sai Allah S.W.T Ya ce: ***(Hakika wadanda ba sa fatan haduwa da mu, kuma suka yarda da rayuwar duniya, suka nutsu da ita, da***

***wadanda suka zama gafalallu game da ayoyimmu. Wadannan makomarsu ita ce wuta, sakamakon abin da suke aikatawa)*** **[Yunus: 7 – 8].** Allah S.W.T Ya ce: ***(Wanda ya ke rayuwar duniya da adonta za mu cika musu ayyukansu, ba za a tauye musu komai ba. wadannan su ne wadanda a lahira ba su da komai sai wuta, abin da suka aikata ya rushe, kuma abin da suke aikatawa ya ɓaci)*** **[Hud: 15 – 16].**

Wannan narkon ya kunshi ma'abota [yi wa rayuwa] wannan kallon, duk daya ne shin sun kasance masu yin aikin lahira amma suna nufin duniya, kamar munafikai da masu yin aikinsu don a gani [riya], ko kuma sun kasance daga cikin kafirai wadanda ba sa imani da tshi [bayan mutuwa], ko hisabi, kamar halin 'yan *Jahiliyya* da kungiyoyi masu rusa [Akida] kamar Jari-hujja da gurguzu da boko-akida da masu musun samuwar Allah, duk wadannan ba su san kimar rayuwa ba, kallonsu [nazarinsu] ba ya wuce irin kallon da dabbobi suke yi ba, kai! Sun ma fi [dabbobi] ɓacewa; saboda sun yi watsi da hankulansu, sun hole karfinsu da lokacinsu cikin abin da ba zai dawwama ba saboda su, su ma ba za su dawwama ba saboda shi ba, ba su yi aiki saboda makomarsu da take jiransu ba, wadda ba su da makawa game da ita.

Dabbobi ba su da wata makoma da take jiransu, kuma ba su da hankali da suke tunani da shi sabanin wadannan, saboda wannan Allah SWT Ya ce: ***(Shin ko kana zaton cewa yawancinsu suna ji ko suna hankalta, su din ba komai ba ne face kamar dabbobi, kai! Ai sun ma fi su bacewar hanya)*** **[Al-Furqan: 44]**

Hakika Allah Ya siffanta ma'abota wannan kallo [nazari] da rashin ilimi, sai Allah S.W.T Ya ce: ***(Sai dai yawancin mutane ba su da sani, sun san zahirin rayuwar duniya, amma game da lahira su gafalallu ne)*** **[Al-Rum: 6 -7].**

Su din ko da sun kasance ma'abota kwarewa a kere-kere da sana'o'i, to, jahilai ne ba su cancanci a siffantasu da ilimi ba, saboda iliminsu bai tsallake zahirin rayuwar duniya ba, wannan kuwa ilimi ne tauyayye mai shi bai cancanci a ba shi wannan siffa mai daraja ba, har [da su] Malamai, kadai ana fadin wannan ga ma'abota sanin Allah da tsoronSa ne, kamar yadda

Allah S.W.T Ya ce: ***(Kadai masu tsoron Allah su ne malamai)*** **[Fadir: 28].** Yana daga cikin yi wa rayuwa kallon duniyanci abin da ya ambata a kissar Ƙaruna, da abin da Ya ba shi na taskoki: ***(Sai ya fitowa mutanensa cikin adonsa, sai wadanda suke son rayuwar duniya suka ce: Ina ma muna da irin abin da aka bai wa Ƙaruna, lallai shi kam ma'abocin babban rabo ne)*** **[Al-Ƙasas: 79].** Sai suka yi fatan irinsa, suka ci burin samun irinsa, suka siffantashi da babban rabo duba da kallon duniyancinsu [da suke yi wa rayuwar duniya], wannan kamar yadda yanayin ya ke a yanzu a Ƙasashen kafirai da abin da suke da shi na cigaban sana'o'i da tattalin arziki, hakika masu raunin imani daga cikin Musulmai suna kallonsu kallon na ganin burgewarsu, ba tare da kallon abin da suke kai na kafirci ba, da abin da ya ke jiransu na mummunar makoma, sai wannan mummunan kallon [nazarin da suke yi wa rayuwa] ya kai su ganin girman kafiran da ganin darajarsu a zukatansu, da kwaikwayonsu a halayensu da munanan al'adunsu, ba su yi kwaikwayonsu a kwazo da shirin yaki da abu mai amfani ba kamar kere-kere da sana'o'i.

**B. KALLO (NAZARI) NA BIYU GAME DA RAYUWA – (INGANTACCEN NAZARI):**

Shi ne mutum ya yi izina da abin da ya ke cikin rayuwar nan na dukiya da mulki da karfi na zahiri a matsayin hanyar da za ta taimaka wajen aikin neman lahira, A hakika duniya ba a kin ta a kankin kanta, sai dai yabo da zargi yana kai wa gareta ne duba da aikin bawa a cikinta, ita din gada ce, matsallaka ce zuwa lahira, daga cikinta ake samun guzirin aljanna. Mafificiyar rayuwar da 'yan aljanna za su samu, za su samu ne saboda abin da suka shukashi a nan duniya, Ita [duniya] gidan Jihadi ce da sallah da azumi da ciyarwa saboda Allah, kuma fagen tsere zuwa alherai, Allah S.W.T Yana cewa ga 'yan aljanna: ***(Ku ci ku sha cikin jin dadi sakamakon abin da ku ka gabatar a kwanakin [rayuwar] da suka shude)*** **[ al-Haakkah: 24]** yana nufin Duniya.

***

## FASALI NA GOMA: GAME DA TAWAIDA DA LAYU

### 1- TAWAIDA:

Jam'I ne Ruƙya, ita ce tawaida da ake yi wa mai cuta magani da ita, kamar mashasshara da farfadiya da sauransu, suna kiransu da *Aza'im*, kuma kala biyu ce:

**NAU'I NA FARKO:** Wadda babu shirka a ciki, shi ne a karantawa mara lafiya wani abu na Alkur'ani, ko a nema masa tsari da sunayen Allah da siffofinsa, wannan halal ne, saboda Annabi SAW ya yi tawaida, kuma ya yi umarni a yi tawaida kuma ya halatta, daga Awf dan Malik ya ce: Mun kasance muna yin tawaida a Jahiliyya, sai muka ce: Ya Ma'aikin Allah yaya ka ke ganin [yin] haka? sai ya ce: ***"Ku nuna min tawaidar taku, babu laifi a tawaida matukar ba ta zamo shirka ba"***[1]. Suyudi ya ce: Hakika malamai sun hadu a kan halaccin tawaida idan sharuda uku suka hadu: Ta kasance da zancen Allah ko sunayen Allah da siffofinSa, kuma ta kasance da harshen larabci da abin da aka san ma'anarsa, kuma ya kudirce cewa tawaida ba ta tasiri da kanta, saidai da kaddarawar Allah S.W.T[2]. Yadda ake yinta shi ne ayi karatu a tofa ga mara lafiyar, ko a karanta a ruwa a bai wa mara lafiya ya sha, kamar yadda ya zo a hadisin Sabit dan Ƙais: (Cewa Annabi SAW ya dauki kasa a Bat'haan, sai ya sanyata a wani kofi, sannan ya yi tofi a ciki, ya zuba masa)[3].

**NAU'I NA BIYU:** Wanda bai wofinta daga shirka ba, ita ce tawaidar da ake neman taimakon wanin Allah a cikinta, kamar rokon wanin Allah, da neman agajinSa, da neman tsarinSa, kamar tawaida da sunan aljanu, ko sunan mala'iku da Annabawa da salihai, wannan rokon wanin Allah ne kuma shirka ce mafi girma, ko kuma ya kasance ba da harshen larabci ba, ko kuma abin da ba a san ma'anarsa ba, saboda tsoron kar kafurci ko shirka su shiga cikinsa ba a sani ba, irin wannan tawaida an hana.

1 - Muslim ne ya rawaito shi.
2 - Fathul Majid shafi na 135.
3 - Abu Dawud ne ya rawaito shi.

## 2- LAYU

Su jam'I ne na laya, ita ce abin da ake ratayawa a wuyan yara saboda maganin kambun baka, a kan ratayawa manya cikin maza da mata, ita kuma nau'i biyu ce:

**NAU'I NA FARKO NA LAYU:**

Wanda aka yi da Al-kur'ani- shi ne a rubuta wasu ayoyi na Al-kur'ani, ko cikin sunayen Allah da siffofinSa, a rataya don neman waraka da su, wannan nau'in malamai sun yi sabani game da hukuncin ratayashi bisa maganganu biyu:

**Magana ta farko:** Halacci, ita ce maganar Abdullahi dan Amr dan Aas, kuma ita ce zahirin abin da aka rawaito daga Nana A'isha, kuma shi ne maganar Abu-Ja'afar Al-bakir da Ahmad bn Hanbal cikin wata riwayarsa, Sun dauki hadisin da ya zo a kan hana rataya layu cewa yana nufin layun da suke dauke da shirka [ake nufi].

**Magana ta biyu:** Hana yin hakan. Ita ce maganar Abdullahi dan Mas'ud da Ibn Abbas, ita ce zahirin maganar Huzaifa da Ukuba dan Amir da Ibn Ukaim, itace maganar wasu jama'a daga cikin Tabi'ai, daga cikinsu akwai almajiran Ibn Mas'ud da [Imam] Ahmad, da wata riwaya da almajiransa da yawa suka zaba, kuma 'yan baya suka tsaya a kantsa, sun kafa hujja da abin da Ibn Mas'ud RA ya rawaito ya ce: (Na ji Manzon Allah SAW yana cewa: Hakika daga cikin tawaida da layu da maganin mallaka (bi ta zai-zai ko bi shi zai-zai) a kwai shirka)[1] .

**Mallaka** (Bi Ta Zai-Zai Ko Bi Shi Zai-Zai): wani abu ne da suke sanya shi, suna raya cewa yana sanyawa miji ya kaunaci matarsa, mata ta kaunaci mijinta.

**Wannan shi ne ya fi inganci saboda fuskoki uku:**

**Ta farko:** Gamewar hanin, babu abin da ya kebance gamewar.

**Ta biyu:** Toshe kafa, domin zai jawo a rataya abin da ba halal ba.

1 - Ahmad ne ya rawaito shi da Abu Dawud da Ibn Majah da Hakim.

**Ta uku:** Idan ya rataya wani abu na Al-Kur'ani, dole wanda ya rataya din zai wulakanta shi, domin zai dauke shi lokacin biyan bukata, da yin tsarki, da makamantansu[1].

## NAU'I NA BIYU NA LAYU:

Su ne wadanda ake ratayawa mutane kuma ba Al-Kur'ani ba ne, kamar tsa-kiya, da ƙashi da wada'i, da guru, da takalma da ƙusoshi da sunayen shaidanu da aljanu da Ɗalasimai, wadannan haramun ne a yanke, kuma yana cikin shirka, saboda dogara ne da wanin Allah SWT da suanyenSa da siffofinSa da ayoyinSa, ya zo a cikin hadisi; ***"Wanda ya rataya wani abu, to, za a bar shi da abin"***[2]. Ai za a bar shi da wannan abin da ya ratayu da shi, wanda kuma ya ratayu da Allah kuma ya fake da Shi, ya fawwala al'amarinsa duka zuwa gareShi, to, Ya isar masa, zai kusanto masa da duk wani abin [alheri] da ya ke nesa Kuma zai sawwake masa duk wani abu mai wuya, wanda ya dogara da waninSa cikin ababen halitta da layu da magunguna da kaburbura, to, Allah zai bar shi zuwa wadannan abubuwan wadanda ba za su amfana masa komai ba, ba sa mallakar cuta ko amfani, sai [mutum] ya yi asarar Akidarsa, kuma alakarsa da Ubangijinsa ta yanke, kuma Allah Ya taɓar da shi.

Wajibi a kan dukkan musulmi shi ne ya kiyaye akidarsa daga abin da zai ɓata masa ita, ko zai jawo mata ɓaraka, kada ya yi amfani da maganin da bai halatta ba, kuma kar ya je wajen masu tsatsuba da 'yan bori domin yin maganin cututtuka a wajensu, domin za su sanyawa zuciyarsa da Akidarsa cuta, wanda duk ya dogara ga Allah, to, Allah Ya isheshi.

Wani cikin mutane zai rataya wadannan abubuwa a kansa, alhalin ba shi da wata rashin lafiya ta zahiri, kawai dai yana cikin cuta ne ta zato da tsammani [wadda babu ita a hakika]. Shi ne tsoron kambun baka da hassada, ko ya rataya a motarsa ko a dabbarsa ko a kofar gidansa ko a shagonsa. Duk wannan yana daga cikin raunin Akida, da raunin dogaronsa ga Allah, kuma raunin Akida shi ne cuta ta hakika wadda ya wajaba a yi maganinta ta hanyar sanin Tauhidi da Akida ingantacciya.

---

1 -Fathul Majid shafi na 136.
2 -Muslim ne ya rawaito shi.

## FASALI NA GOMA SHADAYA: BAYANIN HUKUNCIN RANTSUWA DA WANIN ALLAH DA TAWASSALI DA NEMAN AGAJI DA WANI ABIN HALITTA

### A. RANTSUWA DA WANIN ALLAH:

**RANTSUWA:** ita ce wallacewa – kuma ita ce karfafa hukunci ta hanyar ambaton wani [abu] mai girma a kebance. Girmamawa: Hakki ce na Allah S.W.T ba ya halatta a rantse da waninSa, malamai sun yi ijma'i bisa cewa rantsuwa ba a yinta sai da Allah ko sunayenSa da siffofinSa, kuma sun yi ijma'I bisa hana rantsuwa da waninSa[1] . Rantsuwa da wanin Allah shirka ce saboda abin da Ibn Umar R.A ya rawaito cewa Manzon Allah SAW ya ce: ***"Wanda ya rantse da wanin Allah, to, ya kafirta, ko ya yi shirka"***[2]. Shirka ce karama, sai dai idan abin da aka rantse da shi mai girma ne a wajen mai yin rantsuwar ta yadda har bauta masa ya ke yi, to, wannan shirka ce mafi girma. Kamar yadda abin ya ke wajen masu bautar kaburbura, domin suna jin tsoron wadanda suke girmamawa na cikin kabarin sama da tsoronsu ga Allah da girmamawarsu gareShi, ta yadda idan aka nemi dayansu ya rantse da waliyyin da ya ke girmamawa ba zai rantse ba sai idan yana da gaskiya, idan kuma aka nemi ya rantse da Allah zai rantse da shi ko da karya ya ke.

Rantsuwa girmama abin da aka rantse da shi ne, ba ya dacewa sai da Allah, kuma ya wajaba a rika ganin nauyin rantsuwa da Allah, kada a yawaita, Allah S.W.T Ya ce: ***(Kada ka bi duk wani mai yawan rantsuwa wulakantacce)*** **[Al-Qalam: 10]**. Allah S.W.T Ya ce: ***(Ku tsare rantsuwarku)*** **[ al-Ma'ida: 89].** Ai kar ku rantse sai a lokacin bukata, kuma a halin kuna da gaskiya cikin ɗa'a- saboda yawan rantsuwa ko kuma karya a cikinta suna nuni bisa raina Allah da rashin girmamaShi, wannan kuma yana cin karo da cikar Tauhidi. [ya zo] cikin Hadisi cewa manzon Allah S.A.W ya ce***: "[Mutum] uku Allah ba zai yi magana da su ba, ba zau tsarkake su ba, kuma suna da azaba mai radadi" ya zo a cikinsa: "Da mutumin da ya sanya [rantsuwa da] Allah hajarsa, ba ya saye sai da rantsuwarsa, ba ya siyarwa sai da rantsuwarsa"***[3]. Hakika Ya tsananta narko a kan yawan

---

[1] - Hashiyatu ibn Qasim Ala kitabit Tauhid shafi na 303.
[2] -Ahmad da Tirmiziy da Hakim ne suka rawaito shi.
[3] - Dabarani ne ya brawaito shi da isnadi ingantacce.

rantsuwa wanda abu ne wanda ya ke nuni a bisa haramcinta domin girmamawa ga Alllah S.W.T. Haka nan rantsuwa da Allah bisa karya ya haramta, ita ce *Gamus*[1] [mai dulmiyarwa]. Hakika Allah Ya siffanta munafikai da cewar suna yin rantsuwa a kan karya suna sane:

**Wannan sai ya fitar mana da cewa:**

1- Haramcin rantsuwa da wanin Allah S.W.T: Kamar rantsuwa da amana ko Ka'aba ko Annabi SAW, kuma yin hakan shirka ce.
2- Haramcin rantsuwa da Allah bisa karya da gangan, ita ce *Gamus* mai dulmiyarwa.
3- Haramcin yawan rantsuwa da Allah ko da yana da gaskiya idan babu bukata; saboda wannan raini ne ga Allah S.W.T.
4- Halaccin rantsuwa da Allah idan [mutum] yana da gaskiya a lokacin bukata.

**B. YIN TAWASSALI DA ABIN HALITTA ZUWA GA ALLAH S.W.T:**

**TAWASSALI:** Shi ne neman kusanci zuwa wani abu, da neman saduwa da shi. Wasila kuma ita ce: kusanci, Allah S.W.T Ya ce: ***(Ku nemi wasila [tsanantuwa] zuwa gareShi)*** **[al-Ma'ida: 35]** ai: kusanci zuwa gareshi S.W.T ta hanyar yi maSa da'a da neman yardarSa.

**TAWASSALI KASHI BIYU NE:**

**Kashi na farko:** Tawassali da shari'a ta yarda da shi, shi ma nau'i-nau'i ne:

1- **NAU'I NA FARKO:** Tawassali zuwa ga Allah SWT da sunayenSa da siffofinSa, kamar yadda SWT Ya yi umarni da hakan cikin faɗinSa: ***(Allah Yana da sunaye mafiya kyawu ku rokeShi da su, ku kyale wadanda suke musun sunayenSa, za a saka musu da abin da sukeaikatawa)*** **[al-A'raaf: 18].**

[1] - Ita ce mai dulmiyar da mai yinta a cikin laifi sannan cikin wuta, ita ce wadda [mutum] ya ke yin ta a kan al'amarin da ya wuce ya byi karya kuma yana sane.

2- **NAU'I NA BIYU:** Tawassali zuwa ga Allah S.W.T da imani da ayyuka nagari wadanda mai tawassalin ya aikata, kamar yadda Allah S.W.T Ya fada game da masu imani: ***(Ya Ubangijimmu mun ji wani mai kira yana kira zuwa ga imani cewar ku yi imani da Ubangijinku, sai mu ka yi imanin, Ya Ubangijimmu Ka gafarta mana zunubammu, Ka kankare mana munanan ayyukammu, Ka cika mana tare da masu da'a)*** **[Al-Imraan: 193],** Kuma kamar yadda ya zo a hadisin [mutum] ukun nan wadanda dutse ya rufe da su, kofar kogon ta toshe da su [a ciki], ba su samu damar fita ba, sai suka yi tawassali zuwa ga Allah da nagartaccen ayyukansu, sai Allah Ya yaye musu[1] sai suka fito suna tafiyarsu.

**3- NAU'I NA UKU:** Tawassali zuwa ga Allah da tauhidinSa, kamar yadda [Annabi] Yunus A.S ya yi: ***(Sai ya yi kira a cikin duffai cewa babu abin bautawa sai Kai, tsarki ya tabbata a gareKa)*** **[Al-Anbiya'i: 87].**

4- **NAU'I NA HUDU:** Tawassali zuwa ga Allah S.W.T ta hanyar bayyana rauni da bukata da talautuwa zuwa ga Allah, kamar yadda Annabi Ayyub A.S ya ce: ***(Lallai cewo ya sameni, kuma Kai ne mafi jin kan masu jin kai)*** **[Al-Anbiya'i: 83].**

5- **NAU'I NA BIYAR:** Tawassali zuwa ga Allah da addu'ar salihai rayayyu, kamar yadda sahabbai suka kasance suna yi idan an yi fari suna neman Annabi S.A.W ya yi musu addu'ar rokon Allah, ya yin da ya yi wafati sai suke neman baffansa Abbas R.A ya yi musu addu'ar.[2]

6- **NAU'I NA SHIDA:** Tawassali zuwa ga Allah ta hanyar ikirari da zunubin da aka yi: ***(Ya ce: Ya Ubangiji lallai na zalunci kaina, Ka gafarta min)*** **[Al-Qasas: 16].**

---

[1] - A dunkule sakon hadisin kenan, Bukhari da Muslim ne suka rawaito shi.

[2] -Bukhari ne ya rawaito shi.

## SASHI NA BIYU: TAWASSALIN DA BA A SHAR'ANTA BA:

Shi ne Tawassali na neman addu'a da ceto daga wajen matattu, da tawassali da alfarmar Annabi S.A.W, da tawassali da zatin ababen halitta ko hakkinsu, ga karin bayani game da haka:

### 1- NEMAN ADDU'A DAGA MATATTU BA YA HALATTA:

Saboda mamaci ba shi da ikon yin addu'a, kamar yadda ya ke shi a lokacin rayuwa, da neman ceto daga matattu shi ma ba ya halatta, saboda Umar dan Khattab da Mu'awiya dan Abu Sufyan da wadanda suke tare da su daga cikin sahabbai da tabi'ai yayin da suka gamu da fari sun nemi sha-da-farin ne sun yi tawassali sun nemi ceto da wanda ya ke raye ne, kamar Abbas, kamar Yazid dan Aswad, Ba su yitawassali ba, ba su yi neman ceto ba, ba su nemi sha-da-fari ba da Annabi S.A.W, ko wajen kabarinsa, ko wajen waninsa ba, sai dai sun maye ne da musayarsa kamar Abbas kamar Yazid, hakika Umar ya ce: Ya Allah Mun kasance muna tawassali zuwa gareKa da Annabimmu sai Ka shayar da mu, yanzu muna tawassali da Baffan Annabimmu, Ka shayar da mu, sai suka sanya wannan maimakon wancan, saboda ba zai yiwu su yi tawassalin bisa tsarin shari'a kamar yadda suke a baya ba.

Kuma abu ne mai yiwuwa su zo kabarinsa su yi tawassalin da shi[1] yana nufin da ace ya halatta, rashin yinsu hakan dalili ne a kan cewa baya halatta a yi tawassali da matattu, ko ta hanyar addu'arsu ko ta hanyar cetonsu, da a ce neman addu'a daga wajensa da neman cetonsa a raye da kuma halin mutuwa duka daya ne, to, da ba su koma wajen waninsa ba, tunda ba wanda ya kai shi.

### 2- TAWASSALI DA ALFARMAR ANNABI S.A.W KO ALFARMAR WANINSA BA YA HALATTA:

Hadisin da ya zo cewa: ***"Idan za ku roki Allah, to, ku rokeShi da alfarmata, domin alfarmata a wajen Allah babba ce"*** Haidsi ne na karya ba ya cikin wani abu daga litattafan musulmai da ake dogara da su, kuma ba

[1] - Majmu'ul fatawa (1/318 -319).

wani cikin malaman hadisi da ya ambace shi[1]. Matukar kuwa bai inganta ba, to, ba ya halatta, saboda ibadu ba sa tabbata sai da dalili ingantacce karara.

**3- TAWASSALI DA ZATIN ABABEN HALITTA BA YA HALATTA:**

Saboda idan *"Ba'un"* din ta rantsuwa ce, to, ta zama an rantse da ita wa Allah SWT, idan kuma ya kasance rantsuwa ce da abin halitta wa wanin abin halittar, to, ba ya halatta kuma shirka ne, kamar yadda ya zo a hadisi, to yaya kuma in ya zama rantsuwa da abin halitta wa Mahalicci S.W.T, idan kuma *"Ba'un"* din ta kasnce ta "*Sababiyya"* ce, to, Allah S.W.T bai sanya roko da abin haliita ya zama sababin amsar addu'a ba, kuma bai shar'anta shi ba ga bayinSa ba.

**4- TAWASSALI DA HAKKIN ABIN HALITTA BA YA HALATTA SABODA ABUBUWA GUDA BIYU:**

**NA FARKO:** Allah SWT babu wani abu da ya wajaba a kanSa a matsayin hakkin wani, kawai Shi ne SWT Ya ke falalar hakan ga abin halitta, kamar yadda [Allah] S.W.T Ya ce: ***(Taimakon muminai ya kasance hakki ne a kammu)*** **[Al-Rum: 47].** Sai ya kasance mai da'a ya cancanci sakamako, hakan cancanta ce ta falala da yin ni'ima, ba wai cancanta ce ta biya ba, kamar yadda abin halitta ya ke da shi akan [dan uwansa] abin halitta.

**NA BIYU:** Lallai wannan hakkin da Allah Ya yi falalarsa ga bawanSa, to, hakki ne wanda ya kebance shi, ba shi da alaka da wani, idan wanda ba shi ya cancance shi ba ya yi tawassali da shi, to, ya zama tawassali da wani abu bare da ba shi da alaka da shi, kuma wannan ba zai tsinana masa komai ba.

Amma hadisin da a cikinsa aka ce: ***"Ina rokonKa da hakkin masu roko"*** to, hadisin bai tabbata ba, saboda a cikinsa akawai Atiyya al-Awfiy, shi din mai rauni ne da aka yi ittifaki a kan rauninsa, kamar yadda wani cikin malaman hadisi ya fada, duk abin da ya zama irin haka ba a hujja da shia a wannan mas'ala mai muhimmanci ta lamarin Akida, sannan a ciki babu

[1] - Majmu'ul fatawa (10/319).

tawassali da wani mutum ayyananne, kawai akwai tawassali da hakkin masu roko gaba daya da hakkin masu rokon amsawa kamar yadda Allah Ya yi musu alkawari da haka, kuma hakki ne nasu wanda Ya wajabtawa kansa, babu wanda ya wajabta masa, kenan tawassali ne da alkawarinSa na gaskiya ba hakkin abin halitta ba.

### C. HUKUNCIN NEMAN TAIMAKO DA NEMAN AGAJI DA ABIN HALITTA:

**ISTI'ANAH:** Tana nufin neman taimako, da karfafa ciki al'amari.

**ISTIGASA:** Tana nufin neman agaji, wanda shi ne kawar da tsanani.

**NEMAN TAIMAKO DA NEMAN AGAJI DA ABIN HALITTA NAU'I BIYU NE:**

**NAU'I NA FARKO:** Neman taimako da neman agaji da abin halitta cikin abin da ya ke da iko, wannan ya halatta, Allah SWT Ya ce: ***(Ku taimaki juna a kan nagarta da tsoron Allah)*** **[al-Ma'idah: 2].** Allah SWT Ya ce: ***(Wanda ya ke daga cikin danginsa Sai ya nemi taimakonsa a kan wanda daga cikin makiyansa)*** **[Al-Qasas: 15].**

**NAU'I NA BIYU:** Neman agaji da neman taimako da abin halitta cikin abin da ba shi da iko a kansa sai Allah: Kamar neman taimako da mamata, da neman agaji da rayayyu, da neman taimako da su cikin abin da babu mai iko a kansa sai Allah kamar warkar da marasa lafiya, da yaye damuwa da gusar da cuta – wannan nau'i ba ya halatta, wannan shirka ce mafi girma- a zamanin Manzon Allah S.A.W wani munafiki ya kasance yana cutar da muminai, sai wasu suka ce: Ku mu ta shi mu nemi agaji da Manzon Allah S.A.W daga [sharrin] wannan munafikin, sai Annabi S.A.W ya ce: ***"Ai ba a neman agaji da ni, kadai dai ana neman agaji ne da Allah"***[1]. Manzon Allah S.A.W ya kyamaci a yi amfani da wannan lafazin a hakkinsa, duk da yana da iko a halin rayuwarsa ya yi hakan amma saboda bayar da kariya ga bangaren Tauhidi, da kuma toshe hanyoyin shirka, da kuma yin ladabi da tawalu'u ga Ubangijinsa, da kuma gargadi ga al'umarsa game da hanyoyin shirka cikin maganganu da ayyuka.

[1] - Dabarani ne ya rawaito shi - mai rauni ne

Idan wannan ya kasance cikin abin da Annabi S.A.W ya ke da iko a kansa ne a halin rayuwarsa, to, yaya kuma za a nemi agajinsa bayan ya bar duniya, a rika neman abubuwan da ba mai iya yinsu sai Allah?[1]. idan kuwa wannan ba ya halatta a hakkinsa [Annabi] S.A.W, wanda ba shi kuwa shi ne ya fi zama [wanda bai cancanta a yi da shi ba].

***

[1] -Fathul majid shafi na a97.

# BABI NA UKU

## BAYANI ABIN DA YA WAJABA A ƘUDIRCE GAME MANZO SAW DA IYALAN GIDANSA DA SAHABBANSA

**HAKAN ZAI ZO CIKIN FASALAI:**

**FASALI NA FARKO:** WAJABCIN SOYAYYAR MANZON DA GIRMAMA SHI, DA HANA ZAKEWA DA WUCE IYAKA A YABONSA, DA BAYANIN MATSAYINSA SAW.

**FASALI NA BIYU:** WAJABCIN YI MASA DA'A DA KOYI DA SHI.

**FASALI NA UKU:** SHAR'ANTA YI MASA SALATI DA SALLAMA.

**FASALI NA HUDU:** FALALAR AHLUL BAITI DA ABIN DA YA WAJABA A YI MUSU BA TARE DA JAFA'I KO ZAKEWA BA.

**FASALI NA BIYAR:** FALALAR SAHABBAI DA ABIN DA YA WAJABA A KUDURCE GAME DA SU, DA MAZHABAR AHLUS-SUNNAH WAL JAMA'A GAME DA ABIN DA YA FARU TSAKANINSU.

**FASALI NA SHIDA:** HANI GAME DA ZAGIN SAHABBAI DA SHUGABANNIN SHIRIYA.

## FASALI NA (1): WAJABCIN SOYAYYAR MANZO DA GIRMAMASHI DA HANA ZAKEWA DA WUCE IYAKA WAJEN YABONSA DA BAYANIN MATSAYINSA SAW

### 1- WAJABCIN SOYAYYAR MANZO DA GIRMAMASHI (S.A.W):

Yana wajaba a kan bawa a farko ya so Allah S.W.T [soyayyar Allah] tana daga cikin manyan ibadu- Allah S.W.T ya ce: ***(Wadanda suka yi imani su ne mafi yawan kauna ga Allah)*** **[Al-Baqarah: 165],** sabo da shi ne Ubangiji mai yin falala ga bayinSa da dukkan ni'imomi na zahiri da na badini, sannan bayan soyayyar Allah S.W.T sai soyayyar ManzonSa S.A.W, sabo da shi ne wanda ya yi kira zuwa ga Allah , ya yi bayani game da Shi, ya isar da shari'arSa, ya bayyana hukunce-hukuncenSa, duk abin da ya samu muminai na alherin duniya da lahira, to, ta hannun wannan Manzon ne, ba wanda zai shiga aljanna sai ya yi masa da'a , kuma ya yi masa biyayya S.A.W, ya zo cikin hadisi: ***"Abubuwa uku wanda ya ke da su zai samu zakin imani, Allah da ManzonSa su zama mafi soyuwa a ransa sama da waninsu, ya so mutum ba don komai ba sai don Allah, kuma ya kyamaci komawa kafirci bayan Allah Ya tseratar da shi daga cikinsa kamar yadda ya ke kyamar a wurga shi a wuta"***[1].

Soyayyar Manzon Allah S.A.W tana biye da soyayyar Allah S.W.T kuma tana tare da ita, tana biye da ita a jeri, kuma [bayani] ya zo game da soyayyarsa S.A.W wajibcin gabatar da ita a kan kowane abin so da ba Allah ba fadinsa S.A.W: ***"Dayanku ba zai yi imani ba har sai na zamo mafi soyuwa a gareshi sama da dansa da mahaifinsa da mutane baki daya"***[2].

Kai! [bayani] ya zo cewa yana wajaba a kan mumini Manzo ya kasance mafi soyuwa a gareshi sama da kansa, kamar yadda ya zo a hadisi: " Lallai Umar dan Khattab RA ya ce: Ya Manzon Allah kai ne mafi soyuwa a gareni sama da komai sai dai kaina , sai [Annabi] ya ce: ***"Na rantse da wanda raina ya ke hannunSa har sai na kasance mafi soyuwa a gareka sama da***

[1] - Bukhari da Muslim ne suka rawaito shi.
[2] - Bukhari da Muslim ne suka rawaito shi.

***kanka" Sai Umar ya ce da shi: " Yanzu kai ne mafi soyuwa a gareni sama da kaina" sai ya ce: " To, sai yanzu ne [imaninka ya cika] ya Umar".***[1]

A cikin wannan a kwai bayanin cewa soyayyar Manzon Allah SAW wajibi ce , kuma abar gabatarwa ce a kan soyayyar komai idan ba soyayyar Allah ba, ita wannan [soyayyar Allah] bi mata ta ke, kuma tana tare da ita, sabo da soyayya ce don Allah kuma sabo da Shi, tana karuwa da karuwar soyayyar Allah a zuciyar mumini, kuma tana raguwa da raguwarta, duk wanda ya kasance mai son Allah ne , to zai yi soyayya a bin Allah kuma sabo da Shi. Soyayyarsa SAW tana sanya wa a girmamashi, a ji nauyinsa a bi shi, a gbatar da maganarsa a kan maganar kowa cikin halittu, kuma a girmama sunnarsa.

Babban malami Ibnul Qayyim RA ya ce: Duk wata soyayya da girmamawa ga mutum kadai tana halatta ne in ta zamo biyayya ce ga Allah da girmamaShi, kamar soyayyar Manzon Allah SAW da girmamashi, hakika tana daga cikar soyayyar wanda ya aiko shi da girmamashi, hakika al'umarsa suna sonsa saboda soyayyar Allah gareshi, suna girmamashi saboda girmamawar Allah gareshi, soyayya ce wadda tana daga cikin wajibabbun abubuwan soyayyar Allah.

Abin nufi shi ne cewar Annabi SAW Allah ya sanya masa kwarjini da soyayya, saboda haka ba a taba samun mutum da wani mutum ya so ba, ko ya ji kwarjini ba, ko ya ga girma ba a ransa kamar Manzon Allah SAW ba a cikin ran sahabbansa - Allah Ya yarda da su -.

Amru dan Aas ya fada bayan ya musulunta cewa: "Hakika ba wani mutum da na fi ki sama da shi, yayin da ya musulumta babu wani mutum mafi soyuwa a gareshi sama da shi, ko mafi girma a idonsa sama da shi, sannan ya ce: Da za a tambayeni in siffanta muku shi ba zan iya ba, saboda ba na iya cika idona da shi, saboda ganin girmansa.

Urwatu dan Mas'ud ya ce da Quraishawa: Ya ku mutanena wallahi na je wajen Kisra da Qaisara da sarakuna, ban taba ganin wani sarki da mutanensa suke girmamashi ba irin yadda sahabban Muhammadu suke girmama

[1] -Bukhari ne ya rawaito shi.

Muhammadu ba SAW, wallahi ba sa ƙura masa ido don girmamawa gareshi, ba ya yin kaki sai ta fada a tafin hannun wani a cikinsu, sai ya shafe fuskarsa da kirjinsa da ita, idan ya yi alawala suna kusan yin fada a kan ruwan alwalarsa. [maganar] ta kare[1].

## 2- HANI A KAN ZAKEWA WAJEN YABONSA DA WUCE IYAKA:

**ZAKEWA:** Ita ce tsallake iyaka – ana cewa: Ya zake, zakewa, idan ya ketare iyaka a lissafi, Allah S.W.T Ya ce: ***(Kada ku tsallake iyaka a cikin Addininku)*** **[ Al-Nisa'i: 171]** ai: [kada] ku tsalake iyaka.

**ITRA':** Shi ne tsallake iyaka a wajen yabo da karya a cikinsa, abin nufi da zakewa a hakkin Manzon Allah S.A.W: Shi ne tsallake iyaka a alkadarinsa a a dauke shi daga matsayin bauta [ga Allh] da manzanci, sai a sanya masa wani abu daga kebance-kebancen Allahntaka, a rika rokonsa, da neman agajinsa ba na Allah ba, a rika rantsuwa da shi.

Abin nufi da Itra' a hakkinsa S.A.W: Shi ne a yi kari a yabonsa – hakika Allah Ya hana haka inda ya ce: ***"Kada ku zake wajen yabona kamar yadda Nasara suka zake wajen yabon [Annabi Isa] dan Maryam – ni dai kawai bawan Allah ne kuma ManzonSa ne"***[2] . Ai kada ku yabeni da karya, kada ku ketare iyaka a wajen yabona kamar yadda nasara suka zake a Annabi Isa A.S, suka rika iqrarin Allahnta game da shi. Ku siffanta ni da abin da Ubangiijina Ya siffanta ni da shi, ku ce bawan Allah, kuma ManzonSa, Yayin da wani cikin sahabbansa ya ce da shi; Kai ne Shugabammu, sai ya ce da shi: ***"Shugaba shi ne Allah S.W.T",*** yayin da suka ce: kai ne mafi falalarmu, mafi girmammu a kyuta, sai ya ce: "***Ku fadi maganarku dai, ko wani bangare na maganarku, kar ku bari Shaidan ya fuzgeku"***[3] .

Wasu mutane suka ce da shi: Ya Manzon Allah Ya mafificimmu Dan mafificimmu Ya shugabammu, dan shugabammu, sai ya ce: ***"Ya ku mutane ku fadi maganarku, kar ku bar Shaidan ya mamayeku, ni ne***

[1] - Jila'ul Afham, shafi na 120 – 121.

[2] - Bukhari da Muslim ne suka rawaito shi.

[3] - Abu Dawud ya rawaito shi da isnadi jayyid

***Muhammadu bawan Allah kuma ManzonSa, ba na so ku dagani sama da matsayina wanda Allah S.W.T Ya saukar da ni”*[1] .

[Annabi] S.A.W ya kyamaci su yabeshi da wadannan lafazai: Kai ne shugabammu- kai ne zababbemmu- kai ne mafificimmu- kai ne mafi girmammu- tare da cewa shi ne mafificin halitta, mafi darajarsu sake ba kaidi- sai dai ya hanasu yin hakan saboda nisanta su daga zakewa da wuce gona da iri cikin hakkinsa, da kuma kare Tauhidi, ya shiryar da su a kan cewa su siffanta shi da siffofi guda biyu, su ne mafi daukakar matsayin bawa , babu zakewa a cikinsu babu hadari a kan Akida, su ne: Bawan Allah kuma ManzonSa, ba ya so su daga shi sama da matsayin da Allah S.W.T Ya saukar da shi Ya yarje masa shi, hakika da yawan mutane sun sabawa hanin nasa, sai aka wayi gari suna rokonsa, suna neman agajinsa, suna rantsewa da shi, suna nema a wajensa irin abin da a wajen Allah kadai ake nema, kamar dai yadda yake faruwa a wajen maulidi da kasidu da nashidu, ba sa banbancewa tsakanin hakkin Allah da hakkin Manzo.

***Babban malami Ibnul Qayyin yana fada a cikin Nuniyya:***

*Allah yana da hakkin da ba ya kasancewa ga wani ***

*BawanSa shi ma yana da hakki, ka ga hakki biyu kenan*

*Kada ku sanya hakkoki biyu su zama hakki daya****

*Ba tare da warewa ba ko neman kusanci.*

### 3- BAYANIN MATSAYINSA SAW:

Babu laifi ayi bayanin matsayinsa da yabonsa S.A.W da irin abin da Allah Ya yabe da shi, da ambaton matsayinsa da Allah Ya fifita shi da shi da kuma kudirce hakan. Manzon Allah S.A.W yana da matsayi madaukaki wanda Allah Ya saukar da shi a kai, shi bawan Allah ne kuma manzonSa ne, kuma zababbenSa ne daga cikin halittunSa, shi ne mafi falalar halittu sake-ba- kaidi, shi Manzon Allah ne zuwa mutane baki daya, zuwa gaba dayan nauyaya biyu nutum da aljan, shi ne mafi falalar manzanni, cikamakin

[1] - Ahmad da Nasa’I ne suka rawaito shi.

Annabawa, babu Annabi bayansa, Allah Ya yalwata masa kirjinsa, Ya daga ambatonsa, Ya sanya kaskanci da wulakanci a kan duk wanda ya sabawa umarninsa, shi ne ma'abocin mukami abin yabo, wanda Allah Ya fada game da shi: ***(Ya kusata Ubangijinka ya tasheka matsayi abin yabo)*** **[Al-Isra: 79].**

Ai: Mukamin da zai tsayar da shi domin ceton mutane a ranar Al-kiyama, domin Ubangijinsu ya hutar da su daga tsananin tsayuwar, wannan matsayi ne da ya kebance shi SAW ban da waninsa cikin Annabawa. Shi ne mafi tsaron Allahn halittu, kuma ya fi su kiyayarSa, Ya hana a daga murya a gabansa S.A.W, kuma [Allah] Ya yi yabo ga wadanda suke qasa da muryarsu a wajensa, sai [Allah] S.W.T Ya ce: ***(Ya wadanda suka yi imani kada ku daga muryarku saman muryar Annabi, kuma ku daina bayyanar masa da magana kamar yadda sashinku ya ke yi wa sashi, don kar ayyukanku su rushe ba ku sani ba. Hakika wadanda su ke qasa-qasa da muryarsu a wajen Manzon Allah wadannan su ne wadanda Allah Ya jarrabi zukatansu da taqawa, suna da wata gafara ta musamman da lada mai girma. Hakika wadanda su ke kiranka ta bayan dakuna, da yawansu ba su da hanakali. Da a ce za su yi hakuri har kafito wajensu, da hakan ya zama mafi alheri a garesu, Allah mai yawan Gafara ne, mai yawan jin kai ne)*** **[ Al-Hujurat: 2 – 5].**

Imam Ibnu kasir -Allah Ya yi masa rahama- ya ce: Wadannan ayoyi ne da Allah Ya koyar da ladabi ga bayinSa muminai a cikinsu irin abin da za su rika mu'amalantar Annabi S.A.W da shi wajen ganin nauyi da girmamawa, da darajtawa da gainin martaba, kuma kada su daga muryarsu a gaban Annabi S.A.W sama da tasa muryar, Kuma [Allah] S.W.T Ya hana a kira Manzo da sunansa kamar yadda ake kiran sauran mutane a ce: Ya Muhammad, a'a, za akirashi ne da manzanci da annabta, sai a ce: Ya Manzon Allah, ya Annabin Allah, Allah S.W.T Ya ce: ***(Kada ku mayar da kiran Annabi kamar kiran sashinku ga sashi)*** **[ Al-Nur: 63],** Kamar yadda cewa Allah S.W.T Yana kiransa ne da Ya kai wannan Annabi, ya kai wannan Manzo, ga shi Allah da mala'ikunSa sun yi masa salati, sannan Ya umarci bayinSa da su yi salati da sallama a gareshi, Sai Allah S.W.T Ya ce:

***(Hakika Allah da mala'ikunSa suna salati ga Annabi, Ya wadanda suka yi imani ku yi salati da sallama a gareshi sallama ta sosai)* [ Al-Ahzab; 56].**

Sai dai ba a kebewa yabonsa wani lokaci, ko yanayi ayyananne sai da dalili ingantacce na Alkur'ani da sunnah. Abin da masu maulidi su ke yi na ware ranar da suke raya cewa ita ce ranar haihuwarsa domin yabonsa bidi'a ce mummuna.

Yana daga cikin girmamashi girmama sunnarsa da kudirce wajibcin aiki da ita, kuma cewa tana cikin mataki na biyu bayan Alkur'ani mai girma wajen wajibcin girmamawa da aiki, saboda ita din wahayi ce daga Allah S.W.T kamar yadda [Allah] SWT ya ce: ***(Ba ya furuci daga son rai, sai dai wahayi da aka yi masa)* [Al-Najm: 3 -4],** ba ya halatta a yi kokonto a cikinta, ko a raina sha'aninta- ko a yi maganar inganci ko rauni na hanyoyinta da isnadanta ko sharhin ma'anoninta sai da ilimi da taka-tsan-tsan, a wannan zamanin rashin kunyar jahilai ta yi yawa a kan sunnar Manzon Allah S.A.W , musamman daga wasu samari masu tasowa wadanda har yanzu ba su wuce matakin farko na koyon ilimi ba, amma an wayi gari suna ingantawa suna raunanawa ga hadisan [Annabi], suna yi wa maruwaitan *jarhu* ba tare da ilimi ba, sai dan karatun litattafai, wannan hadari ne babba a kansu da al'omma, ya zama wajibi a kansu su ji tsoron Allah, su tsaya a matsayinsu.

***

## FASALI NA BIYU (2): WAJIBCIN YI MASA BIYAYYA SAW DA KOYI DA SHI

Biyayyar Annabi S.A.W ta wajaba ta hanyar aikata abin da ya yi umarni da barin abin da ya hana, wannan yana daga cikin abin da shaidawa shi Manzon Allah ne, hakika Allah S.W.T Ya yi umarnin a yi biyayya gareshi cikin ayoyi masu yawa, wani lokaci an hadasu tare da biyayya ga Allah, kamar yadda ya zo a cikin fadinSa: ***(Yaku wadanda suka yi imani ku yi biyayya ga Allah , kuma ku yi biyayya ga Manzo)*** **[Al-Nisa'i: 59]** ayoyi ire-irenta suna da yawa, a wani lokacin yana umarni da yin ta [biyayya ga Manzon] ita kadai a ware, kamar yadda [ya zo] a fadinSa***: (Wanda ya yi da'a ga Manzo, to, Allah ya yi wa da'a)*** **[Al-Nisa'i: 80]**, ***(Ku yi da'a ga Manzo, lallai za a yi muku rahama)*** **[Al-Nur: 56].** A wani lokaci Yana yin narko ga wanda ya saɓawa ManzonSa SAW kamar yadda ya zo a cikin fadinSa S.W.T: ***(Wadanda suke saɓawa umarninsa su shiga hankalinsu kada fitina ta samesu ko kuma wata azaba mai radadi)*** **[Al-Nur: 63].**

Ai: fitina za ta samesu a cikin zuciyarsu kamar kafurci ko munafunci ko bidi'a ko azaba mai radadi a duniya ta hanyar kisa ko haddi ko dauri ko wanin haka cikin ukubobi na duniya, hakika Allah S.W.T Ya sanya da'arSa da biyayyarSa a matsayin dalilin samun soyayyar Allah ga bawa da kuma gafarar zunubanSa – Allah S.W.T Ya ce: ***(Ka ce in kun kasance kuna son Allah , to, ku bi ni sai allah Ya so ku, Ya gafarta muku zunubanku)*** **[Al-Imran: 31],** kuma Ya sanya da'arsa shiriya ce, saɓa masa kuma ɓata ne – [Allah] S.W.T ya ce***: (idan ba su amasa maka ba, to, ka sani cewa kadai dai suna bin son ransu ne, wanene ya kai ɓatan wanda ya bi son ransa ba tare da wata shiriya daga Allah ba, lallai allah ba Ya shiryar da mutane azzalumai)*** **[Al-Qasas: 50].**

Allah S.W.T Ya bayar da labari cewa akwai abin kwaikwayo mai kyau ga al'umarsa a tare da shi, sai [Allah] S.W.T Ya ce: ***(Hakika kuna da kyakkyawan abin koyi game da manzon Allah SAW ga wanda ya ke kaunar Allah da ranar lahira, kuma ya ambaci Allah da yawa)*** **[Al-Ahzab: 21].**

Malam Ibnu Kasir -Allah S.W.T Ya yi masa rahama- ya ce: Wannan ayar mai girma asali ce babba wajen koyi da Manzon Allah SAW a maganganunsa da ayyukansa da yanayinsa, saboda haka ne Allah SWT Ya umarci mutane su yi koyi da Annabi SAW ranar *Ahzab* wajen hakurinsa da juriyarsa da dagewarsa da kokarinsa da saurarensa wajen samun mafita daga Ubangijinsa S.W.T Tsira da amincin Allah su kara tabbata a gareshi a kodayaushe har zuwa ranar sakamako.

Hakika Allah Ya ambaci da'ar Manzo da biyayya gareshi a kusan wurare arba'in cikin Al-kur'ani, don haka zukata suna da bukatar sanin abin da ya zo da shi sama da bukatarsu ga abinci da abin sha, wadanda idan an rasasu ake rasa rayuwar duniya, da'ar Manzo kuwa da biyayya a gareshi idan aka rasa su, azaba ake samu da tsiya ta dawwamammiya, hakika [Annabi] S.A.W ya yi umarni a yi koyi da shi wajen yin ibadu , a yi su a yanayin da yake aikatasu, sai ya ce: ***"Ku yi sallah kamar yadda ku ka ga ina sallah"*[1]*. Kuma ya ce: "Ku karbi ayyukan hajjinku a wajena"***[2]. Kuma ya ce: ***"Wanda ya yi wani aikin da babu umarnimmu a ciki, to, abin mayarwa ne"***[3]. kuma ya ce: ***"Wanda ya yi kyamar sunnata, to, ba ni, ba shi"***[4]. Da sauran nassoshin da ba wadannan ba, wadanda a cikinsu akwai umarni da kwaikwayonsa, da hana saba masa.

*******

[1] - Hadisin Bukhari ne ya rawaito shi.
[2] - Hadisin Muslim ne ya rawaito.
[3] - Hadisin Bukhari da Muslim sun hadu a rawaito shi.
[4] - Bukhari da muslim ne suka rawaito shi.

## FASALI NA UKU (3): SHARI'ANTA SALATI DA SALLAMA GA MANZO SAW

Daga cikn hakkinsa da Allah Ya shari'anta masa a kan al'ummarsa shi ne su yi masa salati su yi masa sallama, lallai Allah S.W.T ya ce: ***(Lallai Allah da mala'ikunSa suna salati ga Annabi, Ya wadanda suka yi imani ku yi salati da sallama a gareshi sallama sosai)*** **[Al-Ahzab: 56].** Hakika [bayani] ya zo cewa salatin Allah S.W.T shi ne yabonsa da ya ke yi a wajen mala'iku. Salatin mala'iku kuma shi ne addu'a, salatin 'yan'Adam shi ne neman gafara[1]. Hakika Allah S.W.T Ya ba da labari a wannan aya game da matsayin bawanSa annabinSa a wajenSa a ciki tawaga mafi daukaka cewar yana yi masa yabo a wajen mala'iku makusanta, kuma lallai mala'iku suna yin salati a gareshi, sannan [Allah] S.W.T Ya umarci ma'abota duniyar kasa da salati da sallata a gareshi don yabo ya tabbata a gareshi daga daga duniyar sama zuwa ta kasa.

Ma'anar ***(Ku yi sallama, sallama sosai)*** ai: Ku gaisheshi da gaisuwar Musulunci – idan [mutum] zai yi sallati ga Annabi S.A.W, to, ya hada tasakanin salati da sallama, kada ya takaita a kan dayansu, kada ya ce: Allah Ya yi masa salati kawai, kuma kada ya ce: Aminci a gareshi kawai; saboda Allah Ya yi umarni da su gaba daya.

An shari'anta salati a gareshi a wuraren da neman ya ke da karfi: Ko dai bisa wajibci, ko mustahabbanci mai karfi. [Malam] Ibnul Qayyim –Allah Ya yi masa rahama- ya ambata a cikin littafinsa *"Jila'ul Afham"* ya ambaci wurare arba'in da daya- ya fara da fadinsa: Waje na farko: wanda shi ne mafi muhimmanci kuma mafi karfi cikinsu a sallah ne cikin karshen tahiyya Musulmai sun yi Ijma'I bisa shari'antashi, sun yi sabani wajen wajibcinsa a cikinta[2]. Sannan ya ambata daga wuraren akwai karshen Alkunut, da cikin hudubobi, kamar hudubar Juma'a da idi biyu da neman sha-da-fari, da bayan amsawa mai kiran Sallah, da lokacin addu'a, da lokacin shiga masallaci da fita daga ciki, da lokacin ambatonsa S.A.W, sannan [malamin] -Allah Ya yi

---

[1] -Bukhari ne ya ambace shi daga Abul-Aliyah

[2] -Jila'ul Afham 222- 223.

masa rahama- ya ambaci sakamakon da ake samu saboda salati ga Annabi, ya ambaci fa'ida arba'in daga ciki[1].

Daga ciki akwai bin umarnin Allah S.W.T da Ya yi, daga ciki akwai samun salati goma ga duk wanda ya yi salati daya, daga ciki akwai fatan amsar addu'a idan ya gabatar da shi a kanta, daga ciki akwai cewa yana zama sababin samun cetonsa S.A.W idan ya gwamashi da rokon wasila gareshi S.A.W, daga ciki akwai cewar yana zama sababin samun gafarar zunubai, daga ciki cewa yana zama sababi na Annabi ya amsawa wanda ya yi salatin da sallamar, Tsaira da amincin Allah su tabbata ga wannan Annabi mai girma**.**

***

[1] - Jila'ul Afham 302.

## FASALI NA (4): FALALAR AHLUL BAITI DA ABIN DA YA WAJABA A YI MUSU BA TARE DA JAFA'I KO ZAKEWA BA

Ahlul baiti su ne iyalan Annabi S.A.W wadanda sadaka ta haramta a garesu, su ne iyalan Aliyyu, da iyalan Ja'afar, da iyalan Akilu, da iyalan Abbas, da Banul Haris dan Abdul-muttalib da matayen annabi S.A.W, da 'ya'yansa mata, saboda fadin Allah S.W.T: ***(Kaɗai dai Allah Yana So ne ya tafiyar muku da datti ya ku Ahlul baiti, kuma Ya tsarkakeku tsarkakewa sosai)*** **[Al-Ahzab: 33] .**

Al-imam Ibnu Kasir -Allah Ya yi masa rahama- ya ce: Sannan abu ne wanda babu shakka a kansa ga wanda ya yi nazarin Al-Kur'ani cewa matan Annabi SAW sun shiga cikin fadinSa: : ***(Kaɗai dai Allah Yana so ne ya tafiyar muku da datti ya ku Ahlul baiti, kuma Ya tsarkakeku tsarkakewa sosai)*** **[Al-Ahzab: 33],** domin yanayin koro zancen da su ake yi, shi bayan duk hakan sai Ya ce: ***(Ku tuna abin da ake karantawa a dakunanku na ayoyin Allah da hikima)*** **[Al-Ahzab: 34],** ai: Ku yi aiki da abin da Allah S.W.T Ya ke saukarwa ga ManzonSa S.A.W a dakunanku na Alkur'ani da sunnah, [Malam] Qatada ya ce shi da wasu malaman: Ku tuna wannan ni'ima wadda aka kebanceku da ita tsakanin sauran mutane cewar wahayi yana sauka a dakunanku ban da sauran mutane, [Nana] A'isha Siddika 'yar Siddik –Allah Ya yarda da ita- ita ce ta fi su cancantar wannan ni'ima, kuma mafi kebantarsu da wannan gamammiyar rahamar, domin wahayi bai saukarwa Manzon Allah S.A.W a shimfidar wata mata ba sai ita, kamar yadda [Annabi] S.A.W ya yi bayanin hakan. Wani cikin malamai ya ce: Saboda bai auri wata budurwa ba sai ita, wani namiji bai kwanta da ita a shimfida daya ba in ba shi ba S.A.W (yana nufin ba ta auri waninsa ba) Sai ya dace a kebance ta da wannan banbancin, kuma a ware ta da wannan martaba babba, sai dai idan matansa suna cikin iyalan gidansa, to, ai danginsa su ne mafiya cancanta da wannan suna- [maganar] ta kare daga tafsirin Ibnu Kasir.

Su *Ahlus sunnah wal Jama'ah* suna son iyalan gidan Manzon Allah S.A.W, kuma suna jibintarsu, suna kare wasiyyar Manzon Allah S.A.W game da su a inda ya fada a ranar *Ghadir Khum* (sunan waje ne): "Ina

tunatar da ku Allah game da Iyalan gidana"[1]. *Ahlus-Sunnah* suna sonsu, suna girmamasu, saboda hakan yana daga cikin soyayyar Manzon Allah SAW da girmamashi, wannan din bisa sharadin su kasance suna bin sunna, kuma suna daidituwa a kan Addini, kamar yadda magabatansu suke, irinsu Abbas da 'ya'yansa, da Aliyyu da 'ya'yansa, amma wanda ya sabawa sunnah, kuma bai daidaita a kan Addini ba, to, ba ya halatta a jibinceshi, ko da yana daga cikin Ahlul baiti.

Don haka dai matsayin Ahlus sunnah wal Jama'a game da Ahlul Baiti matsayi ne nadaidaici da adalci, suna jibintar ma'abota Addini da daidaituwa daga cikinsu, suna barranta daga wanda ya saba sunnah , ya baudewa Addini, ko da shi yana daga cikin Ahlul Baiti, domin kasancewarsa daga Ahlul baiti, daga cikin dangin Manzon Allah ba zai amfanar da shi komai ba har ya daidaita a kan addinin Allah, hakika Abu Huraira R.A ya ruwaito hadisi, ya ce: Manzon Allah S.A.W ya mike lokacin da aka saukar masa da : ***(Ka gargadi danginka makusanta)*** **[Al-Shu'ara: 214].**

Sai ya ce: (Ya ku Quraishawa – ko wata kalma mai kama da ita- ku sayi kawunanku, ba zan amfana muku wani abu a wajen Allah ba, Ya Abbas dan AbdulMuttalib, ba zan amfana maka komai ba a wajen Allah, Ya Safiyya Innar Manzon Allah ba zan amfana miki komai ba a wajen Allah, Ya Fatima 'yar Muhammad, ki tambayi abin da ki ke so na dukiyata, ba zan amfana miki komai ba a wajen Allah)[2]. Da hadisin: (Wanda aikinsa ya mai da shi baya, nasabarsa ba za ta yi gaggawa da shi ba)[3]. *Ahlus Sunnah Wal Jama'a* suna barranta daga hanyar *Rafilawa* wadanda suke zakewa game da wasu Ahlul baiti, suna da'awar suna da *Isma*, [haka na suna barranta] daga hanyar *Nawasib* wadanda suka kulla gaba ga *Ahlul Baitin* da suke kan hanya mikakkiya, suke sukarsu, [haka na suna barranta] daga hanyar 'yan bidi'a da masu tsatsuba, wadanda suke tawassali da *Ahlul Baiti* suke daukarsu ababen bauta ba Allah ba.

Su *Ahlus sunna* a wannan babin da waninsa ma suna kan tsari ne madaidaici, suna kan tafarki mikakke wanda babu zakewa a ciknsa, kuma

---

[1] - Muslim ne ya rawaiti shi.
[2] -Bukhari ne ya rawaito shi.
[3] - Muslim ne ya rawaito shi.

babu sakaci, babu jafa'I babu shisshigi a hakkin Ahlul baiti da waninsu, Su Ahlul Baiti da suke kan tafarki suna inkarin zakewa da ake yi a kansu, suna barranta daga shisshigi, Amirul Muminina Aliyyu dan abu Dalib R.A ya kone masu zakewar da suka zake a kansa [ya kone su] a wuta. Ibnu Abbas R.A ya tabbatar da shi a kan kashesun, sai dai yana ganin a kashe su da takobi maimakon ta konewa, [Sayyiduna] Aliyyu R.A ya nemi Abdullahi dan Saba' shugaban masu zakewar domin ya kasheshi sai ya gudu ya buya.

***

## FASALI NA (5): FALALAR SAHABBAI DA ABIN DA YA WAJABA A KUDIRCE GAME DA SU DA MAZHABAR AHLUS SUNNAH WAL JAMA'A GAME DA ABIN DA YA FARU TSAKANINSU

Me ake nufi da sahabbai, kuma me yake wajaba a kudirce game da su?

Sahabbai jam'I ne na sahabi: Shi ne wanda ya hadu da annabi SAW yana mai imani da shi kuma ya mutu a haka, abin da ya ke wajaba a kudirce shi game da su shi ne cewar su ne mafi falalar ai'umma, mafi alherin ƙarni saboda gabacinsu da kebantarsu da abokantar Manzon Allah SAW, da yin jihadi tare da shi, da dauko shari'ah daga wajensa da isar da ita ga wadanda suke bayansu, hakika Allah Ya yi yabo a garesu cikin Alkintaccen littafinSa, sai [Allah] S.W.T Ya ce: (***Magabata kuwa na farko daga cikin masu hijira da Ansaru da kuma wadanda suka biyo bayansu da kyautatawa, (duka) Allah Ya yarda da su, su ma sun yarda da Shi, Ya kuma tanadar musu gidajen aljanna da koramu suke gudana ta karkashinsu, suna madawwama a cikinsu har abada, wannan shi ne rabo mai girma)*** **[Al-tauba: 100].** [Allah] S.W.T Ya ce: ***(Annabi Muhammadu Manzon Allah ne, wadanda kuma suke tare da shi masu tsanani ne a kan kafirai, kuma masu tausayin junansu ne, za ka gansu suna ruku'I suna sujjada suna neman falala daga Allah da yardarSa; alamominsu na gurbin sujjada suna bayyana a fuskokinsu. Wannan shi ne misalinsu a cikin Attaura, misalinsu a cikin Linjila kamar shuka ce da ta fitar da reshenta, sai ya karfafe ta, sannan ta yi kauri sai ta daidaita a kan tushiyarta ta rika kayatar da manoma, don Ya cusa wa kafirai haushi. Allah Ya yi wa wadanda suka yi imani suka kuma ayyuka na gari daga cikinsu alkawarin gafara da lada mai girma)*** **[Al-Fathi: 29].** [Allah] SWT Ya ce: ***(Za a bayar da dukiyar) ga matalauta da suka yi hijira wadanda aka fitar da su daga gidajensu don neman falala daga Allah da yardarSa, suna kuma taimakon (Addini) Allah da manzonSa, wadannan su ne masu gaskiya * Da kuma wadanda suka tanadi gida (mutanen Madina) suka kuma (karbi) imani gabaninsu (masu hijira), suna son wadanda suka yi hijira zuwa gare su, ba sa samun wani kyashi a zukatansu game da abin da aka ba su (masu hijira), suna kuma fifita (masu hijira) a kan kawunansu, ko da kuwa suna***

***da tsananin bukata, duk kuwa wanda aka kiyaye shi daga son kansa, to, wadannan su ne masu babban rabo)* **[Al-hashri: 8 – 9].**

A cikin wadannan ayoyi akwai cewa Allah S.W.T Ya yi yabo ga masu hijira da Ansaru, Ya siffantasu da rige zuwa ayyukan alherai, kuma ya bayar da labari cewa ya yarda da su, Ya tanadar musu aljannatai, Ya siffantasu da jin kan junansu, da tsanani a kan kafirai, Ya siffanta su da yawan ruku'I da sujjada da nagartar zuciyoyi, kuma an sansu da kamanni na da'a da imani, Kuma Allah Ya zabesu domin abota da AnnabinSa don Ya don Ya cusa wa makiyanSa kafirai haushi, kamar yadda ya siffanta masu hijira da barin garuruwansu da dukiyoyinsu saboda Allah don taimakon AddininSa da neman falalarSa da yardarSa, da kuma cewar da gaske suke. Sannan Ya siffanta mutanen Madina cewa su ne masu gidan hijirar da taimako da imani na gaskiya, Ya siffantasu da soyayyar 'yan uwansu masu hijira, da fifita su akan kansu da tallafa musu da kubutarsu daga rowa, da wannan ne suka tattaro samun rabo, wannan bangare ne na falalarsu gamammiya, akwai kuma falala ta kebance da martabobi da wani ya fifici wani, -Allah ya qara yarda da su- wannan gwargwadon rigayensu zuwa musulunci da jihadi da hijira.

Mafi falalar sahabbai su ne halifofi hudu: Abubakar da Umar da Usman da Aliyyu, sannan ragowar goman da aka yi wa albishir da aljanna- su ne wadannan hudun da Dalha da Zubair da Abdurrahman bn Awf da Abu Ubaida bn Jarrah da Sa'ad ibn Abi Waqqas da Sa'id dan Zaid, masu hijira sun fifita a kan Ansaru, da 'Yan [yakin] Badar, da Ahlur-ridwan, Wanda ya musulunta kafin hijira ya yi yaki ya fi wanda ya musulunta bayan fathu.

## 2- MAZAHABAR AHLUS SUNNAH WAL JAMA'A GAME DA ABIN DA YA FARU TSAKANIN SAHABBAI NA YAKI DA FITINA

***Dalilin fitinar:*** Yahudawa sun ywa Musuluncu da ma'abotansa kulle-kulle, sai suka cuso wani makiri mugu, wanda ya bayyanar da Musulunci cikin karya da zuur shi ne Abdullahi Dan Saba' daga yahudawan Yaman, Sai wannan bayahude ya rika fesar da kullatarsa da dafinsa a kan halifa na uku daga cikin halifofi shiryayyu: Usman dan Affan –Allah Ya yarda da shi- ya

rika kirkiro tuhumce-tuhumce don bata shi, sai mutane masu karancin nazari da raunin imani da masu son fitina suka baibayeshi, kulle-kullen a karshe ya kai ga kashe Halifa Rashidi Usman -Allah Ya yarda da shi- bisa zalunci , a sakamakon kasheshi ne sabani ya kunno kai tsakanin musulmai, fitina ta kunno kai da zugawa daga bayahuden da mabiya bayansa, yaki ya faru tsakanin sahabbai bisa *Ijtihadin* da suka yi.

[Malam] mai sharhin Dahawiyya ya ce: Hakika asalin *Rafilanci* wani munafikin *Zindiki* ne ya haifar da shi, manufarsa ita ce bata Addinin Musulunci da suka ga Manzo SAW kamar yadda malamai suka ambata, hakika Abdullahibn Saba' yayin da ya bayyana Musulunci ya yi nufin ya bata Addinin Musulunci ne da makircinsa da muguntarsa, kamar yadda Bulis ya yi da Addinin Nasaranci, sai ya bayyanar da ibada, sannan ya bayyanar da umarni da kyakkyawa da hani daga mummuna, har kuma ya yi aikin fitinar Usman da kasheshi, sannan yayin da ya zo Kufa sai ya bayyanar da zakeawa a kan [sayyidina] Aliyyu da taimaka masa, don dai ya kai ga manufofinsa, da labari ya jewa Sayyidina Aliyyu, sai ya nemi ya kasheshi sai ya gudu zuwa Ƙirƙis, labarinsa sananne ne a tarihi.

Sheikhul Islam Ibn Taimiya -Allah Ya yi masa rahama- ya ce: Yayin da aka kashe [sayyidina] Usman sai zukata suka rarrabu, damuwa ta yi yawa, mutanen banza suka bayyana, mutanen kirki suka kaskanta, har wanda ya ke nakasasshe a harkar fitina ya shiga cikinta, wanda yake son ya kawo alheri da gyara ya kasa yinsa, sai [mutane] suka yi wa Allyyu dan Abu Dalib R.A mubaya'a a matsayin Amirul-muminin shi ne mafi cancantar halifanci a lokacin, ya fi kowa falala a cikin wadanda suka rage, sai dai fa zukata a rarrabe suke, kuma wutar fitinar a rure take, don haka kai bai hadu ba, Jama'ar [musulmai] ba su hau tsari ba, don haka halifa da mafiya alherin al'umma ba su iya yin abin da suka so ba na alheri, sai wasu mutane suka shiga cikin rarrabuwar kawunan da fitinar, sai abin da ya faru ya faru.[1]

Sannan ya fada yana mai bayyana uzurin masu yakar junan cikin sahabbai a yakin Aliyyu da Mu'awiya: shi Mu'awiya bai yi da'awar halifanci ba, kuma bai yi mubaya'a da shi ba a lokacin da ya yaki Aliyyu,

[1] -Majmu'ul Fatawa (25/304 – 305).

bai yi yaki a matsayin shi halifa ba ne , ko kuma shi ya cancanci halifanci, mu'awiya ya kasance yana tabbatar da hakan ga wanda duk ya tambayeshi: kuma shi Mu'awiya da mutanensa ba su faro yakar Aliyyu da mutanensa ba kuma ba su nemi darewa shugabanci ba, sai dai yayin da shi Aliyyu R.A da mutanensa suka cewa wajibi ne a kansu [su Mu'awiya] su yi da'a da mubaya'a, domin dole ne musulmai su samu halifa daya, kuma suna ganinsu a matsayin 'yan tawaye ga shugaba, to, sun ki bayar da wannan wajibin kuma ga su da karfi, sai ya ga dacewar ya yakesu, har sai sun bayar da wannan wajibin don a samu da'a da hadin kan jama'a, su kuma (ai Mu'awiya da na tare da shi), sun ce: Hakan ba wajibi ba ne a kansu, kuma idan aka yakesu a kan haka, to, an zalunce su, suka ce: Saboda Usman an kasheshi bisa zalunci bisa *ittifaqin* musulmai, kuma makasansa suna cikin rundunar Aliyyu, kuma suna da rinjaye da karfi, in muka ki za su zaluncemu , za su yi mana ta'addanci, Aliyyu kuma ba zai iya maganinsu ba, kamar yadda bai iya maganinsu wajen kashe Usman ba, don haka halifan da za mu yi wa mubaya'a shi ne wanda zai iya yi mana adalci kuma zai tsaya ya ga an yi mana adalcin.

Mazahabar *Ahlus Sunnah Wal Jama'a* game da sabanin da ya faru da fitinar da yaki ya afku a sakamakonta tsakanin sahabbai, za a dunkule shi ne a al'amura guda biyu:

**AL'AMARI NA FARKO**: Suna kamewa ga barin zance a kan abin da ya faru tsakanin sahabbai, kuma suna kamewa daga barin bincike a kai, saboda hanyar zaman lafiya ita ce yin shiru game da irin wannan, suna cewa ne: ***(Ya Ubangijimmu Ka gafarta mana da 'yan uwammu wadanda suka rigamu da imani, kada ka sanya mana kullata a cikin zuciyarmu game da wadanda suka yi imani, ya Ubangijimmu hakika kai Mai tausayi ne, Mai Jin kai ne)*** **[Al-Hashr: 10].**

**AL'AMARI NA BIYU**: Bayar da amsa game da abubuwan da aka ruwaito game da munanan ayyukansu, wannan yana zuwa ta fuskoki:

***FUSKA TA FARKO:*** Cewa wadannan abubuwan da aka rawaito daga cikinsu akwai na karya, makiyansu ne suka kirkiresu domin su bata musu suna.

***FUSKA TA BIYU:*** Cewa wadannan abubuwan da aka ruwaito daga ciki akwai abin da aka kara da wanda aka yi ragi a cikinsa, aka sauya shi daga fuskarsa ta ainihi, karya ta shiga cikinsa, ya zamo abin sauyawa ba za a waiwaye shi ba.

***FUSKA TA UKU:*** Cewa abin da ya inganta daga cikin wadannan abubuwa da aka ruwaito – kadan ne- za a yi musu uzuri a kansa, saboda ko dai sun yi *Ijtihadi* sun yi daidai a ciki, ko kuma sun yi *Ijtihadi* sun yi kuskure- [lamarin] yana cikin abin da za a iya yin Ijtihadi a cikinsa, in mai *Ijtihadin ya* yi daidai yana da lada biyu, idan kuma ya yi kuskure yana da lada daya, kuskuren kuma an yafe masa, Saboda abin da [ya zo] a hadisi: Hakika Manzon Allah SAW ya ce: “Idan mai hukunci ya yi *Ijtihadi* sai ya yi daidai, to, yana da lada biyu, idan kuma ya yi *Ijtihadi* sai ya yi kuskure, to, yana da lada daya”[1].

***FUSKA TA HUDU:*** Lallai su din mutane ne ya halatta a samu kuskure daga daidaikunsu, su ba ma’asumai ba ne daga zunubai ta fuskar daidaikunsu – sai dai abin da ya ke faruwa da su yana da abubuwan da za su kankareshi masu yawa, daga ciki:

1- Ya zama ya tuba daga shi- shi kuma tuba yana shafe laifi duk yadda ya ke, kamar yadda dalilai suka zo a kan haka.
2- Lallai suna da gabatattun [ayyuka] da falala irin abin da zai tabbatar da gafarar abin da ya faru daga su, Allah S.W.T Ya ce: ***(lallai kyawawan [ayyuka] suna tafiyar da munanan [ayyuka])*** **[Hud: 114].**
3- Lallai su ana ninka musu ladansu sama da waninsu, babu wanda ya yi daidai da su a falala, ya tabbata da fadar Manzon Allah S.A.W cewa su ne mafi alherin ƙarni, kuma cewa mudu na dayansu idan ya yi sadaka da shi ya fi falala daga dutsen Uhudu na zinare idan waninsu ne ya yi sadakar[2] Allah Ya yarda da su, Ya kara yarda da su.

*Sheikhul Islam Ibnu Taimiya* –Allah Ya yi masa rahama- ya ce: Sauran Ahlus sunnah wal jama’a da jagororin Addini ba sa kudirce *ismar* wani daga cikin sahabbai ba, ko dangin [Annabi], ko magabata [a hijira], ko waninsu,

[1] - Ya zo a cikin Sahihaini cikin hadisin Amru dan Aas R.A.
[2] - A cikin hadisi da bukhari da Muslim ne suka rawaito shi.

a'a, a wajensu ya halatta a samu afkuwar zunubi daga garesu, Allah SWT zai gafarta musu da ayyukan lada masu shafewa, ko da wani abin na dalilai, Allah S.W.T Ya ce: ***(Wanda ya zo da gaskiya kuma ya gasgata shi, wadannan su ne masu takawa, za su samu duk abin da su ke so a wajen Ubangijinsu, hakan sakamako ne na masu kyautatawa. Saboda Allah zai gafarta musu mafi munin abin da suka aikata, sai ya saka musu ladansu da mafi kyawun abin da suka kasance suna aikatawa)*** **[Al-Zumar: 33 – 35]**. Allah S.W.T Ya ce: ***(Har lokacin da ya isa karfinsa ya kai shekara arba'in, ya ce: Ya Ubangijina, Ka kimsa min yadda zan godewa ni'imarKa, wadda Ka ni'imtani da ita da kuma mahaifana, kuma (ka ba ni iko) in yi aiki nagari, wanda za Ka yarda da shi, kuma Ka kyautata min zurriyata; lallai ni na tuba a gareKa, kuma lallai ne ni ina daga cikin musulmai. Wadannan su ne wadanda Muke karbar mafi kyan abin da suka aikata, kuma Muke yafe musu munanan ayyukansu, suna cikin 'yan aljanna)*** **[Al-Ahqaf: 15 – 16]** [karatun] ya kare.

Hakika makiya Allah sun riki abin da ya faru tsakanin sahabbai a lokacin fitina na sabani da fada a matsayin dalili na afka musu, da cin mutuncinsu, hakika wasu daga cikin marubatan zamani wadanda suke hayagaga da abin da ba su da sani a kansa sun tafi akan wannan shirin mummuna, sai suka nada kansu alkalai a kan sahabban Manzon Allah S.A.W suna cewa wadannan sun yi daidai, wadannan sun yi ba daidai ba, da tare da wani dalili ba, sai dai kawai jahilci da bin son rai, da maimaita abin da masu kawo hari, da masu kullata cikin orientalists da 'yan amshinsu, har suka sanyawa wasu matasan musulmai wadanda wayewarsu da kyakkyawan tarihin Musulunci kankanuwa ce, [saninsu] da magabata na kwarai wadanda su ne mafi alherin karni, a karshe sai suka fada zuwa sukar Musulunci, da raba kan musulmai, da jefawa a zukatan 'yan karshe na wannan al'umma kiyayyar 'yan farkonta, maimakon kwaikwayon magabata nagari da yin aiki da fadinSa: ***(Wadanda suka zo bayansu suna cewa Ya Ubangijimmu Ka gafarta mana da 'yan uwammu wadanda suka rigamu da imani , kada Ka sanya mana kullata a cikin zuciyarmu game da wadanda suka yi imani, ya Ubangijimmu hakika Kai Mai tausayi ne, Mai Jin kai ne)*** **[ Al-Hashr: 10].**

***

## FASALI NA SHIDA (6): HANI GAME DA ZAGIN SAHABBAI DA JAGORORIN SHIRIYI

### 1- HANI GAME DA ZAGIN SAHABBAI:

Yana daga cikin assalai na Ahlus sunnah wal Jama'a kubutar zukatansu da harasansu daga sahabban Manzon Allah SAW, kamar yadda Allah Ya siffanta su a cikin fadinSa: ***(Wadanda suka zo bayansu suna cewa Ya Ubangijimmu Ka gafarta mana da 'yan uwammu wadanda suka rigamu da imani, kada Ka sanya mana kullata a cikin zuciyarmu game da wadanda suka yi imani, ya Ubangijimmu hakika Kai Mai tausayi ne, Mai Jin kai ne)*** **[Al-Hashr: 10].** Kuma saboda biyayya ga Manzon Allah S.A.W cikin fadinsa: ***"Kada ku zagi sahabbaina, na rantse da wanda raina ya ke hannunsa da dayanku zai ciyar da misalin dutsen Uhudu na zinare ba zai kai mudun dayansu ba ko ma rabinsa"***[1].

Suna barranta daga hanyar Rafilawa da Khawarij wadanda suke zagin sahabbai R.A suke kinsu, suke musanta falalarsu, suke kafirta yawancinsu, Ahlus sunna suna karbar abin da ya zo a AlKur'ani da sunnah na falalarsu, kuma suna kudirce cewa su ne mafifitan karni kamar yadda Annabi S.A.W ya fada: ***"Mafi alherinku su ne karnina"***[2]. Yayin da [Annabi] S.A.W ya ambaci rarrabuwar al'umma zuwa kungiya saba'in da uku, kuma duk suna wuta ban da daya, suka tambayeshi game da dayar, sai ya ce: ***"su ne wadanda suke kan abin da nake akansa a yau da sahabbaina"***[3].

Malam Abu Zur'ah ya ce –yana daga cikin manyan malaman Muslim-: idan ka ga mutum yana tauye wani abu daga [kimar] sahabbai , to, ka sani zindiki ne, sabo da AlKur'ani gaskiya ne, Manzo gaskiya ne, abin da ya zo da shi gaskiya ne, babu wanda ya kawo mana dukkan wannan sai sahabbai, wanda duk ya *jarrahasu,* to, so ya ke ya bata Alkur'ani da sunna, don haka sai ya zama shi ya fi dacewa wannan *jarhin*, yi masa hukunci da zindikanci da bata ya fi zama daidai, kuma ya fi zama gaske. Babban Malami Ibn Hamdan ya fada a cikin *Nihayatul mubtadi'in*: Wanda ya zagi wani cikin

---

[1] - Hadisin Bukhari da Muslim ne suka rawaitoshi.
[2] - Hadisin Yana cikin Sahihaini.
[3] -Imam Ahmad ne ya rawaito da waninsa.

sahabbai yana ganin halaccin hakan, to, ya kafirta, idan kuma bai halatta ba, to, ya zama fasiki, [a wata riwayar] daga gareshi ya zama kafiri kai-tsaye, wanda ya fasikantar da suko ya sokesu a addininsu ko ya kafirtasu, to, ya kafirta[1].

## 2- HANI GAME DA ZAGIN JAGORORIN SHIRIYA DAGA CIKIN MALAMAN WANNAN AL'UMMA:

Jagororin shiriya daga cikin Tabi'ai, da wadanda suka biyo bayansu cikin karni-karni mafiya falala da karamci, da wadanda suka zo daga bayansu cikin wadanda suka bi sahabbai da kyautatawa duka wadannan su ne suke bin bayan sahabbai wajen falala da matsayi da martaba, Allah S.W.T Ya ce: ***(Magabata kuwa na farko daga cikin masu hijira da Ansaru da kuma wadanda suka biyo bayansu da kyautatawa, (duka) Allah Ya yarda da su, su ma sun yarda da Shi, Ya kuma tanadar musu gidajen aljanna da koramu suke gudana ta karkashinsu, suna madawwama a cikinsu har abada, wannan shi ne rabo mai girma)*** **[Al-Tauba: 100].** Ba ya halatta a tauyesu a zagesu, saboda su din jagorori ne na shiriya, hakika Allah S.W.T Ya ce: ***(Kuma duk wanda yake saba wa wannan Manzo bayan shiriya ta bayyana a gare shi, ya ke kuma bin tafarkin da ba na muminai ba, to, za mu bar shi da abin da ya daukar wa kansa, sannan Mu shigar da shi wutar Jahannama; makoma kuwa ta munana)*** **[Al-Nisa': 115].**

[Malam] mai sharhin Dahawiyyah ya ce: Yana wajaba a kan kowane musulmi bayan jibintar Allah da ManzonSa, Ya jibinci muminai, kamar yadda Alkur'ani ya furta musamman wadanda su ne magada Annabawa, wadanda Allah Ya sanyasu a matsayin taurari da ake shiryuwa da su a cikin duffan tudu da kogi. Hakika musulmai sun hadu a kan shiriyarsu da saninsu, domin su ne magadan Manzo a cikin al'umarsa, masu raya abin da ya mace daga cikn sunnarsa, da su ne Alkur'ani ya tsaya da shi ne suka tsaya, da su ne Alkur'ani ya yi furuci da shi ne suka yi furuci, dukkansu sun hadu haduwa ta yakini a bisa wajibcin bin sunnar Manzo S.A.W, sai dai idan aka samu maganar dayansu hadisi ya saba mata, to, a kwai zurin da ya sa ya bar shi).

[1] -Sharhu Akidatil Safariniy (2/388 – 389).

**UZURURRUKAN A DUNKULE GUDA UKU NE:**

***Na farkonsu:*** Rashin kudirce cewa Annabi S.A.W ya fada.

***Na biyu:*** Kudircewarsa cewa wannan mas'alar ya ke nufi da maganar tasa.

***Na uku:*** Kudirce cewa hukuncin shafaffe ne.

Suna da fifiko a kammu, da alheri a kammu saboda rigaye, da isar da abin da aka aiko Manzo da shi S.A.W zuwa garemu, karin bayanin a kan haka ba abu ne mai buya a garemu ba, Allah Ya kara yarda da su ***(Ya Ubangijimmu Ka gafarta mana da 'yan uwammu wadanda suka rigamu da imani, kada Ka sanya mana kullata a cikin zuciyarmu game da wadanda suka yi imani, ya Ubangijimmu hakika kai Mai tausayi ne, Mai Jin kai ne)*** **[Al-Hashr: 10].**

Zubar da kimar malamai saboda wasu daga cikinsu sun yi kuskure a *Ijtihadi* hanya ce ta 'yan bidi'a, kuma yana daga cikin tsare-tsaren makiyan al'umma domin kawo kokonto a cikin Addinin Musulunci, da afkar da kiyayya tsakanin musulmai, kuma saboda a raba magabatan al'uma da na bayansu, Da kuma yada rarrabuwa tsakanin matasa da malamai kamar yadda yake faruwa a yanzu, don haka sai dalibai masu tasowa irin wadanda suke zubar da kimar malaman Fikhu, da kimar Fikhun Musulunci, kuma ake sanya musu kyamar karantashi da amfana da abin da yake gaskiya kuma daidai a cikinsa,  sai su kula kuma su fadaka- su rika jin izza da Fikhunsu kuma su girmama malamansu, kada su ruɗu da furofaganda ta ɓata da ɓatanci, Allah Ya sa mu dace.

***

# BABI NA HUDU

## BIDI’O’I

**YA KUNSHI FASALAI MASU ZUWA:**

**FASALI NA FARKO:** TA’ARIFIN BIDI’A – NAU’O’INTA – HUKUNCE-HUKUNCENTA.

**FASLI NA BIYU:** BAYYANAR BIDI’O’I A RAYUWAR MUSULMAI, DA DALILAN DA SUKA JAWO HAKAN.

**FASALIN NA UKU:** MATSAYIN AL’UMMAR MUSULMAI GAME DA BIDI’O’I, DA TSARIN AHLUS SUNNAH WAL JAMA’A WAJEN YI MUSU RADDI.

**FASALI NA HUDU:** MAGANA GAME DA MISALAI NA BIDI’O’IN ZAMANI, SU NE:

1- TARON MAULIDIN ANNABI.
2- NEMAN ALBARKAR WURARE DA ABUBUWA DA MATATTU DA MAKAMAN HAKA.
3- BIDI’O’I A WURAREN AL’ADU, DA NEMAN KUSANCIN ALLAH.

## FASALI NA FARKO (1): TA'ARIFIN BIDI'A – NAU'O'INTA DA HUKUNCE-HUKUNCENTA

### 1- TA'ARIFINTA: BIDI'A A YARE:

An samo ta daga "*bid'u"* yana nufin kirkirar da ba a riga da wani misali ba, daga nan ne aka samu fadin Allah S.W.T: ***(Mai kirkirar sammai da kasa)*** **[Al-Baqarah: 117].** Ai: wanda Ya faresu ba tare da wani misalin da ya gabace shi ba, FadinSa S.W.T***: (Ka ce ban kasance kirkirarre ba a cikin manzanni)*** **[Al-Ahkaf: 9].** Ai: Ban kasance farkon wanda ya zo da manzanci daga Allah zuwa bayi ba, sai dai wasu da yawa daga manzanni sun riga ni.

Ana cewa: Wane ya kirkiri kirkira, yana nufin ya fari wata hanyar da babu wanda ya riga shi.

### KIRKIRA KALA BIYU CE:

1- Kirkira a al'adu, kamar kirkira a kere-kere na zamani, wannan halal ne, saboda asali a al'adu shi ne halacci.
2- Kirkira a Addini, wannan haramun ne, saboda asali a cikinsa shi ne a yi *tawakkufi* (jira), Manzon Allah S.A.W ya ce: ***"Wanda ya farar da wani abu acikin Addini wanda ba ya cikinsa, to, [wannan abin] abin mayarwa ne"***|[1]. A wata riwayar: ***" Wanda ya aikata wani aiki wanda babu umarnimmu a ciki, to, abin mayarwa ne***"[2].

### 2- NAU'O'IN BIDI'O'I – BIDI'A A ADDINI NAU'I BIYU CE:

**NAU'I NA FARKO:** Bidi'a ta magana a akida, kamar maganganun *Jahmiyya* da *Mu'tazila* da *Rafila* da sauran kungiyoyi na ɓata da aƙidunsu.

**NAU'I NA BIYU:** Bidi'a a ibadu: kamar bauta ga Allah da ibadar da bai shari'anta ba, kuma kashi-kashi ce:

---

1 - Bukhari da Muslim ne suka rawaito shi.
2 - Muslim ne ya rawaito shi.

**Kashi na farko:** Abin da ya ke kasancewa a asalin ibadar: kamar ya farar da wata ibada da ba ta da asali a shari'a, kamar ya farar da wata sallah da ba a shari'anta ta ba, ko wani azumi da ba a shari'anta shi ba a asali, ko bukukuwa da ba a shari'antasu ba, kamar bukukuwan maulidi da sauransu.

**Kashi na biyu:** Abin da ya ke kasancewa na kari a ibadar da aka shari'anta, kamar ya kara raka'a ta biyar a sallar Azahar ko la'asar a misali.

**Kashi na uku:** Abin da yake kasancewa na siffar yadda za a yi ibadar da aka shari'anta, ya yi ta a siffar da ba a shari'anta ba, wannan kamar yin zikiran da ba a shari'anta ba da murya cikin jam'i da waƙe, kamar kuma tsanantawa kai cikin ibadu zuwa abin da zai fitar daga sunnar Manzon Allah S.A.W.

**Kashi na hudu:** Abin da yake kasancewa na kebance lokacin ibadar da aka shari'anta alhali shari'ar ba ta kebance ba, kamar kebance ranar rabin Sha'aban da darensa da yin azumi da sallar dare, hakika asalin azumin da sallar daren an shari'anta, sai dai kebanceshi da wani lokaci cikin lokatai yana bukatar dalili.

## 3- HUKUNCIN BIDI'A A ADDINI DA DUKKAN NAU'O'INTA:

Duk bidi'a a Addini haramun ce kuma bata ce, saboda fadinsa S.A.W: ***"Kashedinku da fararrun al'amura, hakika dukkan fararren abu bidi'a ne, kuma dukkan bidi'a bata ce"***[1]. Da fadinsa S.A.W: ***"Wanda ya farar da wani abu acikin Addini wanda ba ya cikinsa, to, [wannan abin] abin mayarwa ne"***|[2]. A wata riwayar: ***"Wanda ya aikata wani aiki wanda babu umarnimmu a ciki, to, abin mayarwa ne"***[3]. Wadannan hadisai biyu sun nuna cewa dukkan fararren abu a Addini bidi'a ne, kowace bidi'a bata ce abar mayarwa, ma'anar hakan shi ne cewa a ibadu da akidu haramun ne, sai dai haramcin yana bambanta gwargwadon nau'in bidi'ar, daga ciki akwai abin da ya ke kafurci ne ƙarara, kamar dawafi a kaburbura don neman kusancin na ciki, da gabatar da abin yanka da bakance garesu, da rokon ma'abotansu, da neman agajinsu; da kuma kamar maganganun masu

---

[1] - Abu Dawud ne ya rawaito shi da Tirmiziy, ya ce hadisi ne Hasan sahihun.

2 - Bukhari da Muslim ne suka rawaito shi.

3 - Muslim ne ya rawaito shi.

zakewar *Jahamiyya* da *Mu'tazila*- daga ciki akwai abin da yake shirka ne , kamar gini a kan kaburbura da sallah da addu'a a wajensu, daga ciki akwai abin da yake fasiƙanci ne a aƙida kamar bidi'ar *Khawarij* da *ƙadariyya* da *Murji'a* a maganganunsu da aƙidunsu da suka saɓawa dalilai na shari'ah, daga ciki akwai abin da saɓo ne, kamar bidi'ar *Tabattuli* (ƙin yin aure) da azumi a tsaye cikin rana, da yin fiɗiya da manufar yanke sha'awar jima'i.[1]

**FAƊAKARWA:**

Wanda ya raba bidi'a zuwa bidi'a mai kyau da bidi'a mummuna ya yi kuskure, kuma ya saɓawa faɗinsa S.A.W: ***"Dukkan bidi'a ɓata ce"*** saboda Manzon Allah S.A.W ya yi hukunci a kan cewa dukkan bidi'o'i ɓata ne, Sai kuma mutum ya zo yana cewa ba duk bidi'a ba ce ɓata, sai dai akwai bidi'a mai kyau. *Alhafiz* Ibn Rajab a cikin sharhin Arba'una ya ce: "Fadinsa S.A.W: ***"Dukkan bidi'a ɓata ce"*** yana daga cikin *Jawami'ul kalim* (magana kadan ma'ana da yawa) ba wani abu da ya fice daga cikinsa, kuma asali ne babba daga asalai na addini, kuma ya yi kama da fadisa: ***"Wanda ya farar da wani abu acikin Addini wanda ba ya cikinsa, to, [wannan abin] abin mayarwa ne"***|[2]. Duk wanda ya farar da wani abu, kuma ya danganta shi zuwa Addini, kuma abin ba shi da asali a Addini za amayar masa, kuma ɓata ne, ba ruwan Addini da shi, a nan duk daya ne mas'alolin akida ko na ayyuka ko maganganu na fili da na ɓoye. [maganar}] ta kare.[3]

Wadannan ba su da wata hujja a kan cewa akwai bidi'a mai kyau, sai dai maganar Umar R.A a sallar Tarawihi: (Madallah da wannan bidi'ar).

Kuma sun ce: Akwai abubuwa da aka farar da su kuma magabata ba su yi inkarinsu ba, kamar tattara Alkur'ani a littafi daya, da rubuta hadisi da tattareshi waje guda- Amsa game da haka ita ce: Wadannan al'amura suna da asali a shari'a ba fararru ba ne, kuma maganar Umar (Madallah da wannan bidi'ar) yana nufin bidi'a a yare ba a shari'a ba, duk abin da yake da asali a shari'a da ya ke komawa zuwa gareshi, to, idan aka ce bidi'a ne, to, bidi'a a yare ne ba a shari'ah ba; saboda bidi'a a shari'a: Ita ce abin da ba shi

---

[1] - Duba al-I'tisam na Shatibiy, (2/37).
2 - Bukhari da Muslim ne suka rawaito shi.
[3] -Jami'ul ulumi wal hikam, shafi na 233.

da asali a shari’ah da yake komawa zuwa gareshi; saboda Annabi S.A.W ya kasance yana umarni a rubuta Alkur’ani, sai dai ya kasance a rubuce a warware, sai sahabbai suka tattara shi –Allah Ya yarda da su- a *mushafi* daya, Domin ba shi kariya, *Tarawihi* kuma Annabi S.A.W ya sallace tada sahabbansa a wasu darare, sai kuma ya yi fashi akarshe domin tsoron kada a farlanta mana, sai sahabbai –Allah Ya yarda da su-suka ci gaba suna sallatar ta da ban da ban a warware cikin rayuwar Manzon Allah S.A.W da bayan *wafatinsa* har zuwa lokacin da Umar dan Khattab R.A ya hadesu a bayan limami daya, kamar yadda suka kasance a bayan Manzon Allah S.A.W wannan kuwa ba bidi’a ba ne a Addini. Rubutun hadisi kuma shi ma yana da asali a shari’a, hakika Manzon Allah SAW ya yi umarni da a rubuta wa wani cikin sahabbai a lokacin da ya nemi hakan, kuma abin da ake gudu game da rubutun a dunkule a zamaninsa S.A.W shi ne tsoron kada abin da ba Alkur’ani ba ya cakude da shi. Yayin da S.A.W ya yi wafati wannan abin da ake tsoro sai ya kau- saboda Alkur’ani ya riga ya kammala, an kiyayeshi kafin wafatin Manzon Allah S.A.W, sai musulmai suka taskance hadisi bayan haka domin kareshi daga ɓalɓalcewa, Allah ya saka musu da alheri a madadin Musulunci da musulmai, ta yadda suka kare littafin Ubangijinsu da sunnar Annabinsu S.A.W daga ɓalɓalcewa da wasa masu wasa.

***

## FASALI NA BIYU (2): BAYYANAR BIDI'O'I A RAYUWAR MUSULMAI DA DALILAN DA SUKA JAWO SU

1- **BAYYANAR BIDI'O'I A RAYUWAR MUSULMAI, KARKASHINSA AKWAI MAS'ALOLI GUDA BIYU:**

### MAS'ALA TA FARKO: LOKACIN BAYYANAR BIDI'O'I:

*Sheikhul Islam Ibn Taimiya* –Allah Ya yi masa rahama- ya ce[1]: Ka sani cewa yawancin bidi'o'i masu alaka da ilimai da ibadu sun faru ne a al'umma a karshe-karshen Halifofi Shiryayyu kamar yadda Annabi S.A.W ya bayar da labari a inda ya ce: ***"Wanda ya yi tsawon rai a cikinku zai ga sabani mai tarin yawa, ina umartarku da sunnata da sunnar halifofi shiryayyu masu shiryarwa"***[2]. Farkon bidi'a da ta faru ita ce bidi'ar *Kadariyya* da bidi'ar *Murji'a,* da bidi'ar Shi'anci da *Khawarij* yayin da rarrabuwa ta faru bayan kashe Usman sai bidi'ar Haruriyya, sannan a karshen zamanin sahabbai fitinar Kadariyya ta faru a karshen zamanin Ibn Umar da Ibn Abbas da Jabir da makamantansu cikin sahabbai, *Murji'a* ta faru kusan haka, amma *Jahamiyya* ta faru ne a karshen zamanin Tabi'ai bayan rasuwar Umar dan Abdul'aziz, Hakika an rawaito cewa ya yi gargadi game da su, bayyanar Jaham A Khurasan ta kasance a zamanin halifancin Hisham dan Abdulmalik.

Wadannan bidi'o'i sun bayyana a karni na biyu sahabbai suna nan kuma sun yi inkari ga masu yin su, Sannan bidi'ar Mu'tazilanci ta bayyana, fitintinu suka faru tsakanin muslmai, sabanin ra'ayoyi da karkata zuwa bidi'a da son rai ya bayyana, kuma bidi'ar sufanci ta bayyana, da bidi'ar gini a kan kaburbura bayan karni-karni mafifita, hakan abin ya ke duk lokacin da zamani ya ja sai bidi'o'i su karu su zo da sabon salo.

### MAS'ALA TA BIYU: WAJEN BAYYANAR BIDI'O'I:

Garuruwan musulunci sun sha banban wajen bayyanar bidi'o'i acikinsu, Sheikhul Islam Ibn Taimiya ya ce: "Hakika manyan birane da sahabban Manzon Allah S.A.W suka zauna a cikinsu kuma ililmi da imani ya bayyana

---

[1] -Majmu'ul Fatawa (10/354)

[2] -Abu Dawud ne ya rawaito shi da Tirmiziy ya ce: Hadisi ne hasan sahih

a cikinsu biyar ne: Haramai biyu Iraki biyu da Sham. Daga cikinsu ne Alkur'ani da hadisi da Fikhu da Ibada da abin da ya biyo bayan haka na al'amuran Musulunci duk suka fito, kuma daga wadannan birane ne ban da Madina bidi'o'in *Asali* (Akida) suka fito, Ita Kufa daga cikinta ne Shi'anci ya fito da Murji'anci sai ya yadu a wasu wuraren bayan haka, Ita kuma Basara daga cikinta ne Kadariyya da Mu'tazilanci da yin ibada ta barna suka fito, kuma suka yadu bayan haka a wasunsu, Sham kuma a cikinta akwai *Nasbu* da *Ƙadar*, Amma *Tajahhum* (goyon bayan Jahamu) kadai ya bayyana ne a bangaren Khurasan shi ne mafi sharrin bidi'o'i, kuma bayyanar bidi'o'i yana kasancewa gwargwadon nisa daga gidan Annabta (Madina), yayin da fitinar rarrabuwa bayan kashe Usman ta faru sai bidi'ar *Haruriyya* ta bayyana, Amma Madinar Annabi ta kasance ta kubuta daga bayyanar wadannan bidi'o'i, idan kuma an samu wanda ya kunso hakan, to, yana zama wulakantacce abin zargi a awajensu, idan aka samu wasu mutane a cikinta 'yan Kadariyya da sauransu, sai dai suna kasancewa a kaskance a wulakance sabanin Shi'anci da Murji'anci a Kufa, da Mu'tazilanci da bidi'o'in ibada a Basara, da *Nasbu* (gaba da Ahlul baiti) a Sham shi wannan ya kasance a bayyane, lallai ya tabbata a ingantacce daga Annabi SAW cewa Dujal ba zai shigeta ba, Kuma ilimi da imanai ba su gushe ba a bayyane har zamanin almajiran [Imamu] Malik ga shi kuwa suna cikin 'yan karni na hudu[1]..

Amma Karni-karni na ukun nan mafifita acikinsu ba a samu wata bidi'a a Madinar Annabi ba gaba daya, wata bidi'a a asalin Addini (akida) ba ta fito daga cikinta ba irin yadda ta fito a sauran birane.

### 2- DALILAN DA SUKA JAWO BAYYANAR BIDI'O'I:

Yana daga cikin abin da babu kokontao a cikinsa cewa riko da Alkur'ani da Sunnah akwai matserata a cikinsu daga afkawa cikin bidi'o'i da bata, Allah S.W.T Ya ce: ***(Wannan ne tafarkina miƙaƙƙe, ku bi shi, kada ku bi hanyoyi sai su watsar da ku daga hanayarSa)*** **[Al-An'am: 153].** Annabi SAW ya yi bayanin haka a cikin abin da Ibn Mas'ud R.A ya rawaito ya ce: "Manzon Allah S.A.W ya zana mana wani layi, sai ya ce: ***"Wannan ce***

[1] - Majmu'ul Fatawa (20/300 – 303).

***hanyar Allah,"*** sannan ya yi wasu zane-zanen a damansa da hagunsa, sannan ya ce: ***"Wadannan kuma wasu hanyoyin ne, a kan kowace hanya akwai Shaidanin da yake kira zuwa gareta"*** sannan ya karanta***: (Wannan ne tafarkina mikakke, ku bi shi, kada ku bi hanyoyi sai su watsar da ku daga hanayarSa, wannan ne abin da aka yi muku wasiyya da shi ko za ku yi takawa )***[1]. Wanda ya ya bijirewa Alkur'ani da Sunna, sai hanyoyin bata da bidi'o'I su fuzgeshi.

Dalilan da suka jawo bayyanar bidi'o'i za a iya dunkule su a cikin al'amura masu zuwa: "Jahiltar hukunce-hukuncen Addini, bin son rai, kabilanci ra'ayoyi da mutane, kamaceceniya da da kafirai da kwaikwayonsu, za mu tattauna wadannan dalilai tare da karin bayani:

**(A) JAHILTAR HUKUNCE-HUKUNCEN ADDINI:**

Duk lokacin da zamani ya ja, kuma mutane suka nesa da abubuwa na manzanci sai ilimi ya yi kadan jahilci ya yadu, kamar yadda Annabi S.A.W ya bayar da labari cikin fadinsa: ***"Wanda ya rayu a cikinku zai ga sabani mai yawa"***[2]. Da fadinsa: "***Allah ba Ya karbe ilimi ya fuzgeshi fuzgewar da zai fuzga daga bayi, sai dai Yana karbar ilimi ne da karbar malamai, har idan ya bai rage wani malami ba, sai mutane su riki shugabanni jahilai, sai a tambayesu, sai su bayar da fatawa ba tare da wani ilimi ba, sai su bata su batar"***[3] .Ba mai iya fito-na-fito da bidi'a sai ilimi da malamai, idan aka rasa ililmi da malamai, to, an bai wa bidi'o'i dama su bayyana , su yadu, kuma masu su yi ta karsashi.

**(B) BIN SON RAI:**

Wanda ya bijirewa Alkur'ani da sunnah ya bi son ransa kamar yadda S.W.T Ya ce: ***(Idan ba su amsa maka ba, to, ka sani suna bin son ransu ne, wanene ya kai bata sama da wanda ya bi son ransa ba tare da shiriya daga Allah ba)*** **[Al-Qasas:50]** S.W.T ya ce: ***(Ba ni labarin wanda ya riki son ransa abin bautarsa, ya batar da shi bisa ilimi, ya toshe masa jinsa da***

---

[1] -Ahmad ne ya rawaito shi da Ibn Hibban da hakim da waninsu.

[2] - Daga cikin hadisin da Abu Dawud da Tirmiziy suka rawaito, ya ce hadisi ne mai kyau ingantacce.

[3] - Bukhari da Muslim ne suka rawaito.

***zuciyarsa, kuma ya sanya rufi a kan ganinsa, wanene zai shiryar da shi bayan Allah)* [Al-Jasiya: 23],** su bidi'o'i aiki ne na bin son rai.

(C) **KABILANCI GA RA'AYOYI DA MUTANE:**

Yana shamakance wa tsakanin mutum da bin dalili da kuma sanin gaskiya, S.W.T ya ce: ***(Idan aka ce da su ku bi abin da Allah Ya saukar, sai su ce a'a, za mu bi abin da muka samu iyayemmu a kai)* [Al-Baqarah: 170],** wannan shi ne yadda sha'ani ya ke game da masu kabilanci a yau daga cikin mabiya mazhabobin sufanci da masu bautar kaburbura idan aka kira su zuwa Alkur'ani da Sunnah da barin abin da suke a kai cikin abin da ya saɓawa musu, sai su kafa hujja da mazhabobinsu da iyayensu da kakanninsu.

**(D) KAMACECENIYA DA KAFIRAI:**

Yana daga cikin mafi tsananin abin da ya ke afkarwa cikin bidi'o'i, kamar yadda yake a cikin hadisin Waqid al-laisiy ya ce: Mun fita tare da Manzon Allah S.A.W zuwa Hunain alhalin muna sababbin barin kafirci, Mushirikai suna da wata magarya da suke duƙufa a wajenta, suna rataya makamansu a kai, ana cewa da ita ma'abociyar rataye, sai muka wuce ta wajen magaryar sai muka ce: Ya Ma'aikin Allah ka sanya mana ma'abociyar rataye kamar yadda suke da ma'abociyar rataye, sai Manzon Allah S.A.W ya ce: ***"Allahu Akbar, lalla hanyoyi ne, kun fada –na rantse da wanda raina ya ke hannunSa- kamar yadda Banu Isra'ila suka fadawa Annabi Musa: (Ka sanya mana abin bauta kamar yadda suke da abubuwan bauta, sai ya ce: Lallai ku mutane ne masu wauta)* [Al-A'raf: 138].**

***"Lallai za ku bi hanyoyin wadanda suke kafinku"***[1]. A cikin wannan hadisin akwai bayanin cewa kamanceceniya da kafirai shi ne abin da ya sanya banu Isra'ila suka nemi wannan mummunan abin nema, shi ne cewar ya sanya musu abubuwan bauta da za su bautawa, shi ne abin da ya faru da wasu sahabban [Annabi] Muhammad su rokeshi ya sanya musu wata bishiya da za su nemi tabarrakinta ba Allah ba, wannan shi ne ainihin abin da yake faruwa a yau, hakika yawancin mutane daga cikin musulmai sun kwaikwayi kafirai wajen ayyukan bidi'o'i da shirka, kamar bukukuwan maulidi da

[1] - Tirmiziy ne ya rawaito shi kuma ya ingantashi.

tsayar da wasu raneku da makwanni domin wasu ayyuka na musamman da tarurruka na kewayowar abubuwan addini da na tunawa, da kafa mutum-mutumi da girke abubuwan tarihi, da shirya taron mutuwa da bidi'o'in jana'iza, da yin gini a kan kaburbura da sauransu.

***

# FASALI NA (3): MATSAYIN AL'UMMAR MUSULMAI GAME DA 'YAN BIDI'A DA TSARIN *AHLUS SUNNAH WAL JAMA'A* WAJEN YI MUSU MARTANI

## 1- MATSAYIN AHLUS SUNNAH WAL JAMA'A GAME DA 'YAN BIDI'A:

*Ahlus Sunnah Wal Jama'a* ba su gushe suna yi wa 'yan bidi'a martani ba, suna yi musu inkarin bidi'o'insu suna hana su aikatasu, ga misalan haka:

**A.** Daga Umm-Ad-darda' ta ce: Abu Darda' ya shigo wajena a fusace, sai na ce da shi: Mene ne ya ke damunka? Sai ya ce: Wallahi ban san wani abu na lamarin [Annabi] muhammad tare da su ba sai dai kawai suna yin sallah dukkansu.[1]

**B.** Daga Umar dan Yahaya ya ce: Na ji babana yana zantar wa daga babansa, ya ce: Mun kasance muna zaune a kofar gidan Abdullahi dan Mas'ud kafin sallar Asuba, idan ya fito sai mu tafi tare da shi zuwa masallaci, sai Abu Musa al'Ash'ariy ya zo mana, sai ya ce: Shin baban Abdurrahman ya riga ya fito muku? Sai muka ce: A'a – sai ya zauna a tare da mu har ya fito- yayin da ya fito sai muka mike zuwa wajensa gaba daya, sai ya ce: Ya Baban Abdurrahman lallai ni dazu na ga wani abun da na yi inkarinsa a masallaci, amma ban ga komai ba –Alhamdu lil laahi- sai alheri, sai ya ce: Mene ne abin? Sai ya ce: In dai kana raye za ka ganshi, sai ya ce: Na ga wasu mutane sun yi halqa a zaune a cikiin masallaci suna jiran sallah, a kowace halqa akwai mutane, a hannunsu akwai tsakuwa da yawa, sai ya ce: ku yi kabbara ɗari, sai su yi kabbara ɗari, sai ya ce: Ku yi hailala ɗari, sai su yi hailala ɗari, sai ya ce: Ku yi tasbihi ɗari, sai su yi tasbihi ɗari, sai ya ce: To, me ka ce da su? Sai ya ce: Ban ce da su komai ba ina sauraron ra'ayinka, ko kuma ina sauraron umarninka, sai ya ce: Shin ba ka umarcesu si kirga munanan ayyukansu ba, ka lamunce musu cewa kyawawan ayyukansu ba za a tauye musu komai ba, sannan sai ya wuce muka wuce tare da shi, har muka zo halqa daga cikin halqoqin, sai ya tsaya a kansu, sai ya ce: Mene ne na ganku kuna yi? Ku kirga

[1] -Bukhari ne ya rawaito shi.

munanan ayyukanku, ni na lamunce muku kyawawan ba za a tauye muku komai daga ciki ba, kaicenku Ya al'umar [Annabi] Muhammadu mamakin gaggawar halakarku, wadannan sahabbansa ne suna nan, wannan tufafinsa ne ko bushewa bai yi ba, kwanukansa ba a karyasu ba, na rantse da wanda raina ya ke hannunSa, lallai kuna kan wata hanya wadda ta fi hanyar [Annabi] Muhammad wadda ta fi shiriya a kan tasa, ko kuma kun bude kofar ɓata, sai suka ce: Wallahi ya baban Abdurrahman ba mu nufi wani abu ba sai alheri, sai ya ce: Sau nawa za ku ga mutm ya nufi alheri amma bai dace da shi ba, hakika Manzon Allah S.A.W ya zantar da mu cewa wasu mutane suna karanta Alkur'ani ba ya ketare makogaronsu, na rantse da Allah ban sani ba ko yawancinsu daga cikinku suke, sannan ya juya ya bar su. Sai Amru dan Salama ya ce: Mun ga yawancin wadannan tare da *Khawarij* suna sukar mu ranar yaƙin Naharawan.[1]

**C.** Wani mutum ya zo wajen Imam Malik dan Anas –Allah Ya yi masa rahama- sai ya ce: Daga ina zan yi harama? Sai ya ce: Daga miƙatin da Manzon Allah SAW ya sanya ka yi harama daga shi, sai mutumin ya ce: Idan kuma na yi harama daga wajen da ya fi nisa fa? Sai Malik ya ce: Ba na ganin haka, sai ya ce: Me ka ke ƙi game da haka? Sai ya ce: Ya jiye maka fitina ne, sai ya ce: Ina kuma fitina take wajen ƙarin alheri? Sai ya ce: Hakika Allah SWT Yana cewa: ***(Wadanda suke saba umarninsa su shiga hankalinsu kada fitina ta samesu ko azaba maqi radadi)*** **[Al-Nur: 63],** wace fitina ce ta kai cewar kan kebanta da wata falala da Manzon Allah SAW bai kebanta da ita ba[2]. Wannan misali ne, kuma malamai ba su gushe ba suna inkari akan 'yan bidi'a a kowane zamani wal hamdu lil laah.

## 2- TSARIN AHLUS SUNNAH WAL JAMA'AH WAJEN MARTANI A KAN 'YAN BIDI'A:

Tsarinsu wajen hakan an gina shi ne a kan Alkur'ani da Sunnah, kuma shi ne tsari mai gamsarwa ta yadda suke yin martani a kan shubuhohin 'yan bidi'a suna warwaresu, suna kafa dalili da Alkur'ani da sunnah a bisa

[1] - Darumiy ne ya rawaitoshi a gabatarwar sunan dinsa lamba (210).

[2] - Abu Shamah ya ambaceshi a littafin: Alba'ith ala inkaril bida' wal hawadith cirowa daga abubakar Alkhallal shafi na 14.

wajibcin riko da sunnoni da kuma hani daga bidi'o'i da fararrun abubuwa, hakika sun yi wallafe-wallafe masu yawa a kan hakan, sun yi martani a cikin litattafai na Akidu a kan Shi'a da *Khawarij* da *Jahamiyya* da *Mu'tazila* da *Asha'ira* cikin makalolinsu na bidi'a cikin asalai na imani da akida, kuma sun wallafa litattafai na musamman a kan hakan, kamar yadda imam Ahmad ya wallafa littafi, "Martani a kan Jahamiyya" wasunsa cikin malamai sun yi wallafa kamar Usman dan Sa'id al-Darumiy , kuma kamar yadda ya ke acikin litattafan Sheikhul Islam Ibn Taimiya da almajirinsa Ibnul Qayyim, da sheikh Muhammad ibn AbdulWahhab da sauransun wajen martani a kan wadannan kungiyoyi, da masu bautar kaburbura da sufiyya, amma litattafai na musamman wajen martani a kan 'yan bidi'a suna da yawa, daga cikinsu bisa misali akwai daga litattafai na da kamar:

1- Littafin "*Ali'itisam*" Na Imam Al-Shtibiy.
2- Littafin "*Iqtida' Al-siratil mutaqim*" na Sheikhul Islam Ibn Taimiyah, martani a kan 'yan bidi'a ya ci kaso mai girma na sa.
3- Littafin (*Inkarul hawadith wal bida'*) na Ibn Waddah.
4- Littafin (*Inkarul hawadith wal bida'*) na al-Tartushiy.
5- Littafin (*Al-ba'ith ala Inkaril hawadith wal bida'*) na Abu Shamah

**Daga litattafai na zamani akwai:**

1- Littafin (*Al-ibda' fi madaril ibtida'*) Na Sheikh Aliy Mahfuz
2- Littafin "*Al-sunan wal mubtada'at Al-muta'alliqa bil azkaar was salawaat*" na sheikh Muhammad bn Ahmad al-Shuqairiy al-Hawamidiy.
3- *Risalat al-Tahzir minal bida'* na Sheikh Abdul'aziz bn Baz.

Malamai musulmai ba su ba su gushe ba –Alhamdu lil laah- suna inkarin bidi'o'i, suna yin martani da cikin jaridu da mujallu da kafafen yada labarai da shudubobin juma'a da bitoci da laccoci, abin da ya yi tasiri sosai wajen wayar da kan musulmai da kuma magance bidi'o'i da dakushe 'yan bidi'a.

***

## FASALI NA HUDU (4): BAYANIN MISALAI NA BIDI’O’I NA ZAMANI

**Su ne:**

1- TARON MAULIDIN ANNABI.
2- NEMAN ALBARKAR WURARE DA MATATTU DA MAKAMANTANSU.
3- BIDI’O’I A FAGEN IBADU DA NEMAN KUSANCI ZUWA GA ALLAH.

**Bidi’o’i** na zamani suna da yawa gwargwadon dadewar zamani da karancin ilimi da yawan masu kira zuwa bidi’o’i da saɓawa, da nasowar kamanceceniya da kafirai cikin al’adunsu da bukukuwansu kamar yadda ya tabbata a fadinsa SAW: “Lallai za ku bi hanyoyin wadanda suka gabaceku”[1].

**1- Taron Maulidin Annabi a Rabi’ul Auwal:**

Shi din kamanceceniya ne da Nasara wajen aikin abin da suke kira da taron maulidin Almasihu, sai jahilan musulmai ko malamai masu batarwa su ke taro a watan Rabi’ul Auwal a kowace shekara a zagayowar haihuwar Manzo [Annabi] Muhammad S.A.W, a cikinsu akwai masu yin wannan taron a masallatai, daga cikinsu akwai masu yinsa a gidaje ko wuraren da aka tanada domin hakan, cincirindon mutane da yawa da gama-garinsu suna halarta- suna aikata hakan saboda kwaikwayon Nasara a bidi’arsu ta taron mailidin Almasihu A.S- kuma yawancin wannan taron bayan kasancewarsa bidi’a da kuma kamanceceniya da Nasara ba ya rasa abubuwa na shirka da munanan abubuwa kamar rera kasidu wadanda akwai zakewa a cikinsu game da hakkin Manzo S.A.W har zuwa matakin rokonsa ba Allah ba, da neman agaji da shi, Hakika Anabi S.A.W ya hana zaƙewa wajen yi masa yabo, sai ya ce: ***“Kada ku zaƙe a yabona kamar yadda nasara suka zaƙe a yabon [Annabi Isa] dan Maryam, ni dai bawa ne, ku ce bawan Allah kuma ManzonSa”***[2].

---

1 -Timiziy ne ya rawaito shi kuma ya inganta shi.
2 - Bukhari da Muslim ne suka rawaito shi.

Ma’anar zaƙewa a yabo shi ne: Shisshigi a bege, mai yiwuwa ma har rayawa suke cewa Manzon [Allah] yana halartar tarurrukan nasu, yana daga cikin munanan abubuwa da suke hade da wadannan tarurrukan waƙe- waƙe da ake rerawa bai-daya da kidan ganguna da sauransu cikin irin ayyukan sufaye ‘yan bidi’a, har a kan samu cakudedeniya tsakanin maza da mata, abin da yake jawo fitina, ya kai ga afkawa cikin alfasha, ko wannan tarurrukan sun kubuta daga wadannan haramtattun abubuwa, aka takaita su a taruwa da cin abinci da nuna farin ciki kamar yadda suke cewa – to, dai bidi’a ne fararren abu ne (dukkan fararren abu bidi’a ne, dukkan bidi’a bata ce), kuma dai tsani ne zuwa abin ya ci gaba, abubuwa munana da suke faruwa a sauran tarurruka su faru.

Mun ce lallai bidi’a ne saboda ba shi da asali a Alkur’ani da Sunna da ayyukan magabata na gari da karni-karni mafiya falala, kadai ya faru ne daga baya, bayan karni na hudu na hijira, *Fatimiyyun* ‘yan Shi’a su ne suka fara yinsa, Al-imam Abu Hafs Tajuddin al-Fakihaniy –Allah Ya yi masa rahama- ya ce: Bayan haka: Hakika tambaya daga wasu [‘yan uwa] masu albarka ta maimaitu game da taruwar da wasu mutane suke yi a watan Rabi’ul Awwal suna kiransa maulidi- shin yana da asali a Addini, suna son amsa game da haka dalla-dalla da bayanin game da kai tsaye, Sai na ce – cikin taimakon Allah-: Ban san wani asali da wannan maulidi ya ke da shi ba a Alkur’ani ko a sunna, kuma ba a rawaito aikata shi daga wani cikin malaman al’umma ba, wadanda su ne ababan koyi a Addini, masu riko da abubuwan magabata, kawai bidi’a ne da ci-ma-zaune suka farar da shi, kuma sha’awa ce da maciya banza suka wadata kai da ita.[1]

Sheikhul Islam Ibn Taimiya –Allah Ya yi masa rahama- ya ce: Haka nan abin da wasu mutane suka farar ko dai suna kwaikwayar Nasara a haihuwar [Annabi] Isa A.S, ko kuma kaunar Annabi S.A.W da girmamawa.. wajen yin maulidin Annabi SAW a matsayin biki, tare da cewa mutane [malamai] sun yi sabani game da [ranar] haihuwarsa, hakika wannan abu magabata ba su yi shi ba, da kuma a ce alheri ne tsantsa rinjayayye da magabata –Allah Ya yarda da su- su ne mafi cancanta da yin sa sama da mu, domin sun kasance sun fi mu son Annabi S.A.W, da girmamashi, sun fi mu kishin alheri, kaɗai

1 - Risalatul maurid fi amalil maulid.

dai soyayyarsa da girmamashi tana cikin binsa da da'a ga umarninsa, da raya sunnarsa zahiri da baɗini, da yaɗa abin da aka aiko shi da shi, da yin kokari a kan haka da zuciya da hannu da harshe, domin wannan ita ce hanyar musumai magabata na farko daga cikin masu hijira da Ansaru (mutanen Madina) da wadanda suka biyo bayansu da kyautatawa[1].. [maganar] ta kare da ɗan takaitawa.

Hakika an wallafa litattafai da rubuce-rubuce kanana masu yawa a da, da yanzu, kuma kari a kan kasancewarsa bidi'a da yin kwaikwayo kuma yana kai wa ga yin wasu maulidai kamar maulidan waliyyai da shehunai da jagorori, sai ya bude kofofin sharri masu yawa.

## 2- NEMAN ALBARKACIN WURARE DA ABUBUWA DA MUTANE RAYAYYU DA MATATTU:

Yana daga cikin bid'o'i fararru neman albarkaci da ababen halitta-wannan wani launi ne na launukan bautar gumaka, kuma tarko ne da masu arzuta kansu suke farautar dukiyar mutane masu karancin tunani. *Tabarruki*: Shi ne nemam albarka, wato tabbatuwar alheri a cikin abu da karuwarsa-Neman tabbatar alheri da karuwarsa kadai yana faruwa daga wanda ya mallaki hakan, kuma ya ke da iko a kai Shi ne Allah S.W.T, Shi ne wanda Ya ke saukar da albarka, kuma Ya tabbatar da ita, Amma abin halitta ba shi da iko wajen bayar da albarka da samar da ita, ko wanzar da ita da tabbatar da ita, neman albarka da wurare da abubuwa da mutane rayayyu da matattu ba ya halatta; saboda ko dai ya zama shirka, idan mai [mutum] ya kudirce cewa wannan abin zai ba shi albarka, ko kuma [ya zama] tsani ne zuwa shirka idan ya kudirce cewa ziyararsa da shafashi da shafe jiki da shi dalili ne na samunta daga Allah, amma abin da sahabbai suke yi na neman albarka da gashin Annabi S.A.W da yawunsa da abin da ya fita daga jikinsa kamar yadda ya gabata,[2] to, wannan ya kebance shi ne S.A.W a halin rayuwarsa da kasancewarsa a tsakaninsu saboda dalilin cewa sahabbai ba su kasance suna neman *tabarruki* da dakinsa da kuma kabarinsa ba bayan ya bar duniya. Kuma ba su kasance suna tunkarar wararen da Annabi S.A.W ya zauna ba don su nemi *tabarruki* da su, don haka wuraren waliyyai su suka fi dacewa,

1 -Iqtida'us siratil mustaqeem (2/615) tahkikin Dr NAsir al-Aql.
2 - A shafi na 81.

kuma ba su kasance suna neman tabarrukin mutane salihai ba kamar Abubakar da da Umar da sauransu cikin mafifitan sahabbai ko a raye ko bayan mutuwa, kuma ba su kasance suna tafiya kogon Hira domin su yi sallah a cikinsa ba ko don su yi addu'a, Kuma ba su kasance suna tafiya zuwa Dur (dutse) ba wanda Allah Ya yi magana da [Annabi] Musa don su yi sallah ko addu'a, ko zuwa wasu wuraren da ba wadannan ba na duwatsun da ake cewa akwai makwantan Annabawa ba ko wasunsu, ko wajen wani *mash'had* da aka yi gini a kan wani abu na Annabi cikin Annabawa, haka kuma lallai wajen da Annabi S.A.W ya ke sallah a kansa kodayaushe a Madinar Annabi, babu wani a cikin magabata da yake tabashi ko yake sumbantarsa, ko wajen da ya yi sallah a kansa a Makka da watanta, idan kuwa ya zama wajen da yake takawa da kafafunsa masu albarka, ya yi sallah a kai ba a shari'antawa al'ummarsa su shafa ba ko su sumbanta, to, yaya kuma wuraren da za a ce waninsa ne ya yi sallah ko ya yi barci, to, sumbantar wani abu irin haka da shafe jiki da shi hakika malamai sun sani bisa tabbas a Addinin Musulunci cewa wannan ba ya cikin shari'arsa S.A.W.[1]

### 3- BIDI'O'I A FAGEN IBADU DA NEMAN KUSANCI DA ALLAH:

Bidi'o'in da aka farar da su a fagen ibadu a wannan zamanin suna da yawa- asali a ibadu shi ne *Tawaqqufi* (a jira kar ayi), ba a shari'anta wani abu a cikinsu sai da dalili- duk abin da dalili bai nuna shi ba, to, bidi'a ne saboda fadinsa S.A.W: ***"Wanda ya farar da wani abu acikin Addini wanda ba ya cikinsa, to, [wannan abin] abin mayarwa ne"***[2].

Ibadun da ake yi yanzu wadanda babu dalili a kansu suna da yawa sosai, daga cikinsu akwai:

**Bayyana niyya a sallah:** shi ne ya ce: Na yi niyyar sallah saboda Allah kaza da kaza, wannan bid'a ce, saboda ba ta cikin sunnar Annabi SAW, kuma saboda Allah SWT Yana cewa: [ Ka ce: Yanzu kwa rika sanar da Allah Addininku, alhali kuwa Allah Yana sane da abin da yake cikin sammai

---

1 - Iqtida'us Siratil Mustaqim (2/795 – 802), Tahkik: Dr Nasir al-Aql
2 -Muslim ne ya rawaito shi.

da abin da ya ke cikin kasa? Allah kuwa Masanin koma ne) [al-Hujurat:16], Niyya mahallinta shi ne zuciya, ita aiki ce na zuciya ba na harshe ba, daga ciki akwai Zikiri na jam'I bayan sallah, saboda abin da aka shari'anta shi ne kowane mutum zai karanta zikirin da aka rawaito shi kadai, daga ciki akwai neman karanta fatiha a tarurruka, da bayan addu'a ga mamata, daga ciki akwai makoki na mamata da yin abinci, da dauko makaranta a biya su, suna raya cewa duk hakan yana daga cikin lissafi na ta'aziyya, ko kuma ganin cewa hakan zai amfanar da mamaci, duk wannan bidi'o'i ne da ba su da asali, sasarai ne da uqumai da Allah bai saukar da wata hujja a kai ba.

Daga ciki akwai tarurruka na bikin Addini kamar taron Isra'i da Mi'iraji da bikin [zagayowar] Hijirar Annabi. Wannan tarurruka da wadannan bukukuwa ba su da asali a shari'a, daga ciki akwai abin da ake aikata wa a watan Rajab kamar umarar Rajab, da abin da ake aikata wa a cikinsa na ibadu na musamman kamar nafilar sallah da azumi a cikinsa na musamman, hakika ba shi da wani fifiko a kan watannin da ba shi ba ko a umara ko azumi ko sallah ko yin *Nusuk* (yin yanke-yanke) a cikinsa ko wanin hakan.

Daga ciki akwai zikirai na sufaye da nau'o'insu, dukkansu bidi'o'i ne kuma fararrun abubuwa, saboda sun sabawa zikirai na shari'ah a sigoginsu da yanayinsu da lokutansu.

Daga ciki akwai kebance daren Nisfu (tsakiyar) Sha'aban da sallar dare, da [kebantar] ranar rabin Sha'aban da azumi, hakika duk babu wani abu da ya tabbata daga Annabi ba SAW a kebance, daga ciki akwai gini a kan kaburbura da daukarsu a matsayin masallatai da kai musu ziyara saboda neman tabarruki, Da yin tsani da matattu da sauransu daga manufofi na shirka, da ziyarar mata garesu tare da cewa Manzon Allah S.A.W ya la'anci mata masu yawan ziyarar kaburbura da masu rikarsu a matsayin masallatai da sanya musu fitilu.

***

**A KARSHE:**

Muna cewa: Hakika bidi'o'i 'yan aiken kafirci ce, kuma su ƙari ne a Addini wanda Allah ko manzonSa ba su shari'anta ba, Ita bidi'a ta fi babban saɓo sharri, Shaidan yana farin ciki da ita sama da yadda ya ke yi a kan ayyukan saɓo manya, saboda mai saɓo yana aikata saɓo ne alhalin ya san cewa saɓo ne [wata ran] sai ya tuba, shi kuwa dan bidi'a yana aikata bidi'a ne yana kudirce cewa Addini ce da yake neman kusancin Allah da shi ba zai tuba ba, bidi'o'i suna gamawa da sunnoni, suna sanya wa masu yinsu kyamar sunnoni da Ahlus sunna, ita bidi'a tana nesantarwa daga Allah, tana jawo fushinSa da ukubarSa, suna jawo karkacewar zukata da lalacewarsu.

**ABIN DA AKE MU'AMALANTAR 'YAN BIDI'A DA SHI:**

Ya haramta a ziyarci dan bidi'a da zama tare da shi sai dai a salo na nasiha gareshi da yi masa inkari, saboda yin hulda da shi tana yi wa mai hulda da shi tasiri na sharri tana jawo kiyayyarsa ga wani, ya wajaba a yi kaffa-kaffa daga su da kuma sharrinsu, idan ba za a iya kame hannunsu ba da hanasu yin bidi'o'in ba- idan ba haka, to yana wajaba a kan malaman musulmai  da shugabanninsu hana bidi'o'i da kuma kame hannun 'yan bidi'a da tsawatar da su game da sharrinsu. Saboda hatsarinsu a kan Musulunci yana da tsanani, sannan yana wajaba a sani cewa kasashen kafirai suna karfafar 'yan bidi'a wajen yada bidi'arsu, kuma suna taimaka musu a kan hakan ta hanyoyi da ban da ban; saboda akwai gamawa da musulunci cikin yin hakan da ɓata masa suna.

Muna rokon Allah S.W.T ya taimakawa AddininSa, Ya daukaka kalmarSa, Ya taɓar da makiyanSa- tsira da amincin Allah su tabbata ga Annabimmu Muhammad da iyalansa da sahabbansa.

# ABUBUWAN DA KE CIKI

**Gabatarwa …………………………...……………………………………. 3**

**BABI NA FARKO**

**KARKACEWA (BATA) A RAYUWAR MUTANE DA DAN TARIHI GAME DA KAFURCI DA MUSUN SAMUWAR ALLAH DA SHIRKA DA KUMA MUNAFUNCI…………………………………………...5**

**FASALI NA FARKO:** KARKACEWA (BATA) A RAYUWAR MUTANE …...……. 6

**FASALI NA BIYU:** SHIRKA – MA'ANARTA DA NAU'O'INTA ……..…………… 9

**FASALI NA UKU:** KAFURCI – MA'ANARSA DA NAU'O'INSA ……...…..…….. 14

**FASALI NA HUDU:** MUNAFUNCI - MA'ANARSA DA NAU'O'INSA ….………..17

**FASALI NA BIYAR:** BAYANIN HAKIKANIN WADANNAN ABUBUWA:

JAHILIYYA – FASIKANCI – BATA – RIDDA – RABE-RABENSU DA HUKUNCE-HUKUNCENSU ……………………………………..………….. 22

**BABI NA BIYU**

**MAGANGANU DA AYYUKAN DA SUKE WARWARE TAUHIDI KO SU TAUYESHI…………………………………………………………27**

**FASALI NA FARKO:** DA'AWAR SANIN GAIBI WAJEN KARANTA TAFI KO FINJANI DA DUBA (ILIMIN TAURARI) .. ZUWA KARSHE ……….……………...28

**FASALI NA BIYU:** SIHIRI BOKANCI DA BUGUN KASA …………….………..30

**FASALI NA UKU:** GABATAR ABUBUWAN YANKA DA BAKANCE DA YIN KYAUTUTTUKA GA WAJEN ZIYARCE-ZIYARCE DA KABURBURA DA KUMA GIRMAMASU ……………………………………………………………..……34

**FASALI NA HUDU:** GIRMAMA MUTUM-MUTUMI DA GIRKAKKUN ABUBUWAN TARIHI ........................................................................................38

**FASALI NA BIYAR:** IZGILANCI GA ADDINI DA WULAKANTA ALFARMARSA ……………………………………………………………………………………40

**FASALI NA SHIDA:** HUKUNCI DA WANIN ABIN DA ALLAH YA SAUKAR ……………………………………………………………………………………42

**FASALI NA BAKWAI:** DA'AWAR HAKKIN YIN DOKA DA HALATTAWA DA HARAMTAWA ……………………………………………………………………………47

**FASALI NA TAKWAS:** DANGANTUWA ZUWA MAZHABOBIN KARYATA SAMUWAR ALLAH DA KUNGIYOYI NA JAHILIYYALI …………………………50

**FASALI NA TARA:** KALLON RAYUWA A MATSAYIN ABIN DUNIYA KAWAI…………………………………………………………………………..54

**FASALI NA GOMA:** LAYU DA TAWAIDA ………………………………………...57

**FASALI NA GOMA SHA DAYA:** RANTSUWA DA WANIN ALLAH, DA TAWASSALI, DA NEMAN TAIMAKO DA ABIN HALITTA DA ALLAH ……......60

## BABI NA UKU

**BAYANI ABIN DA YA WAJABA A ƘUDIRCE GAME MANZO SAW DA IYALAN GIDANSA DA SAHABBANSA.........................................67**

**FASALI NA FARKO:** WAJABCIN SOYAYYAR MANZON DA GIRMAMA SHI, DA HANA ZAKEWA DA WUCE IYAKA A YABON SA,……………….. …………68

**FASALI NA BIYU:** WAJABCIN YI MASA DA'A DA KOYI DA SHI ……………..74

**FASALI NA UKU:** SAR'ANTA YI MASA SALATI DA SALLAMA ………………76

**FASALI NA HUDU:** FALALAR AHLUL BAITI DA ABIN DA YA WAJABA A YI MUSU BA TARE DA JAFA'I KO ZAKEWA BA …………………………………….78

**FASALI NA BIYAR:** FALALAR SAHABBAI DA ABIN DA YA WAJABA A KUDURCE GAME DA SU, DA MAZHABAR AHLUS-SUNNAH WAL JAMA'A GAME DA ABIN DA YA FARU TSAKANINSU …………………………………….81

**FASALI NA SHIDA:** HANI GAME DA ZAGIN SAHABBAI DA SHUGABANNIN SHIRIYA ………………………………………………………………………….87

# BABI NA HUDU

**BIDI’O’I.............................................................................................90**

**FASALI NA FARKO:** TA’ARIFIN BIDI’A – NAU’O’INTA – HUKUNCE-HUKUNCENTA ……………………………………………………………………...91

**FASLI NA BIYU:** BAYYANAR BIDI’O’I A RAYUWAR MUSULMAI, DA DALILAN DA SUKA JAWO HAKAN ………..…………………………………….....95

**FASALIN NA UKU:** MATSAYIN AL’UMMAR MUSULMAI GAME DA BIDI’O’I………………………………………………………………………………..100

**FASALI NA HUDU:** MAGANA GAME DA MISALAI NA BIDI’O’IN ZAMANI, SU NE:.......................................................................................................................103

1- TARON MAULIDIN ANNABI ……………………………………………….103
2- NEMAN ALBARKAR WURARE DA ABUBUWA DA MATATTU DA MAKAMAN HAKA ………………………………………………………..105
3- BIDI’O’I A WURAREN AL’ADU, DA NEMAN KUSANCINN ALLAH…..106

**A KARSHE** ………………………………………………………...……………….108

**ABUBUWAN DAKE CIKI**.........................................................................................109

**A KARSHE:**

Bayan ka karanta wannan littafin mai kima wanda malaman da suke neman gaskiya kuma suka kasance masu bin dalili da Manzo SAW suka yi bayaninsa, to, muna kiranka zuwa aiki da shi domin ka kasance cikin wadanda Allah Ya fada game da su: ***(Wadanda suke jin magana, sannan su bi mafi kyawu, wadannan su ne wadanda Allah Ya shiryesu, kuma wadannan su ne ma'abota hankula)***

Ka sani cewa abin da ka karanta ko dai ya zama hujja a gareka ko kuma a kanka, ka gaggauta aiki da shi da karbarsa da zuciya budaddiya, kar ka ce wannan magana ce daga cikin maganganu, ko mazahaba ce daga cikin mazhabobi ba lallai sai na yi aiki da shi ba, to, wannan ba daidai ba ne, kada ka bari Shaidan ya samu mashiga a tare da kai, kada ka sallamawa ingizar Shaidan ko son zuciya, hakika duk wannan zai hana shiga aljanna, ka yi kishin yada wannan alherin tsakanin mutane ***"Mai nuni ga aikin alheri kamar wanda ya aikata shi ne"***, idan ka gama karanta wannan littafin ko waninsa ka yi kyautarsa ga wani, kada ka manta ka yi addu'a ga wanda ya yi shi, [wanda] ya buga shi, [wanda] ya yada shi tsakanin mutane cewar Allah Ya gafarta masa da iyayensa da dukkan musulmai.

Muna rokon Allah S.W.T Ya datar da mu da kai wajen karbar gaskiya da aiki da ita, lallai shi ne majibincin yin haka, kuma Mai iko a kai.